a zallah
Birnin gayu
Chapter1
BIRNIN GAYU. BOOK1
tunkwal Tunkwal Tunkwal "Sautin daka ne ke tashi daga Cikin kewayayyen Gidan Karan wanda aka yi masa danga da
itacen Dalbejiya. , , . Tafiya ta ke cike da nutsuwa dauke da
Littattafan karatunta a hannu ta" nufo Gidan, ga dukkan alamu yunwa da Gajiya na tattare da ita. Da sauri ta shiga Gidan tare da yin sallama. Cikin nutsuwa, "Assalamu alaikum".
Abin da ta gani ne ya sa ta yi sororo kamar wacce aka zarewa rai.
Inna mai Fura ce ta fara kokawar kife wani ' qaton Turmi wanda ga dukkan alamu itama gadon shi ta yi daga Kakanninta. A qiyasi na zan iya cewa Turmin ya bata . shekaru'. ” Inna mai Fura, kenan, yadda mutane suke kiranta ta juyo. '
"Au Deeda har an taso ku?" "Eh mun taso walléhi".
Inna ta yatsina fuska ta dan kau da kai.
"Ni wallahi banga amfanin wannan zuwa Makarantar 'ba. yanzu in a Gida ki ke da tuni mun
‘ Surfe Gero yafi Kwano uku, kin ga, Gidan su Talle .da suka aiko ma sai mayarwa nayi don aiki ya yi min
yawa.Shiga ki cire kayanki ki zoki karasa min sallanabku dai". Aka yi sallama daga waje. ' Inna ce ta amsa sallamar. ' "Allah Ya yi mana. Wa na keji haka kamar Tabawa?" . ' , . ' "Ni ce wallahi cikin ranar nan "To shigo ga Tabarma nan ki zauna”. Inji Inna. Kan wata- busasshiyar Tabarmar Kaba suka zauna Bayan sun gama gaisawa Tabawa ta dubeta kamar .matar da aka ba ta labarin mijinta zai kara Aure, ta ce, "Wata magana nazo miki da ita idan har zaki amince ' Kin san dai wannan jikar taki .duka 'yan matan garin nan ba sa'arta,,yanzun ga shi shekararta goma sha takwas har yau ba manemi, to me zai hana ki bani ita in tafi DA ita birni don ko kinsan

dai lalurar data kashe Yan,uwanta har biyu Ina tabbatar miki da harta manyanta ba zata taba samun mijin aure a kauyennan ba in banda wannan jarababbiyar bokon DA take zuwa Wanda daga ke har ita baya tsinana muku komai kalleki Ki gani yanxune lokacin Daya dace ace kin huta Amman kinanan kullum surfe da saida fura ya kamata Ki amincemin dan Ina tabbatar miki da akwai alkhairi acikin wannan lamarin kika sanima ta wannan dalilin ta samu mijin aure DA maganin matsalarta
Inna tai shiru tana nazarin tayin tabawa Anya kuwa bazan amince wannan Karon DA tayin tabawaba kuwa to saidai kuma deeda miskilar gaske ce banajin zata amince
Ta kalli Tabawa tace, "To ban ki ta taki ba, ‘ amma fa kin san Deeda halinta sai ita..." "Duk halinta ai batafi karfinki ba, sai dai in keki ka so... _ Ni fa taimako na ke son yi, don kuwa BIRNIN GAYU zan kai ta Aiki".Inna ta zaro ido jiki rawa ta ce, “Me..me...me kika ce BIRNIN GAYU fa?" Tabawa ta gyada kai ta ce, "Kwarai ’BIRNIN GAYU zan kai ta Kin San k0 dan kammin Yaro da ke cikin Kauyen nan ya san sunan Birnin Kin san irin kudinsu ‘kuwa ba irin‘ masu kudin yanzu'bane ba, don tun zamanin da...tun xamanin da za a iya kirga masu kudi a kasar nan suke . Tuni Inna ta susuce Ta mike jiki na rawa ta ce "Ah, gaskiya na yarda kina sonmu da. arziki. Wai Ai dole Deeda k0 tana so, k0 ba ta so...ta wuce Birni.. Can kuma ta yi KaSa da murya, cikin sanyin jiki tace "To amma Tabawa ba kya ganin lalurar Deeda zai shiga tsakaninta da wannan dama da ta samu?" ‘
' Tabawa ma ta mike ta ce "Karki damu, lalara ce da a Keuye kawai aka santa, kuma ya shafi Aure ne, amma ai lafiya take ba mai kallonta ya cr ‘ tana da wani lalura..in kina son zuwanta Birni to, dole lalurarta ya zama sirri tun da anan Kauyen ne" kawai aka sani, don haka maganar Kauye a barta a Kauye...Yanzu dai babbar matsalar Deeda ta yarda".
"Ba zan yarda ba Suka ji muryar Deeda ta ratso

kunnuwansu. Tsaye take a Kofar daki ta ‘rike kugu tana dubansu. ' ‘ 1 "Sanin kankine Tabawa ba inda za ni k0 da ‘kuwa Inna za tai kuli-kulin kubura da ni ba zani aiki Gidan waSu ba, k0 da kuwa zan tafi tsirara ne don talauci balle Allah Ya rufa min Asiri. In ban da son zuciya me na ke nema da zanbar Mahaifata in tafi wata uwa duniya don neman kudi...?." "To mara kunya‘ Inna mai hura ta fada cikin hasala. Deeda ta Bata fuska .ta ce, "K0 me za ki ce sai dai ki fada amma ba mai canja min ra'ayi.

Ke kuma Tabawa ja jiki ki bar mana Gida kar ki kuma zuwa mana Gida in kin san ba abin arziki yakawo ki ,ba.

Kuma duk na ci da maitarki ba za‘ki yi ' nasarar kaini Birni ba. Ba mai shiga tsakanina da ’ tushena

Tana fadin hakan ne cikin tsiwa da, daga murya. Tuni Tabawa ta harzuqa, haushi ya cikata. Ta ce"Magani na Daga yin abin arziki yarinya karama Za ta tsaya min da rashin kunya?" Nan ta fita cikin fishi tana mita.

Inna ta_ bita tana ba ta hakuri amma ba ta saurareta ba. Nan ta juya ta hau Deeda da fada da zagi. -

Cikin zafin zuciya. ta ce, "Ai sai ki rayu ki mutu da karatun. Me karatun zai tsinana miki‘?

Ban ga uwar da ki ke daukowa a Makarantar ba, ki ci uban tafiyar Kafa ki je ki tsugunna Gindin Bishiya ga Kishi ga Yunwa duk inda ki ka wucé a garin nan Zaginki ake ana tsegumi, qatuwar Budurwa dake ba Mijin Aure, maimakon ki zauna a Gida ki rufawa kanki Asiri amman ina gara dai ki fita ki Kara tona mana Asiri.

Ni ba ki ’min amfani ba, ke baki yiwa kanki wani amfaniba. To ni na gaji da miki Wahala, duk ran da bakincikinki ya kasheni sai ki Huta.

Bakincikin ki da shi nake kwanaina dashi nake tashi duk kin zame min Larura, k0 Ubanki kasa ‘rike ki‘ya " yi sai ‘ni da ki ka zamar min dole, don na uwar ki

Bakincikin' Yayunki ya kasheta, kema kema kikeaon naki ya karasani. To baki isa ba

“Deeda ta 'kalléta' cikin_ zuciya da
tsantsar bakin ciki da Bacin rai, idonta yayi jawur.
Tayi murmushin takaici tace, "gara
. maganar jama'ar Kauyen nan ai ba komai bane
kan
wanda ki ke min'kullum. . '
Idan bar kin ga na zame miki larura kina da
damar' ki koreni a Gidanki...sai dai Gorinki hade
da Bakaken Maganganun da kike fadamin'bazai
sa na
karaya ba k0” yasa naje Birni Aikatau ba."
"‘ Tana gama fadin haka ta juya tama bar
gidan ta nufi can wani gindin Gadah ta ,zauna
kan
wani Dutse tana kukan bakinciki wanna kan
dutsen shine ya Zame matar tamkar cinyar
mahaifiyarta DA take hawa idan ta shiga wani hali
na baqin ciki tashin hankali KO kuncin rayuwa
@@@@@@@@@
Nana khadija yar asalin kyauyen hayin hago ne
dake qaramar hukumar tofa dake kanon dabo
mutanen kauyen sun shahara ne akan sana ar
Zuma matuqa ba boyayyu bane indai akan harkan
Sana,ar Zuma ce
sun shahara wajen noman tumatir DA albasa
garine Wanda ya hada Hausa fulani hakanan aure
na shiga tsakanin su khadija ta fitone daga
Hausa Fulani mahaifinta bahaushe inda
mahaifiyarta take bafulatana
dukda qaramin kauyene Amman suna rayuwansu
cikin jin dadi DA kwanciyar hankali sunada
tsangayu na karatun alqur,ani a yayinda
makarantar
Boko sai an yi tafiyar' kusan kilo mita uku kafin a
samu firamari daya jal sabo da karancin Dalibai
da su kansu Malaman. ‘ ' Haka itama Sakandare
(Secondary) a na daf'
Suna karatun Boko dai—dai 'gwargwa'do; sai‘ dai
da alama mutanen Kauyen bokon bai'damesu ba
musamman ma sabo da wadannan abubuwan
Na- farko, ga nisan tsiya kafin akai ga zuwa
Makarantar.
Wani lokacin ga rashin Malamai. da rashin

'fahimta, don haka da yawa suka watsar do karatun. Mahaifin Khadija ba shi da sana'ar da ta wuce Zuma.
Mahaifiyarta kuwa tana sai da Nono ne, ya yin " da Kakartake sana'ar Fura' Sunan .Mahaifin - Khadija Mallam' Audu: Mahaifiyarta kuwa Halima', suna kiranta da" hali' , Su uku rak Mallam Audu ya haifa, dukkan su' Mata ne Jamila ce babba sai Mariya sai kuma ' Khadija wacce ake kiranta da suna DIJA'. ' ' Sunan DEEDA kuwa ya'sam'asali ne'daga wurin Kakarta Inna mai Fura lokacin da aka yayeta' '
ta koma hannunta ta yayeta, in tana kukan 'shagwaBa irin na 'yan yayan nan sai ta yi ta mata Wasa'da; cewa Deeda na yar gidan Inna ma'iFura ". Da haka sunan ya bita duk kauyen sunan DIJAN ya Bata sai 'DEEDA'. ' 'Kusan girma da wayon Deeda ta yi shine a hannun 'Kakarta wacce 'ta haifi Mahaifiyarta kasancewar Inna mai Fura ita kadai ce a gidanta Mijintaya jima da RasUwa-'yan tsoffin da suke tare ko duk sun rasu, 'yan uwa kuWa kowa ya kama gabansa, don haka Deeda ke debe ma ta kewa. Kauna da shakuwata shiga tsakanin-su sosai, duk da Kaka ce Inna mai Fura ba ta yi ma ta goyon Kaka ba, tana kokarin sanyata a hanya da ba ta tarbiyya dai-dai gwargwadon tunaninta da saninta. ,. .
,Iyayen Deeda suna .rayuwa cikin kWanciyar hankali Yayyun Deeda Jamila _da Mariya ba su damu da_'karatun zamani ba, don haka iyaycnsu 'ba su matsa musu ba suna dai Kokarin zuwa" na Allo, shima a kwana a tashi suka watsar.
Matsalarsu ta- fara, ne a lokacin da aka yi Auren Jamila yayar Deeda, an kaita gidan miji washe gari ta tashi da wani irin ciwo marar kyan gani. jikinta ya dawo tamkar waccé ta yi shekaru tana jinya. Mijinta bai Bata. lokaci ba ya dawo da ita
gida ta'dinga jinya.
' Duk .wani abu da suka mallaka sai da ya kare a jinya, masu magani ko ba Kauyen da ba a shiga ba
amma ba nasara 'kowa da irin abin da ya ke fadi

‘ wasu su ce Asiri, wasu Su ce Aljanu, amma" ba wanda ya samo maganin, da haka har'kwanan Jamila ya kare a duniya ta koma ga Mahaliccinta. Haka abin da ya faru da Jamila ma dai irinsa ya faru da Mariya ciwon iri: daya. ne
Daga nan fa aka camfa gidan su Deeda cewa' Aljanu sun aure jinin gidan. '
Wasu kuma suce Aljani. ne ya auri uwarsu ba 'ya'yan mutum bane
' . Wasu kuwa‘ su ce‘ Asiri aka yiwa Babansu wani Saurayi da aka kasa gurin ‘neman auren Mahaifiyarsu. -_
‘ Abin ka da Kauye, Kauyen ma na sosai, ’ akwai karancin-ilimi da wayewa,~haka duk maganin nan da suke ba wanda ya gwada na Asibiti don ba su yarda da shi ba. ‘
. Asalin garin ma wani ’busasshcn (Dispensary) ne don sai a dau tsawon shekaru k0 nurse babu balle Likita. ' Haka nan “sun fi 'bada gaskiya ga maganin gidan akanna Asibiti.' Wannan champi da aka yiwa gidan su' Deeda ya kuntata rayuwar Mallam Audu da. zuri'arsa, ' Dukkan; jama,ar gari sukayanke huld'a dashi,
wai aljani ya auri
' Matarsa k0 haka baibata Iokaci ba ya saketa ya kuma ta. ..
ce ta kwashe kayanta a Iokacin tabar masa gidansa ' Haka nan Deeda ya yafe mata k0 ganin .fuskarta bayasonyi wai don karta. shafa ‘masa cutar maita ta manta ma tana da Uba. shi kuma zai dauka ‘kamar baitaba haihuwar wata'ya- Khadija. a duniya ba
Haka Inna Hali ta koma gidan Inna mai Fura , ; tana' kuka, ta Iabarta mata yadda aka yi.- Inna mai Fura tai ta bata haquri 'gami da kalamai masu ‘_kwantar. da hankali a matsayin .ta’na Uwa, ta shiga qunci .da‘ 'bacin ran ganin 'yarta a wannan hali ga Saki " ga ‘ wulaqanci, 'yar .tasa ma baya so
Sai dai Inna Hali ta fita shiga tashin bankali sabo da Mace mai runi yayin da Inna mai Fura ke karfi hali.‘kawai
' Deeda. na shckara bakwai. rabonta-da ganin

Mahaifinta suna gari daya kuma guri guda amma ko. ahan'ya bai son ganinta, daga karshe ma aurensa ya yi ya ci gaba da' rayuwarsa da sabuwar Matarsa

Wannan bakinciki yayiwa Inna Hali-Yawa, ta _ kwanta Ciwo, haka Deeda ta ga Mahaiflyartacikin ciwo da wahala, tana- tausaya mata har kwananta ya kare ta barta a'hannun Inna mai Fara, lokaci guda Deeda 'ta zama marainiya ba Uwa ba Yayye duk da k0 tana da Uba Amman dashi DA babu duk Daya suke' rayuwarta ta dawo daga ita sai Kakarta. -

Deeda ta, tashi yarinya shiru-shiru da ba ta da magana kwata—kwata, in har ta bude Baki to dole ya zama-za ta. tambayi wani abu ne ko ,ta fadi wani abu ~ mai muhimmanci

Wannan abu da ya yi' ta faruwa a gidansu ya zame mAta~ ayar tambayoyi da yawa a KwaKWalwarta .wanda ba 'ta da amsarsu da alama idonta da zuciyarta tare da Kwakwalwarta' suna, fadawa duniyar yawon neman amsar ne kowanne lokaci.

Wannan al'amari ya dasa 'babban' Ayar 1 "tambaYa a kwakwalWarta Haka Inna mai Fura za'tasata'tai ta yi mata Surutu, wani lokacin Waka, wani lokacin - , Zolaya, wani lokacin 'Ta'tsuniya,' amma'Decda ba ta'" taba tanka ma ta ba sai in ta gaji ta fashé da' kuka.' 'Hakan yasa tsoro ya darsu a zuciyar Inna 'mai ' F ura ta fara :tunanin cewa karfa wani ciwo ya kama Deeda, tana tsoron rasata, don ita kadai 'ta mallaka duk duniya. Sannan tana tunanin idan ta mutu tabarta kuWa ya rayuwar-Deedan zata kasance? bata da kowa bata da komai? - ' ' .

Inna'mai Fura bata gaza ba, ba'ta karaya har ta tashi rokon Allah iya iliminta da kuma da rubu da addu'o'i a wurin Malaman Kauyen. ' . Duk 'yan kwabbanta sun. kare-a. wurin, neman samun canji a tare da Deeda

'Wani yammaci' Deeda ta fita karkashin " gada ka'mar yadda ta saba kullum sabo

" da ba komai take yi ba ba k0 ina take;

zuwa batada DA abokan yawon Amman wani

zubin takan taya Inna Mai hura surfe KO aikin
Gida
rai bace ta shigo gidan Inna Mai hura tai mata
tambayan duniyannan Amman taqi kulata harta
gaji ta koma kan harkokinta kaman daga sama
taji deed na cewa Inna menene wannan dake
fitowa a jikina DA Sauri ta janyota tana dubawa
cikin tashin hankali tace menene wannan deeda
kuma tun yaushe ya Fara fito miki cikin tashin
hankali ta jero mata tambayoyin har biyu
deeda tace na cikina yadan Dade yanxu kuma
harda cinyata yanabin kafafuwata Inna mai hura
ta Saki salati
deeda ta kalleta menene Inna!?tai dan murmushin
DA za,a Iya kiransa DA yaqe tace ba komai gobe
idan Allah ya kaimu Zan kaiki wajen me mAgani
a ranan Inna bata rintsaba don tunda take bata
taba ganini irin wannan ciwonba was he gari DA
sassafe suka nufi wajen Mai magani shimadai
abin sabo ya zame masa amman ya basu wani
magani yace a dinga shafa mata za,a dace a
hanyarsu ta dawowa deeda ta dubi Inna taga
yaddah hankalinta ke a tashe tace inna a kaini
asibity mana Inna ta dubeta tace asibiti sai birni
deeda kumama wannan ciwon naki bana asibity
bane tundaga nan bata sake cewa komai ba shafa
wanna maganin ake Amman Ina Abu sai qara
fesowa yake anyi maganin anyi maganin Amman
Ina hakan baisa an daceba tsoron kada mutane
su game halin DA deeda ke ciki yasa Inna ta Fara
Neman mafitar yaddah zatayi domin ta boye
wannan lalura na deeda
tai dabarar dinka ma ta riguna masu dogon
hannu da tsayi wadda idan ta sa har kusan rufe
mata kafa takeyi, haka kuma rigunan suna da
kwala wadda take rufe mata har wuya. . Abin
wasa-gaske, sai da ta kai wannan abin '
ya bi dukkan jikinta ya gewa'ye, ya zamo fuskarta
ce kawai ta tsira. ,
Wannan kalar kayan su suka zama kayan
Deeda. . ' ' Akwana a tashi bar Deeda da Kakarta
suka saba da lalurarta.
Deeda na da shekara tara ta matsawa Inna mai'

Fura akan ta sakata a makarantar Boko, yara tsiraru ' da take gani a garin suna zuwa boko ne hakan ya ba ‘ ta sha,awa, _ta sawa ranta' Son karatu; Inna k0 ta ce sam ba bokon da za ta sakata in ba neman fallasa ba yanzu ma tana da lalura ta ce za ta shiga Makaranta?
Nan fa Deeda ta dage, kukan rana daban, na dare daban, haka ma na safe daban, har da rashin lafiya. Dole Inna mai Fura ba don ta so ba 'ta amince
akan za ta sakata a makarantar.
Ranar kasuwar dawakin Tofa ta fito ita da Deeda da kafa, ta tattara 'yan kwabbanta ta saya ma ta irin kayan gwanjon nan biri da wando na dai-dai shekarunta ta sai ma ta guda hudu, biyu‘masu nauyi biyu marasa nauyi. '
Duka kayan da Deeda za ta saka sai ta saka ' wadannan biri da wandon ta ciki, idan ta sasu a ciki k0 yatsanta ba a gani balle jikinta sai fuskarta kawai.
Inna mai Fura ta yiwa Deeda Kokari kwarai wajen sa ta a Makaranta daukan nauyinta da mata dawainiya ba ta gajiya ba, haka ta sai ma ta Littattafai, wani lokaci ta rakata wani lokacin taje ita daya har ta-saba kwarai karatu na debe mata kewa gata da naci da jajircewa akan sai ta koya don duk da ba ta kokari da fahimtar karatun naci ke sa ta ganewa. Mutanen Kauycn suyi ma ta caa! 'Akan Makarantar Deeda, Inna mai - Fura ta tsaya, tsayin daka ta kwato ma ta 'Yanci, kasancewarta Mace mai Baki da' fadan tsiya, dole suka Kyalesu, har ma suka saba da ganin Deeda a . hakan, tun shigarta da take na ’kayan da take sawa naba wasu'mamaki suna tsegumi har suka gaji suka daina‘ don Inna bata bai wa kowa damar yi musu shisshigi‘ ba, kowa tana ba shi amsa'dai-dai da shi ne. .
Komai tsananin Sanyin da ake k0 Zafl shigar Deeda ba"ta canjaWa "illa iyaka lokacin Zafi ta saka
marasa nauyi , lokacin Sanyi kuma ta sa masu 'nauyi.
‘ Haka nan daga sun fara tsufa Inna mai Fara za

tara Asusunta ta shiga kasuwa ta siyo mata
wasu
Abinda kebai wa Inna mai Fara mamaki shi ne, '
wannan abu bai san ya tafi koya ragu ba ina illa
iyaka ya ya zauna daram ne a jikinta.
Wannan da shi‘ Inna mai Fura kekwana ta tashi’
gami da adduhr Allah Ya yi musu maganin abin.
** ' ** *
' tabawa Kawa ce kuma aminiya ga Mahaifiyar
Dceda kafin ta rasu, don ko abinda ke faruwa na‘
rayuwar gidansu Deeda
ba abin da ba ta sani ba dana ta auren ya mum
tayi nasarar fita daga Kauyen ta sahun shiga
cikin garin Dawakin Tofu, daga nan ta samu
Aikatau a‘ cikin garin Kano gidan wani Alhaji ta
koma can ma ‘ tana musu Girki da Shara, duk
kuwa me son dan Aiki ita ce me‘ shiga kauyuka
tana nema musu masu aikin ana dan biyanta
wani abun, don haka ta shahara har
ta samu fili ta gina dakuna biyu da Kicin da kuma
Bayi. .
_ Ta jima tana nacin daukar Decda amma Inna
mai hura taki, ko da wasa har Deeda ta girma
Tabawa ba ta gajiyawa da yiwa Inna mai hura
maganan daukar Deeda ba ta hanyar kwadaita
ma ta yadda rayuwar BIRNI ta keda yadda
Deedan za ta. samu canjin rayuwa da canjin wuri,
har ma dai ta ce mata in tana so sai su taho tare
har da ita, in ma don ba ta son rabuwa da ita ne.
.
Anan fa Inna mai hura ta fara yarda da maganar
Tabawa, har ma ta fada ma ta Ialurar Deeda. '
Nan Tabawa ta nuna ma ta tun da~ ai ba
kwanciya ciwon ta yi ba da Iafiyarta ai shi kenan.
‘ '
A wannan Iokacin Deeda na aji biyu na gaba da
firamire.
Ya yin da Deeda ta ji batun zuwanta Aikatau ta
nuna musu ba za ta je ba, ba yadda ba su yi ba
amma ta Ki amincewa. Damuwar Inna mai Fura
ma ita ce yadda ake zaginta a Kauyen da yadda
aka camfata da cewa 'yar Aljani ce
Ba Mijin aure, ba Saurayi, ba Abokin wasa ba

na Hira.
Ba zai yiwu ace su yi'ta rayuwa su biyuba sa '
haka bada kowa'ba. ,
Tabbas tana son .yiwa Deeda canjin rayuwa,
kuma hakan ba zai yiwu ba sai ta bar Kauyen.“
A tunaninta in sun dace suma za su- iya samun
gida kamar Tabawa, sam ba aikin ta sowa Deeda
ba, sai son barin garin, ku'ma basu da hanyar
barin garin da wannan Kauyen sai ta hanyar
Tabawa.
A halin yanzu Deeda na aji biyu na Sakandare
(Secondary). Duk wahala duk wuya ,duk kishirwa
da yunwa baya hanata "zuwa Makaranta duk da
dai ,karatu irin na Kauye amma ba laifi ta san
abubuwa ‘da .dama, haka kuma. tana kokarin
zuwa karatun
;Allo, daga Karshe aka ce ta yi' girma aka korata
ta
daina zuwa. Haka ta hakura don dole. '
Kullum Tabawa ta zo da maganar sai sun yi
fada daKarta tazageta tayi matagori wai don
ko zatayi zuciya tace zataje ammaharyanxu ba ta
yi nasara'ba.
Wannan shine ,takaitaccen tarihi Deeda da
Kauyensu. .
bayan Deeda‘ ta gama kukanta gab da~
Magariba ta koma gida, ba ta kula Inna ' ba,
haka nan itama Innan ba ta kulata. ba alamar
suna fishi da juna har bayan issha. Deeda k0
Abinci ba ta ci ba’ ta kwanta.
Abin ya dami Inna ‘mai Fura kwarai, ta kasa
bacci, ta samu Deedan a' daki, shesshekar kukan
da taji ne ya tabbatar‘ mata: idonta biyu, kuma
har yanzu kuka ta ke. -'
"Deeda". Inna ta kira sunanta.
"Ki yi 'hakuri nasan ban kyauta ba, na san bani
da kirki, ina son kai ki Aikatau Birni, ki yi haquri
kar ki daga rai, insha Allahu daga yau ba zan
sake yi' miki maganar zuwa’Birni ba na zama mai
son kai".
‘ Ta sake cewa
"Deeda sona ki rabu da Kauye nan k0 ta halin
kaka, ganin irin, hazakarki da irin yadda KiKeso ki

yi ilimi da duk wasu bincikenki da' amsoshin
tambayoyinki'. a Kauyen ~ nan babu maganan
matsalarki deeda
na miki gori amma Deeda duk bai sa kin canja
ra'ayi ba, shin Deeda in na mutu ya za ki yi?"
Decda da ke kwance tana kuka tun da' Inna ta
fara magana sai lokacin tayi saurin" juyowa ta
rungumi Kakarta tana kuka.
"Inna ki yi hakuri na miki mummunan fassara,
ban fahimce ki ba, Inna yanzu da ki ka_ yi . min
maganar mutuwa sai na ji hankalina ya tashi,
wani irin tsoro ya shigeni Inna hala ma in riga ki
mutuwa, idan na mutu kema za ki zama ke 'daya.
Inna kece komai na, niCe komanki, Inna Allah na
tare da mu yana ganin halin da muke ciki in
tafiyarmu Birni shi ne mafi alkhairi, Allah Ya
tabbatar mana, ki cewa Tabawa ashirye na ke da
in bita a duk lokacin da ta shirya daukana zamu
bita".
Inna mai Fura ta rungumeta Deeda cikin tsananin
farinciki tana' fadin, "Allah, Ya miki
albarka
Da sassafe k0 Inna ta daga sammako sai -
masaukin Tabawa'don kar ta bata lokaci ta koma
Birni. "
Ganinta da farar safiya ya bawa Tabawa'
. mamaki, bayan sun gaisa tace; "Lafiya dai ko
Inna?" ~ Inna ta yi murmushi' ta ce, "Tabawa
yau dai andace Deeda ta yarda zamu bi ki". ' - '
Tabawa ta washe Baki. . _ "Kai madallah, amma
na ji dadin labarin nan 'da yardar Allah kuwa ba
za ta yi dana-sani ba, sai ku shirya bayan Azahar
mu' tafi, ina ce dai kuna da kudin Mota k0?"
Tabawa ta tambaya.- -. Inna ta ce "Muna da shi,
duk da ba yawa, jiya nayi cinikin hur da Surfc, in
ma ya kasa sai ki yi mama ciko". 'tabawa ta ce,
"To shi ke nan ba laifi". Bayan, 'A'zahar "din
kuwa suka. 'tattara' yan kayansu da abin biyau
bukatarsu, Inna ta ja gida ta rufe duk da dai ba
wani abin kirki ciki,' Gadonta ne sai 'yan Tukwane
da suuran kayan amfanin Kicin' ta
ja kofar langa-langa ta rufe.
Mahaifin Deeda bai sani ba, kuma bai nemij ya

sani ba, amma duk da hakan sai da Inna mai Fur ta kai ta suka yi masa sallama, ya kau dakai ya ce "In ta ga dama ma ta saida ita shi bai dameshi ba".
A fusace Inna ta bar gidan ya yin da Deeda ta durkusa ta ce, "Baba addu'arka na ke buqata".
' “Sauka lafiya Allah Ya ba da sa'a". Abin da ya fada ke nan, ya‘ tashi ya barta a wurin. ta mike cikin kunar zuciya da Bacin rai tace "Amin".,
_,.,.Ta fita-tasamesu sukai sallama-da wanda Suk"dace a garin, sannan suka kama hanyar barin Kauyen da kafa har zuwa inda za su sami mota. ‘ Rana ta farko ke nan da suka taBa shiga Mota ‘(Bus) aka sa su a kujerar .qarshe, Inna mai Fura" akai ta buga qauyanci duk lokacin da-Mota ta shiga kwana k0 gargada saita'yi ihu, Tabawa‘na mata dariya, yayin da Deeda ta kifa kai tana tunani, wani, lokacin ta dan yi dariyar‘ Inna darkanta, don itama takan dan taBa Kau'yancin, sai ’ dai- ba ta" nunawa a fili" , Lokacin da' suka- hau titi 'zurawa bishiyoyi ido tayi tana kallonsu suna gudu,‘ tana kallon .ikon Allah, Inna mai Fura ko tuni bacci ya kwasheta da ta ji gargada ya Kare, Tabawa k0 saka musu ido tayi tana tunanin tabbas sai ta zauna da su na dan'wani lokaci ta gyarasu sun dan 'waye kadan kafin ta kai ga kai su wani gidan aiki, don ta yi, niyyar Inna ma‘ko wanke—wanke kadai ta dinga yi'za ta kawo kudi, yayin da Deeda dama ’dai-dai shekarunta Hajiya ta ce ta samo 'wanda hakan ya ma. ta wuya sabo da duk sa'anninta sunyi raure hakan ya sa zuwan'Deeda'ya ma ta dadi dOn ta san tabbas Hajiya zata ba ta' kudi mai. tsoka, don haka ya‘ zama dole sai ta gyara Deeda ta kuma' nuna musu yadda‘rayuwar'Birni take.Da irin wayennan. tunane-tunanen suka iso _ cikin ,Birnin Kanon Dabo, su 'Inna mai 'hura an sha‘ kallo, duk Wanda ya kallesu‘ dole sai ya sa musu alamar tambaya, da .Kyar Tabawa” ta samu suka tsallaka titi, ta_ sama musu Adai-daita sahu suka ' shiga, wannan karon da aka zo tudu da gangara da kwana har da su Deeda a ihu, sai. damai Adai-daita ‘ Sabun ya tsorata ya

tsaya ya dinga masifa da kyar da, . kyar tabawa
ta .rarrasheshi ya‘karasa da su gidanta ‘dake tal
udu ' Dakuna biyu ne sai tsakar gida da kuma
bayi a gefe da ‘alamar Tabawa ba ta gama ginin
nata ba, ta dai
Wai cewa ake babba ya san komai, dama kullum
abin na damunta, ya za a yi babba' ya san komai
bayan ba a koya masa ba?
Ta yi murmushi. . -.
Lallai idan abin da nake gani shine birni to lallai
bazan taba Dana sanin shigoba da alamun burina
zai-cika ".
Deeda ta fada a ranta. ‘
Kiran Sallar Magariba ne ya katse ma ta abin'da
take yi, ta dawo cikin gida don yin sallah.
Kusan kwana suka yi Tabawa na ba su labarin
Birni da yadda ake rayuwarsu,a ciki akwai'
banbanci sosai da na Kauye.
Ta kara da. ce musu, "-Indai suna'so su‘ji ’ dadin
zama to su dage da sana'a su nemi na kanSu,
banda zaman banza
Inna mai Fura -ta ‘fahimci. me Tabawa ta ke nufi
sai dai ita fa tunaninta daban, burinta shi ne ta
inganta rayuwar Deeda ta kai ta. Asibiti ta kuma
sakata a Makaranta irin na Birn
,' "Amma anya Tabawa za ta yarda taci gaba DA
ajemu a gidanta ba tare DA deeda ta mata
amfanin data daukota musamman dominshiba
kuwa?
ohhhhhhhhooooo
taya za,ai admin ya isa Sani mu hadu a next
chapter donjin ci gaba
Birnin gayu
chapter2
Da wadannan 'tunane tunanen da ‘hanyar shawa
kan matsala_bacci ya dauke Inna mai' F ura'.'
‘Kira‘n sallar: farko akunnen Deeda,‘ akai ta ji’ ..
kiran‘ Sallar a Cikin. Gidan ya ba‘ta mamaki, ,
musamman da ta-dinga jin k0 ta ina 'sallah ‘ake,
' Masallatai daban-daban. ‘ Ta ‘mike ta yi»
Alwala tana” jinjina abin, zuciyarta ta yi ma ta
fari,‘ ta yi godiya ga Allah da Ya sata shigo Birni.
' " Tabbas ,datasan‘“ haka; Birni yake data jima

dabiyo TabaWa. ' Kafin gari ya washe' har ‘tana Tabawa. shara,’ ‘gogegoge da‘ wanké-wanke- Abin'ya yiwa Tabawa dadi sosoi.
Lallai‘zata ci Riba da Deeda, ba ta da kwiuya Karar Motoci “yasa' ta fit0wa Kofar gida kasancewar bakin Titi ne, ta zauna a Karkashin wata ; Bishiya tana kallon Titi tana shakar iskar sanyin'
safiya mai albarka, hakan "ba‘ Karamin nishadi da farinciki ya‘jefa a zuciyarta ba Tananan zaune :tana murmushi' ta soma ganin .'yan Makarantar Boko na wucewa ,sanye‘, Riga da Wando da Hijabi;
ta miqe tabi cikinsu tana tafiya, nan ta hangu (Gate) din Makarantar; -an rubuta "(NANA AISHA ISLAMIYYA, PRIMARY AND SECONDARY SCHOOL)". Ta ga an mbuta a jikin bangon K0far Makaranta
Ta jima tana tsaye tana kallonsu suna shiga cikin Makarantar, Wasu sa'ann'inta, wasu kuma sun fita, wasu kuma qannenta maza da'mata. ‘
Kwarai tayi sha‘awar ,itama ace tana daya daga_ cikinsu, sai dai ta_san abu ‘ ne mai matukar wahala.
Sai da‘ taga an rufe (Gate) din Makarantar . sannan ta juya ta _ daWo gida, ta ' samu .Tabawa ta yi musu abin Karyawa za ta fita.
Ta kalleta ta' ce,""Ina ki :ka shiga ne Deeda? Na leka waje ban ganki ba. Ki daina'nisa fa kar ki Bata".
Deeda ta yi murmushi. ‘
"Ba zan‘ Bata Ba Tabawa insha‘Allahu, 'yan Makaranta da Shaguna na gani a titi na bi ina kallo". TabaWan ta yi dariya ta ce, "Deeda kenan,
nan fa Birni ne ba Kauye‘ba, Birnin ma fa Kanon " Dabo, babban; gari wasa ba, a hankali yau da gobe za ki fahimta‘, in kin biyewa kallon Makaranta da Shaguna‘ kuwa to sai ki dau tsawon ,shekaru kina yi ba ki‘ gama ba Ki zo ki karya ni zan fita, zan
. je gidan dana ke aiki sannan in je in yiwa gidan dana daukomusu ke magana mutattauna akan

yaushe za,a kaiki ki '
. Dam! Ta ji gabanta ya yanke ya: fadi, ta bi '
Tabawa da kallo yayin DA take fita daga gidan, ta ji
hankalintaya tashi, ta manta Aikatau tazoyi a Birni'
shine har' ta'fara tunani da Wani burinta na datun
Nan da nan idonta ya ciko da hawaye. ta ji tana
son yin kuka ta juya sukai ido biyu da kaka ta
fada'Cinyarta tana kuka.'
Ta ce "Kaka banason aiki gidan kowa, Kaka-ina
son yini karatu". "Kiyi~haquri Deeda dole mu yi
'haquri da halin da muka. tsinci kanmu ba ke kadai ba ce
' keda wannan' buri ba har ni ma ina da wannan:
buri akanki. ' .
Karki damu, mu yi ta addu'a sanan a hankali
zamu cimma nasara; A halin yanzu dole mu fara
da . haka zuwa gaba maga abin,da Allah zaiyi ..
Nan Kakar ta'yita kwantar mata da hankali har ta
samu'nutsuwa. Haka suka' yini har yamma lis!
_sannan . TabaWa ta dawo a gajiye, ta samu
Inna mai Fura ta 'yi sana'ar na ta, wato Fura, tun
da ba ta barmusu ko abinci ba, ganin garin gero
da' suga yasa ta yi musu lafiyayyiyar Fura, ta bai
wa Deeda kudi ta siyo masu _ nono a bakin'
hanya gun: Fulani-wajenda ta ga suna kawo'wa
wasu masu Gini ' 'Nan fa Tabawa-ta 'zauna ta
sha none da'Fura osai tana santi, saunan ta tuna"
Ba ta bar musu abinci tayi hamdala sannan ta
ce, "Kin kyauta Inna, tabbas,don'kinyi dabara-irin
ba bana Kauye ba don hakaba da kun zauna'da
yunwa, na mancé, ina sauri na saba in na tafi ba'
kowa a gida, don haka tunanin Abinci , , "ma bai
zo min ba; kun ga-harnima nasamu na sha~ '
don ban tsaya cin Abinci a can ba,'~ ina san in
samu inshiga BIRNIN GAYU ne Déeda tajuya ta
kalleta. inane kuma BIRNIN GAYU?"
Tabawa ta kalleta cike da mamaki ta' ce
"Kina nan'cikin Kauyen Kanonnan baki san
BIRNIN GAYU ba?" ~ Deeda ta daga kai cike da
kosawa tace,' "ina'zan sani ina Kauyen'Kano' ba

Birniba?". "To Kakarki ai ta sani", In ji Tabawai . zatayi miki bayani, kuma shi ne Gidan da» Matar da ta ce- in dauko miki ita tace tana son 'Yarinya mai kamar shekarunki, suna da masu aiki; ma‘za da ‘mata‘ na wasu qasa ma. haka~ suna da; ., manyan Mata na nan qasar sai dai 'yan matan naga' duk kamar 'ba Hausawa bane, na ga har wani 'unifom) suke sakawa na‘su na masu Aiki.‘ ~Sai dai duk da haka ta ce tana son in nemo mata 'yar— Budurwa Bahaushiya haka wacce zata dinga; kula da Bangaren dakinta bisa ga‘ wannan, kuma-tana son yar gidan mutunci mai hankali, don hakan .shiyasa na dauko mata ke; Na san yadda take so haka‘ki‘ ke har ma kin, 'wuce tsammaninta, kuma karki ga kamar aikin wahala ne dan gyaran Dakinta ai ‘ba‘ matsala bane, gashi kuma kiyini a cikin A.C ki kwana a A,c 'ki sa mai kyau, ki Ci mai kyau ki sha mai kyau, to me ya ’ wannan 'hutu?
, Ai da tsohuwa take so da tuni‘naje k0 da ina da 'yar uwa k0 'ya k0 jikar da‘ ba su yi aure‘ba da na kai ma ta don Zama da wadannan ai alheri ne An yi ta kawo 'mata yan ‘matan'Birni ma ganin duk rayuwarta a kasa‘shen waje tayi‘ tace wai ita ba ta son marasa. kunya Wadanda idonsu ya“ bude wadanda za su yi tayi‘ma ta sata ko wani mugun hali. Kin san sha’anin masu kudi sai su. Deeda‘dai da Inna mai Fura sun sa ma ta 'idone' sunaji kuma suna kallonta kamar wata Talabijin 'Duk wannan kurara? gidan da take yi ammahakan bai sa Deeda taji tana sha,awar zuwa gidan ba sabo da karatunta yaf1 mata jin dadin da Tabawa take
kirgo,mata Tabawa ta ci’gaba ’da'cewa, "daganan gidan na biya na bata lokaci ina jiranta kafin ta fito nayi mata bayanin na- daukoki shi ne ta bani wasu kudade tace-.ayi .miki: siyayyar Sutura ‘mai 'kyau da abin‘ " buKatarki ki fito a mutum sosai, bata So kizo mata da wani daudar Kauye
'Tun daga' kan Sabulu, Turare, Mai; Takal'mai zuwa Kaya tace komair Sabo” take so ‘Sannan a nuna miki yadda-zaman Birni yake da yaddah

zakiyi my,amala DA mutane
sannan tace a sakaki a Makarantar koyon
Komfuta, (Computer), k0 menene sunansa,
wannan abin' latsawar kamar Talabijin.
' .Deeda da kanta 'ke sunkuye tayi ~
. saurin .daga kanta, tana juya abin a ranta anya
duk
duniya akwai abin da take son ,koya kamar
(Computer) kuwa? Ta yi dariya cikin 'doki "tace
dan Allah tabawa da gaske ki' ke zan shiga
,wannan Makarantar?" " kwarai"; Tabawa ta
tabbatar mata
"Ga'kudin'komai ta bani, 'da mutumin da zai kaiki
sanda za ki fara zuwa ya
. _ miki komai, wai so take ki dinga shiga
da Wasu abubuwanta wanda "qila sirri ne don
BABB-MACE. ce, Mace mai ilimin. kakuwmi- sosai
kullum, lissafi take na shigar kudi da fitarsa
da'kuma'saida Kaya harsu Gwala-gwalai da irin
gadajen 'qasar wajennan take saidawa _. Ina jin
shi yasa ta ke neman mataimakiya don abin 'ya
yi ma ta-yawa, yayanta
biyu kuma duk suna kasar waje. Naji dai 'an ce
kwanaki akwai 'yan uwanta masu' ilimi da sukai
ta
cutarta, amma dai jita-jita na ji. Ta ce dai a
sakaki ki koyi na wata uku, sannan a wata shidan
nan kafin ta dawo tana son ganinki tsab
Kinga makudan kudaden da ta bani, nima ai na
samu rabona
Lokacin dq Tabawa ta ciro kudin Inna mai- Fura
ta bude baki ta kasa magana don tunda take k0 a
Mafarki bata taBa ganin irin wadannan makudan
kudaden ba masu yaWa haka.
Ba su ankara ba sai ga Inna mai Fura a zube a
qasa, suma neta tayi k0 dai firgita ta yi da'
'ganin tsabar kudaden a zahiri shi .ya sa ta
faduwa, Allah ne kadai Ya sani. '
. Tabawa- dai sai da dariya takeyi
Deeda tana tayqta suka sannan suka dagota'
*.* ** ,*.*
Deeda 'da Inna mai Fura ba wanda ya kaisu
farincikin shigarta (Computer School), duk' da ba

ta gane manufar Hajiya na‘ Sonta ga ta koyi sarrafa (Computcr) ba, ita a nata tunanin ta samu hanyar koyon wani ilimi da
ba ta sani ba, wannan iliminma:inta samu nata ne ba. mai‘rabata da shi sai Allah. ‘ Musamman- Hajiyar :ta' hada Deeda da Taba'wa da wata mata suka'shiga’ kasuwa don yiwo ma ta siyayyar irinkayan da take So ta ga ta saka. ' Kaya ne irin na zamani, wasu‘riga da wando ne, wasu riga da siket, Wasu dogayen ‘ riguna dinkakku wato (Red made), wasu kuma habayas irin na zamani kala-kala.Haka Takalma zuwa kayan ciki; su shimi, (vsst), bra da‘ makamantansu, sannan Hijabai‘ na Sallah manya. . ‘ Ganin yanayin shigarta ya sa matar ta'siya mata (Body shaft) masu kyau‘da tsada a tunaninta haka take son yanayin shigarta a matsayinta na ‘yar Bahaushiya. haka ba ta son barin jikinta a waje ne ko
kuma dai qila haka na ta kalar gayun yake, don Tabawa dai ta boye musu lalurar Deeda Cikin kayayyakin Deeda ‘ kuwa harda Kwat" (Coat) irin na Mata mai hade da Siket.
ita dai sa wa kayan ido ta yi tana mamakin ta yanda za ta fara sakasu a jikinta.
Ta wani Bangaren Kuma tana tunanin wacce irin' Mace ce ita da zai sa ta kashewa mai aiki kudi haka, anya kuwa ba wani abu Wanda ba su sani ba? , Tana cikin wannan tunanin ta ji mota ta tsaya kofar wani babban shago. (Beauty Palace) to ga an- rubuta an rubuta. Tabawa ne taja hannunta‘ suka bi matar ciki. ‘ . A nan akai ta tsiya da Deeda don da 'kyar ta bari suka ma ta gyaran gashi, ta Bata rai ta dinga zazzaga musu masifa ta qara da cewa in ba za su dauketa a yadda ta ke a" yadda ta ke to ita zata FASA don ikon da suke mata ya isheta‘ da qar Tabawa‘ta lallaBata suka dawo
Tabawa Matar haquri. ' ‘ Deeda’ da Kakarta Suka tsare Tabawa da tambayar céwa ta fada musu gaskiya in ta san akwai illa k0 wani abu mara-kyau a tattare da inda zata ‘aikin, gara ta‘fada musu su sani‘ deeda ta yi ma ta rantsuwada

cewa in taje ta 'tarar da abin da bata zata ba to
za ta bar Gidan sai . dai abin da zai 'faru. ya faru
Tabawa ta washe baki tana dariya. tana. qokarin
kwantar musu da hankali da tabbatar musu
da cewa ba wani mummunan aiki k0 wani illa a
Gidan, kawai dai su Manja ne masu tsama tsab-
tsab, bayan shi babu wani abu.
Da irin wannan bayanin Tabawa ta gamsar da su,
ya yin da Inna mai F ura ta ci gaba da-burin kai
Deeda Asibiti.
*.* . *§*' *,*
KWANA-A-TAShi Deeda da Kaka "suka saba da
rayuwa; cikin garin Kano, ' wani abu da ke yiwa-
Deeda dadi shi ne, yanda ta samu riba biyu lokaci
guda, kasancewar Computer Class dinta qarfe
daya ne ya sa ta lallaBa Tabawa ta sakata a
Makarantar ’dake unguwarsu,” wato "(NANA
AISHA SECONDAR Y
SCHOOL)"wanda hade ya ke da. Arabic-da Boko.’
Tayi sa,a sun dauketa aji hudu bayan anyi mata
Interview.
Tabawa ta dinka mata (Uniform) tare da siya ma
ta Takardu, ya yin da Kakarta ta yi buga bugar
hada kudi ta biya ma ta kudin Makarantar, .
bakarantar gwanmati ba né, na kudi ce kudi, '
amma dai ba zai gagari Talaka ba,
‘Ba‘shin kudi Inna mai Furta' ta karba Wurin
Tabawa, don haka ta dage da sana'ar Furanta
ganin
ya samu karBuwa sosai. ‘
Tabawa‘ ke aikawa Kauye ana siyo musu
madara mai kyau suna Nono da Fura mai dadi,
yayin da masu shago ke layin zuwa sari suna
sawa a
‘Fridge suna sayarwa.
Sana'ar kam ta ' karbu’ ‘ sosai, Allah Ya
albarkaci sana'ar, daga Tabawan har Inna mai
Fura
‘ ‘ Suna samu sosai a ciki, don haka Inna mai
Fura ta
biya Tabawa bashinta, haka ta budewa ‘deeda
asusun makaranta da Asibiti.
Dewda kam ba laifi tana fahimtar Karatunta,

fana jin dadinsa, musamman Makarantar da ta shiga
tana fahimtar abubuwa da yawa
Wanda ba ta sani ba, wanda. ya shige ma ta duhu
kuwa ba ta Bata lokacin tambaya har sai ta fahimta. Karfe daya suke tashi ta dawo Gida da wuri
tayi Sallah kuma ta wuce (Computer Classes) dinta wani lokaci in sun taso ta kan taimakawa Inna da
aikin Furanta tare da taimakawa da aikace aikacen Gida.
Inna wani lokaci ta kan hanata ta ce ita mai da hankali ta yi karatu, ita kuma za ta dage da: sana'a da neman kudi da mata addu'a domin ta ga ta cimma burinta.
A duk lokacin da Inna mai Fura ta fadima Deeda haka ta kan fada jikinta tana hawaye tace Kaka Allah Ya barni da ke, Allah Ya ba ni ikon yi miki abin da ki ka min, Allah Ya kaimu lokacin da ' za ki huta, ni in nema miki in miki gata kamar yandda ki ka min.
Kaka ba don ke ba ban san ya rayuwata zata kare -ba..Na gode Kaka, Allah Ya biyaki duniya da ' lahira". ' " Inna mai Fura ta yi murmushi ta' ce, "Deeda‘ wa na keda shi duk duniya idan ba ke ba?
Allah dai Ya cika min burina akanki, ki samu duk abin da ki ke so, Allah Ya ba ki miji na gari mai tausayinki, wanda zai kula da ke.
Deeda Allah Ya ba ki lafiya, Allah Ya min burina in ganki Gidan miji kafin in mum."
Deeda ta fada cinyar Kakarta tuna juya kalaman Inna mai Fura don ya daga mata hankali, ita dai ba ta da tsammanin yin aure a rayuwarta don zai ta samu namijin da zai sota har ma ya yarda da ita a yadda take.
A duk lokacin da ta kalli fatar‘jikinta ta ga yadda ya nannade ya yamutse sai ta ji hankalinta ya
' yi mummunan tashi, ta fashe da kuka, “tausayin kanta

ya kamata, ya yin da ta shiga tunanin wane irin
ciwo ne haka? K0 kuma ita haka nata halittar ya
ke?
. Alhamdu lillah! Allah na gode ma ka da ka
Barni da hankalina da kuma rai da lafiya ta, k0
kowa
bai soni ba zan'so kaina. Haka Kakata na tare da
ni,
Allah abin godiya".
*9* *9*
WATA UKU KACAL! ‘Deeda tayi ta
" san Computer da yadda ake sarrafata
kasancewar ta samu kwararrun Malamai,
“"“haka nan tana da naci da son sanin abin da ba
ta sani ba, musamman ma dai Computér din da
saninsa da koyonsa yana daya daga cikin burinta
tuni Deeda da Kakarta suka saba da rayuwar
Birni‘da irin yanayin yadda suke rayuwa da‘
mu'amala da su, jama'ar ’unguwa da dama sun
santa sabo’ da suna gannin tana shiga da fita
tsakanin Makaranta zuwa shaguna kai
Fura da Nono, wani lokacin haka nan tana da
wani irin yanayi na daukan hankali tundagakan
irin shigar da ta kena kaya wato dresing zuwa
tafiyarta. maganarta, kalamanta a nutse ta ke
yinsa komai nata dabam, sam ba ta da rawan kai
irin na 'yan mata sa'anninta' ba ta da shisshigi,
ba ta shiga harkar matan makaranta yasa a
Ajinsu ba, da makarantar gaba daya sai dai
gaisuwar mutunci da maganar da ya zama dole,,
bayan shi Deeds bata mu'amala da wasu bayan
Kakarta da Tabawa, Deeda wankan taiwada ce
tana‘ da tsayi‘ kadan da Kyan Diri, wato Kira mai
kyau, fuskarta bata cika wani Kyau ba, sai dai
Allah Ya batajini, tana da saurin shiga rai, bata da
magana ko raini, Mishkila ce mai ra'ayin tsiya
duk yadda abu koya mata dadi baiwuce tayi
Murmushiba haka duk' tsananin abu da Zafinsa
bai wuce Idonta ya kada? ya yi Jaba ko qallah.
Tana da Dauriya da kunya.
zAUNE YAKE kan kujera ya harde hannunsa a
‘kirji gami da daura Kafa ‘ dayakan daya.
Ya sawa Sabeer ido, bacci‘ ya ke yi sosai basi da

k0 alamar bude ido balle ya yi shirin fita. "Sabeer Ibrahim ya kira sunansa
- .Cikin nutsuWa_ bai _kula shiba ya ci gaba DA ' baccinsa. Ya’mike ya isa dab da: gadon ya girgizashi.
"Sabeer ya 'kamata‘ ka tashi ko ka manta munada shiga Asibiji yau ne? Cikin muryar Bacci yace, "please
ka barni in yi Baccina,_Asibitin .sai gobe A Nan ya qara lumewa cikin Bargo Ibrahim’ya ‘ yi murmuhi ya; ce, 'Gobenma sai jibi k0?" ,‘ ‘- . Nan ya sa hannu ya dauko Wayarsa ya soma lallatsawa, alamar waya zai kira."Yayata". Ya fada yana murmushi. Ya ce, Wannan; Babyn nakifa banajin ‘ akwai abin da zai 'iya yi a rayuwarsa bayan 'bacci da zuwa yawon- shaqatawa itama murmushin ta sakar masa tace na Sani qanina sanin halin babyn nawa yasa yasa na damqashi a hannunka kafin na dawo na san/zaka 'iya shawo kan shi kuma na ga' - Daddy ma ya'sashi a gaba ka yi kokarin tashinsa in ya ki ka tuna masa sharadin Daddy zai mike da .wuri" i
Ibrahim ya ja” 'dogon numfashi gami da“ ’ fadada murmushinsa ya ce "(Thanks) Yayata, ban san ya Zan yi da Matsalolina ba, inda ba kya tare dani kina bani shawarwari ‘dakwarin guiwa.DA bansan ya zamba Allah Ya bar ni da ke'Yaya ta -.-Ta yi murmushi (Allah Ya bar ni‘da kai Kanina. Ina godiya fatan Ranina yana cikin koshin lafiya". Shiru ya yi 'nadan wani lokaci bai ‘amsa mata _' ‘ ba, sai saukar numfashinsa da ta keji itama 'dan ta kasace masa komai, ya katse shirun da ceWa ina’fatan kina samun nasarar abin da ya kai ki‘ "Eh".'Ta amSa.taRaicc. ‘to Ki kula-da kanki . Bai saurari amsa'r taba ya katse wayar ya jima yana kallon Wayar-tamkar Mai karantar wani abu sannan ya mai da ta .Aljihu ya dubi gadon‘ Sabeer
ya yi sau’rin janye Bargon gami da matsawa dab da Kunnensa ya ce, "Albishir-Sabeer, Dady'ya ce ba kai ba komawa Canada har sai ka yi aikin da ya kawoka ka yi.,.na san dai ,Daddy‘wata uku

yaba ka, in ba hakaba kuwa, ka ci wata daya
baka kulla komai,ba . hakan ‘yana nufin zaman
naija daram idan ka sall‘lake wata, ukun nan ba-
kai ba komawa ‘ Saunan kuma na ji labarin ya.
samu’wata a can yar Kauyc za a hadaku aure"
wat Ya fada da karfi? gami da' mikewa da sauri.
' ' . Ya kalli' Ibrahim cikin zare ido da alamar
tsorata ya ce; "Uncle ib ka rufa min asiri Ka san
na tsani jin k0 maganar Aure ko da (Classy
girls)ce balle'yar Kauyc?" Ya batafuska. ' 'Ka 'san
yadda na tsani abu mara kyau, mara aji‘ kuwa?
Na tsani Mutan Kauyen su Daddyn 'yan' Matan
Kauycn duk munana‘ne, kuma» qazamai,‘jiki duk
Tabo (No way), ba ‘zan iya Auren (Villegers ba)
Yana magana yana ‘yamutsa fuska, ya nufi Bayi
don .yin Wanka.
birnin gayu(season1)
chapter3
ibrahim" ya bishi da kallo yana nazarin'
kalamansa hankalinsa Yayi matukar tashi; Shin ta
ya ya zai soma gyara Sabeer dan ya yi nisa, ya
tashi a wata irin aqida da da‘bi‘a kuma lallai
akwai aiki agabansa, don ya yiwa Yayarsa
alqawarin zai gyara Sabeer zai nunA masa
hanyar gaskiya duk‘da baisan "ta ina zai faraba
Allah Ya taiméke ni”. Ya fada a ransa'ya“ ' bude
wadrof ya ciro masa kayan da zai 'sa,"ya‘ ajiye A
gadon sannan ya fita don ganin an shirya
masa‘break abin karyawa. ' James! Jamcs!
james!!!”' " .,kiran sunansa yake da karfi Cikin
hasala ‘ransa ya gama baci ibrahim din ne ya
shigo yace Ify
. ‘ .Watsi'ya’ yi do Kayan ya ce, "'Yau zan kori
“James a Gidan nan; ba shi, da hankali ne koshi
Mahaukaci ne da zai ciro min wannan kayan?
Ibrahim ya daure fuska,
. Ya ce, -"Ni ne Mahaukacin Ba James ba! K0
nima korata za ka yi mr Sabeer?“ Sabeer ya turo
,baki irin na shagwababbun yaran; masu
kudinnan, ya bata fuska ya ce "Haba Uncle IB, ni
ba zan sa wannan kayan ba gaskiya (Coat) Kwat
din nan ta min nauyi a ciro min kaya'mara nauyi,
ka san qasar nan da zafin tsiya, .yanzu muna fita

zakaji Wani irin ' zafi Ibrahim ya Bata rai ya ce
Asibiti za ‘ kaje kuma aiki za ka jeyi ba wasa k0
yawon shan ‘ iska ba, dole kasa (Decent) kaya
masu mutunci. in ya so in ka dawo ka sa duk irin
kayan da ka ke‘sO. Bari in fada‘ maka, ba za
ka'yi yadda ka so a nan ba (You bave'to behave
your Self) kuma daga yau ba james da John ni ne
zan‘ dinga; maka komai ya Daure fuska ya
nunashi da yatsa ya ce: ’ " "Kanajina?" Kansa a
sunkuye bai ce komai ba. Ibrahim ya dauko kayan
ya ajiye masa ya ce, "Masa ka shirya ka fito,
yanzu ina jiranka zamu je wurin Daddy a . falo
yanajiranmu"
Yana gama fada 'bai sauraresa ba ya fice Sabeer
ya ji hankalinsa ya tashi. Shi fa ba zai iya
wannan takuran‘ba.
Nan da nan ya ji ya quntata, ya tsinCi kansa a
cikin qunci bai taBa ganin Uncle IB haka ba sai
yau Hawaye ya ciko masa ido. A cikin wannan
yanayin ya sa kaya ya shafaya.Mai ' sai‘dai bai
fita ba ya nemi wuri ya zauna ransa Bace, ; bakin
ciki ya ishe shi an sa shi abin da baya so.
Ibrahim kuwa
Ganin halin da yake ciki ya tausaya masa' ‘
saboda har yanzu bai san halin rayuwa ba. Ya
rayu a wata duniya ta daban, waccr ba ta da
alaqa da (Reality) ya matsa gefensa,“ ya kallesa
ya yi' saurin juya fuska alamar fushi ya ke
Ibrahim din ya yi murmushi gami da kama Kunne
ya ce, "Sorry Sabeer, Uncle 1B ya yi laifi a yafe
masa."
Ya. jima yana magiya kafin ya juyo da idonsa
daya ,kada saura Kiris ya zubar da hawaye Yace
ba kaike min tsawa ba, ba ruwana da kai, kuma
sai
na fadawa Sister abin da kamin, zan ce mata
Uncle Ib baya sona yanzu ita kadai ce mai
sona";"Yi haquri Sabeer, Uncle 1b na sonka". "Ba
ka sona". Ya fada cikin _ hasala. ‘ ‘ "Kuma don
ka ga Sister ba ta nan ne shi ya sa kowa‘ ya
tsancni daga kai har Daddy". . ' ' ‘ 'ya jawOsa
jikinsa don ya kula da ya tsinci kansa cikin kewa,
musamman na Yayarsa suka- shaqu, haka ya-

zama masa dole ya lallashesa.
' ” "Sabeer kwantar da hankalinka bawanda ya tsaneka duk muna sonka. ancle ib ba zai sake ma ka .tsawa ba
" . Ya‘dagoshi. '. kayi alqawari"Na yi alkawari ba zan sake ma ka tsawa‘ ba (Now smile)". Hakan ya masa dadi Wanda ya saya saki lallausan murmushi. da ta qarawa fuskarsa kauriji Ibrahim ya~ yi‘dariya, suka mike ya ce an; ‘ "Ka ganka kuwa (Very Handsome)a cikin (Suit)
‘yan Matan Kano za su ‘yi kallo". . Dariya suka yi a tare suka fito zuwa falo; Riqe yake' da 'yar karamar ‘ Jakar saka qananan Takardu a hannunsa._
Sanye yake cikin Kananan 'Kayan Turawa da‘ ake musu lakabi da (Suit), Kansa ba Hula, dan qaramin Sankon da ya shata tsakiyar Kanshi shi zai
tabbatar maka da ‘cewa lallai Dr. Sulaiman rikakken dan Boko ne mai ji da ilimi; ‘
Shigowarsu Falon ya sa ya dago kai ya mai da hankalinsa kan su
‘Ya dan kalli dansa Sabecr cikin tsananin Rauna - ya sakar masa ‘murmushi ya ce "Lallai na gai da‘ Ibrahim, ka yi qokarin taso Saberr karfe Tara na . Safe ‘na ganshi ya shirya tsab, ~yau da alamar Asibiti'
za su yi babban bako"
Ibrahim ya sunkuyar da kai yana murmushi, ya yin da Sabeer ya bata fuska. Cikin muryar qasa qasa ya ce, "(Good ” moming Dad)". Wato ina ina kwana?"
. Yavfada da murmushinsa ya amsa da‘, "(Morning Son). Na ji dadin ganinka kWarai; alamar ’ dai baka son in auto maka 'yar Kauyen mu"..
Sabeer ya Kara bata fuska ya dauki. Coffée din da aka riga aka hada masa yana kokarin kaiwa Baki ya ce "Ni dai an takura min‘kawai, lokacin dana ke Medicine mun yi da kai
da sharadin ba. zaka sani yin aiki dole ba, kace min ilimi kawai ka keso nayi, kana'so in cika

maka burinka in zama Likita,’ duk da bana so sabo da kai na daure na jure wahalarsa na yi ta karatu ba ji ba gani na takura kaina, amma shi ne yanzu ka Bullo mintanan. . Gaskiya Daddy ba ka min adalci ba, ni gaskiya bana son wani wahalar aiki". Kalamansa sun ‘Batawa Mahaifinsa ,rai sun ‘ kuma kufulashi. Ya matsa kusada shi ya ce, "Inbakayi aiki ba. me zakayi?"Ya fada cikin' basala. ' . .koso "Kake ka kare rayuwarka a haka ba zakayi . komai,ba‘ baka da exPRIENCE) baka da wata dabara‘, . inna mutu wa2ai kula Ma da dukiyar? . Ka san yadda zuciyata kemin inna . ganka haka baka komai sai Sakarci? ‘ ' Lokaci ya yi da za ka nitsu kasan Ciwon kanka Sabir ya kufula shima ya hau dokin zuciya ya ce, "Me yasa zan yi aikin wahala in nemi > kudi tunda Mahaifina nada kudi, 'yan uwana na da
Sabo da me zan nemi kudin yanzu ba lokaci bane da zan nemi kudi, lokaci ne da zan more . rayuwata, inji dadi Haka kawai rana tsaka kace zaka shiga tsakanina da jin dadina ka zama , kana so ka doramin nauyin da, ba naWa ba, in ka takura min da maganar aure da a'iki Daddy bazamu‘ _ _,shiryaba,mezakayi? 1‘ 'Mezakayi me zaka iya yi- inji Daddyn ya..." Ya fada ' cikin zafin rai. . . "Bari in fada ma ka, kudin da kake gani ka’ke gadara da su nawa ne ni na nemesu da gumina da
wahalata ba zan bari ka Barnatar dasu a banza ba, idan zaka nutsu ka san me kakeyi, ka nutsi, inba hakaba kuwa za ka sha mamaki." ‘
Wane mamaki zan sha? Nima bana bukatar kudinka, nima ina da nawa kudin, kudin da Mahaifiyata ta mutu ta bar min,
"Sabir
ibrahim. ya kirashi cikin tsawa. Ya yin da ‘ Mahaifinsa ya wanke shi da mari.
Tsananin Bacin rai bakinciki ‘ya hanasa magana. Ya yin da Sabir din ya juya rike da fuska zai tafi Ibrahim! ya tsai da shi. Sabir ya jawo hannunsa zuwa gaban Mahaifin nasa ya ce"Ma za ka bashi haKuri,‘ kar ka kuskura ka. sake yiwa Mahaifinka irin wannan magana in kana so ka gama da

duniyar nan lafiya.'
Ba Mahaifinka. kadai .ba, ka koyi girmama manyanka 'na gaba ' da kai, kuruciya da iskar samartaka' ba. hauka bane, kowa ma ya yi Wannan lokacin ya wuce, meye laifin Mahaifinka don yana nuna maka Kauna,' ya damu da'rayuwarka, yana so kasan ciwon kanka da zafin kanka shi ne zaka dinga yi masa magana cikin wannan harshen?
Ka yi hankali da duniya, maza. ka bawa Mahaifinka hakuri".
Kansa sunkuye idonsa ya yi ja zuciyarsa kamar za ta kashe shi ya bawa Mahaifinsa haquri (Sorry ' Daddy Ya kama kunne. Ba zan sake ba, ka yi hakuri
Daddy ka yafe min» ' Tausayinsa da Kaunarsa ne suka shige shi lokaci guda. , '
Ya dafa kafadarsa yace "Na yafe maka Sabir. Ina' so ka sani Babanka na sonka sosai (Just)' how that i love you) girgiza masa kai ya yi ya fita ya bar falon, Babansa ya bishi da kallo cikin tsananin son dansa da kuma tausaya masa...in akwai abin da ya tsana bai wuce Bacin ran dansa ba. Bayan fitarsa ya mai da kallonsa kan Ibrahim? cikin damuwa ya ce, "Ibrahim na yi kuskure, na yi. " babban kUSkure-~iyayena sun min 'gata amma' ba kamar yadda na yiwa dana ba, son dana yasa nayi . ~ babban kuskure na Bata masa rayuwa, ban san ta yaya zan soma' gyara wannan kuskurenvda na yi ba, soyayyata gareshi ya: Bata tarbiyyarsa. '
_ Ibrahim ya kallesa cikin tausayawa ya ce Kwarai Daddy kayi .kuskure sosai wurin tarbiyyar ' ~ Sabir,' yanzu gyarashi ta hanyar tsawa ko fada ba zai yi gareshi ba, don ba zai taBa fahimta ba
Yace yayi nisa canja tunaninsa zai yi wuya sai anbi Wasu hanyoyi cikin dabara da. kuma masa adddu'a harmu cimmasa
Karka damu Daddy inshal AllahuSabir Zai fahimta' a hankali ya isa garesa ya ,zaunar da shi Daddy ka kwantar da hankalinka, kar ciwon hawan jininka Wanda bayason yawan

tunani ya tashi na san ma dai baka sha magani ba,
nan ya'dauko maganinsa tare'da‘ruwan ya mika masa
_ ya sha sannan ya rakashi daki ya kwantar'da shi yace daddy ka kwantar da ’ka huta kadan kafin ka fita office
, . Sabir ne zaune a karamin falonsa'cikin idonsa jawur kamar zai zubar da hawaye. ' Ya dauko Wayarsa don ya kira ‘wacce ke kwantar masa da hankali. Sister ya kira sunanta'cikin.., muryar kuka. Sister please ki dawo ki zoki daukeni ina: missing dinki' sosai, Daddy baya sona, yanzu quntata min yake son yi. Sister bana son zama a Nigeria ki dawo please, Daddy da Uncle IB fada suke min, basasona. Yi‘ shiru Sabir takatseshi.“Kayi hakuri .ka ga duk hankalina yatashi, wa ya fada maka Daddy baya sonka, .ka san Daddy yafi sonka akan kowa, kuma Sister na sonka, « yanzu- kaifa ba yaro bane, 'Sabir dina‘yanzu babban .
mutum ne
ka manta~ ‘ .alkawarin da kai yiwa Sister dinkane...ka manta kace ‘ min zaka nunaWa Daddy cewa ka girma kaima za-ka ‘ iya daukar nauyin Asibiti da kulada Business dinsa? .me yasa tun daga yanzu ka soma nunamin kasawarka? Sabir dine yanzu, zaka iya komai, ‘ ga Uncle IB yana tare da‘ kai, zai taimaka maka Sabir ka san‘. Sister na sonka sosai, damuwarka 'zai daga min‘ hankali har in kasa mai‘da hankali akan abin da- ya kawoni in yi a nan Sabir ka yi kokari ka daure kayi abin da Daddy keso..kanajina "Eh ina .ji Sister". Ya fada cikin sanyin murya. ‘ ‘
\ . . . zan yi kokarin danne zuciyata , nan gaba. Ki; kula da kanki Sister (Ilové you) ta yi ‘ dariya‘ ta ce ka kula da kanka da Daddy da Uncle IB ‘ zan yi duk abin da kika ce Sister na san Sabir dama ‘ yana jin maganata yanzu zan shiga Asibiti kai ma ka tashi ku shiga Asibiti"“To Sister sai an jima"Nan sukai,sallama ya dago .kai’ gami da - jan:dogon numfashi.
"Kaje ka tabbatar .masa da kaima' kana

kaunarsa, kuma za ka yi duk abin da ya‘ ke so
Bata fUSka yayi” ' Uncle Ib kaima ka san abu mai
wuya ne yin abin da Daddy yaks so".
"Na sani Sabir". Ibrahim ya katseshi. Amma duk
da hakan kaje ka fada mai don kWanciyar
hankalinsa". ‘ Ba‘don yaso ba ya mike yanufi
falon Dadin‘ ya ’sameshi kwance rufe a gadonsa
da hannunsa.
daya... Sabir ya durkusagabansa ya jawo
hannunsa yace am “sorry dadi. Ya fada murya
kasa-kasa."Daddy ka yafe min ba .zan sake ba,
Mahaifin‘ nasa ya yi murmushin'jin dadi, duk“ da
ya san ba har‘ zuci yake fada ba, ganin
kulawarsa garesa ya faranta ransa. Yace"Allah Ya
taimaka Sabir Yau zaka' fara xuwa Asibiti da
Ibrahim, ina fatan za ka ba da himma da kOkari
Wurin duba marasa lafiya Kar kasa wasa k0
sakaci da rayukan al'umma" Ya kau da kai
alamar bai son maganar ya ce"Daddy zan je dai
in fara koyon aiki ba in kai ga duba mara
lafiyar,,,,,
‘ "Sabir abin da ka‘karantane sannan da ka gama
ka yi (Service) wane koyon aiki ya yi ma ka
saura?” .
Ibrahim ne ya shiga tsakani ya ce "Daddy ka san
ya jima da yi, kuma ba (Practics) yake yi ba,
amma dai a hankali zai gane ai muna tare yanzu,
dolensa zai koya sabo da Daddy da kuma gujewa
auren 'YAR KAUYE!" Ya fada cikin" tsokana.
.Sabir ya qufula ya- fisge Key din Mota. a hannun
Ibrahim din ya fita tare da fadin, "Ina mota zan
jiraka‘in 'ka gama da Daddy din". ‘ .
Suka bishi da kallo har ya fice. Daddy ya mai
da kallonsa kan Ibrahim ya ce"Na rasa me ke
damun Sabir, wace irin rayuwa ’ya ke sowa
kansa, yana girma amma yana gudun
(Responsibilities) dinsa Ibrahim don Allah ina so
ka taimaki Sabir ya '‘san me yake yi, ya zama
(Seriousc). Ibrahim ina
.kishi da kyashinka, ina kyashin me yasa Sabir ba
kamarka bane?
Ina kishin me yasa dana ba irinka bane? Me yasa
jinina ba zai zama irin ka ba sai dan riko?

Ibrahim kullum kana cewa na da zuriata don haka
komai zaka iya mama muddin bai sabawa‘
Shari'ah ba, ka‘tuno kalamanka Ibrahim
Dr. Sulaiman ya fada yana kallonsa ido cikin ido.
Ibrahim ya girgiza kai tare‘ da fadin, "Eh Daddy
na tuno komai ban manta ba, banda kalamai
nama harda irin taimakonku da alkhairinku kun
kyautatama rayuwata, kun min duk abin da iyaye
za su yiwa dansu, don haka na yiwa kaina
alkawarin yi muku biyayya da yi muku duk wani
abu da da nagari dan halal zai yiwa iyayensa da
zuciya daya ba cuta ba cutarwa".
Dr. Sulaiman ya yi ajiyar zuciya ya ce, “Na ji
dadin haka. Ibrahim lokaci ya yi da mu ma zaka
mana (F avour) taimako kamar yadda muka yi
maka, a matsayina na uba na yi kuskure nayi
kokarin gyara' kuskurena ,amma hakan ya gagara
sabo da rashin’ fahimtar da ke tsakaninmu da
dana Sabir.
Ibrahim ina so ka mai da sabir kamarka, ina so
Sabir ya zama kaman. Ibrahim (Smart, Intelegent)
mutum mai kwazo, hikima da dabara wanda ya
san ciwon kansa,. za ka iya Ibrahim?"
"zan yi iya dukkan qokarina Daddy k0 ba ka '
fada ba Daddy dama wannan ita ce niyyata na
taimakawa, Sabir ya samu ingantacciyar rayuwa
kuma ya samu tsira har a gobe Kiyama, ba
duniya kadai nake so in taimakawa Sabir ya
samu ba, har da Lahira wanda ita ce Matabbata.
Kafin kai na yima wata wannan alkawari kuma na
yiwa kaina.
Sai dai dama tuni kaine ka shiga tsakanina da
’cika wannan alkawarin sabo da k0 ya ya ba ka
so a batawa Sabir k0 a cusguna masa, kai ka
kyale Sabir ya yi duk abin da ya ke so ya yi duk
abin da ya ga dama, wani bai isa ya hanashi k0
ya sa shi ba, don haka wannan magana da ka
fada min yanzu ya kawo
min sauki sosai, kuma na ji dadin hakan, Sai
ka’bimu‘
da addu'a'da fatan Allah Ya bamu ikon inganta
masa
rayuwa. . Sabir ina jin’sa tamkar‘ Kanina na jini,

ina
matuqar kaunarsa kamar yadda ka ke kaunarsa,
don
haka zan baka karfina da kokarina dari bisa dari ;
wurin inganta masa rayuwa da fatan za ka bani
hadin kai sosai." Dr. Sulaiman ya fada, "Zan baka
dukkan wani hadin kai. Sai dai don Allah ka bishi
a hankali i ‘ kar a Bata masa rai Ibrahim ya yi
murmushi ya Ce, "Daddy sai ka kau da kai". ‘ Dr.
Sulaiman ya ce, "Ba zan iya ganin Sabir cikin
bacin rai ba, sai dai ina ga zan yi tafiya ma‘ sabo
da kar ma in ga wani hali da zai shiga, zan barshi
(In your care) ka kula da shi, duk da zan yi
kewarsa -‘ gara in yi kewarsa da in ganshi cikin
yanayi na. quntata ko na takura." ' ‘ Ibrahim ya
ce"Duk yadda ka yi daidai ne ‘ Daddy. Bari muje
Asibitin".To Allah Ya taimaka, Ya bada'sa'a". ‘
Nan sukai sallama Ibrahim ya fita, ya yin da Dr.
Sulaiman ya kwanta yana tunanin dansa a ransa
da yadda rayuwarsa za ta kasance
sabir
ya fito daga zuriar ALHAJI BALA-RABE
ABUBAKAR Wanda ake_ma Zuri'ar lakani da
BIRNIN GAYU. Ba don arzikinsu kadai ba, har da
shaharar da suka yi da ilimin zamani wanda a
wannan lokaci ba kowa ke yi ba. ' Alhaji Balarabe
Kaka ne ga Mahaifin Sabir Dr. Sulaiman. Ya yi
zamani da' Turawa, kuma ya yi rayuwa ~dasu, ya
yi zama da su a engla ' Asalinsu mutanen Kano
ne. Sunada
' zuriarsu a gauraye suke Hausa-Fulani
Lokacin da Alhaji Balarabe ya dawo daga
ingila ne bayan ya yi karatu kuma ya yi aiki da
su harna tsawon shekaru ya dawo Kano tare da
Matarsa da 'ya'yansa. .
‘ Ya dawo da kudi maSu yawan gaske, ya sayi
makeken Fili ya ' gina gida a Estate guda Wanda
a wannan lokaci ya zamana abin kallo da
‘sha'awa sabo da gini ne irin na kasar waje' da
da yawan mutane akan gidan suke fara ganin ‘irin
wanna“ gidan... Wannan yasa -' akai ma gidan
lakabi' ‘daBIRNIN gAYU saboda irin yanayin'
ginin, da tsarinsa da kyansa da .kuma yadda‘ ~'

suke rayuwarsu irin na Turawa'ne tamkar ba
Hausawaba"
'Tsarin ° rayuwarsu ba irin
. tsarin rayuwar Bahaushe, bane haka dabi'unsu
da ; akidarsu.
A hankali zuri'ar Alhaji Balarabe ta cika" da yara
‘maZa da mata, shi da qannensa da sauran
danginsa sukai ta hayayyafa, Zuri'a ta girma ta
'cika, ta bazu kota ina,rasuwarsa, 'ya'yansa ,
‘ ,suka ci gaba da tafiyar da ,tsarin rayuwars kan
yadda ya‘bari.
Zuri'a ce mai cike da 'yan: Boko, 'yan
Kasuwa, 'yan Siyasa. Ba dai kalar da babu.‘
Hatta
masu (Uniform) akwai a zuriyar, wato manyan
Sojoji; 'yan Sandadasauransu
A hankali Suka dinga fita daga BIRNIN GAYU,
wato gidansu na gado, kowa'ya kama gabansa
yaje yayi irin kalar gininsa da yake so. Amma sai
ya dora BIRNIN GAYUN nan sbd sunan laqani ne
da shaida na zuriyar
Yawancin auren gida suka dinga yi, wato, AURE‘N
DANGI, shi'yasa kusan kowa dan uwan kowanene
azuriyar.
Dr. .Sulaiman 'ya kasance babba a cikin gidansu,
wurin nasu‘ Mahaifin su"uku, ne da- qannensa
duka maza. . "
lyayensu duka sun' rasu; saidai kafin su rasu
kowa‘ ya kama gabansa dukkansu kowanne- da
matarsa suna da yara suna zumunci ta hanyar
ziyartar' juna in Sun .samu‘". lokaci daga
harkokinsu sai dai gaskiya ba wani shaquwa a
tsakanin yaransu, in an yi la'akari irin akidar da
suka tashi da ita ba ruwan koWa da kowa ba mai
shiga harkar wani sai-ta kama, don haka Dr
Sulaiman yake nasa rayuwar daban da
yaransa
Dr. Sulaiman- ya riqe manya-manyam mukaman
Gwamna‘ti a cikin tarihin rayuwarsa. Bayan ya
kammala karatun Digirinsa na uku ne a kasar
Sweesland ya cancanci zama (Doctor sai ya
dawo qasa Nigeria. da zama inda nan ya gina
wani qaton Asibiti da ya yi masa lakabi da sunan

Mahaifiyarsa HAJIYA RABI HOSPITAL sabo da sha'awarsa‘. ga taimakawa qasarsa. IYa riqé mukamin comisionan ilimi na Jiha har tsawon‘ ‘ shekara takwas. Bayan shudewar Gwamnatin ne sabuWar gwamnati ta sake nadashi a matsayin kWamishinan lafiya, inda bai dade ba da wannan mukamin Sunansa ya fito cikin jerin mutanen da ; ‘Fadar Shu‘gaban Kasa ta lissafa a matsayin .Ministoci. ' ' Anan ma dai Gwamnatin Tarayya ta sake : nadashi ;Ministan Ilimi na qasa gaba daya har zuwa qarshen zangin Mulkin na' wannan qarnin
Alhaji Dr. Sulaiman ya mallaki manya~ manyan Kamfanunuwan da ake ji dasu a kasarnan. , ._dr Sulaiman ya yi matan aure uku. ' Matarsa ta farko ita ce Hajiya Sande wacce 'yar uwarsace; Ita ta°fara haifa masa 'ya Mace mai suna ' Farida, wacce Dr. Sulaiman ke‘ ji da ita sosai. Tana da shekara biyar a duniya Allah Ya yi ma ta rasuwa, ba tare da ta sake haihuwa ba. Anan' Dr. Sulaiman ya sake auren Hajiya Amina. .
’wannan karon ba' 'yar— uwarsa bane, 'yar aminin Mahaifinsa ne ya ba shi ita. . . Bayan Hajiya Amina ta haifa yaran ne Zulaiha da Rufaida rikon Fadila ya gagareta, _. rainonta ya Kare ahannun 'yan aiki. '
farida ta kasance cikin kewa da kadaici sabo ba mai janta a jiki' sai Mahaifinta wanda kullum baya nan, harkokin gabansa basa bari ya ‘ kusanta da ita, ’
Zuwan Ibrahim 'gidan ya dan kawo ma ta sassauci. Wanda dane. ga abokin Dr. ‘Sulaiman wanda ya samu hatsarin Mota shi da Matarsa suka- rasu a.take.
A cikin zuriyarsu 'akai' ta kame-kamen mai rikonsa, don haka Dr. Sulaimanya daukoshi ya kawoshi. gidansa ya bawa Hajiya Amina amana don shi bai san‘ma irin rikon da ake yiwa yarsa ba. Farida na da shekara bakwai,‘ Ibrahim nada shekara hudu
Shi ya zame mata abokin ‘wasanta, yana" debe mata kewa, har goyo tana masa, ta bashi abincisuje Ma‘karanta tare, yana rabin Aji

.itakuma tana Aji uku, ya yin da kulawarsu,-kayan sawarsu da kOmai na hanmin masu Aiki. ‘
. Wata Kanwar Dr. Sulaiman neta~zo gidan taga irin halin‘ da suke ciki,"tayi saurin sanar _ shi, sai» suyi ciwo su kwanta ma Hajiya’ Amina .ba ta da labari,‘ ita da yaranta kuwa basuma cika zama qasarba kasar yarda take ta naci da‘ qokarin samun da namiji, amma ikon Allah k0 Ciki bata
- sake yiba.
Bayan Dr. Sulaiman ya samu labarih abin da ke faruwa, ranshi ya baci, ya yi niyyar yin maganin Hajiya Amina, tana qasar waje k0 sai ji ta yi ya yi aure, ya _auro Hajiya Fatima 'yar hamshakin mai kudi Bafillatana"fara sol, kyakkyawa mai ilimi', ga Wayewa
_Riqon 'Farida da 'Ibrahim ya"—koma hannunta ta rungumesu. ko— hannu ~biyu kamar yayanta So, “Kauna' da — Kulawa da 'Gata ba Wanda ba ta‘ nuna musU' har suka manta da rayuwar ‘ kadaicinsu.
Hakan ya jefa soyayyarta ‘a'Zuciyar Dr: Sulaiman sosai. Suka yi wata irin shakuwa.
Dr Sulaiman ganin ya» gama .sauka a Mukamansa, kuma ya tara dukiya .mai-dumbin: '_ yawa, ga kuma._ manyan - Kamfanoninsa‘ da Asibitinsa na aiki yadda ya kamata, hakan ya tattara Yaransa da Matansa Hajiya. Fatima da Kasuwancinsa ya ‘koma kasar Canada, ya yin da‘ ya bar Hajiya Amina a Nigeria da Yaranta.
shi kansa Dr. Sulaiman sai dai -wayewar ta ratsashi sosai, haka bokon ya shigesa sosai akan addini. Tana burin gyara rayuwar gidan ' Wannan magana na Hajiya Fatima» ya shiga kwakwalwarSu sosai, musamman Farida da takeda'wayo so Sai dai burin Hajiya Fatima bai kai ga cika
ba allabYa karBi ranta ta hanyar haihuwar Sabir Kwarai - Fatima da Ibrahim sunyi kuka"
Sun yi rashin Uwa' mai .sonsu da qaunarsu Haka suka ’shiga’halin MARAICi da shi ’" da yaransab dukda Yana da‘ wata-Matar, amman
" jinta yake ba kamar Hajiya Fatima,ba

‘ Rainon Sabir 'ya koma hannun‘ farida
qanuwar Dr. Sulaiman, musamman ya
daukota-‘ta dawo Canada’sabo da rainon Sabir,
don kuwa bata da aure, tana gida ta samu saBani
da Mijinta
har auren ya mutu. Tare suka zauna' su Farida
da
shared a profile .
birnin gayu
chapter4
Ibrahim. suka yi rainon sabir. Yana da shekara
uku a duniya Auntynsa ta yi aure.) ' , Farida da
Ibrahim da masu aiki da shi kansa Dr. Suleiman
din sun: sukaita rainon Sabir ya saba dasu sosai
ya shaqu da Farida sosai, komai Sister: haka ya
dauketa tamkar uwarsa, bashi da magana da‘ ya
wuce na Sister.
‘Sun dauki son duniya sun daura masa ,
musamman Dr. Sulaiman yadda yake Bata Sabir
abin ba,a magana duk abin da yake so shi zai'yi,
ba a sa shi ba a hanashi. Haka ya tashi sakale,
gata ya yi masa yawa. a wajen
Dr. Sulaiman tamkar bashi da wasu ‘ ‘ya'yan. duk
da yana kaunarsu amma soyayyar Sabir daban
take a zuciyarsa da ransa, don haka duk abin da
Sabir keso ya zauna ba mai hanashi.
Farida abin na damunta, duk yadda ta yi kokarin
gyara Sabir sai Daddy ya rushe, tana matuqar son
sabir; haka nan bata mance kaunar da
Mahaifiyatsa ta nuna musu, sannan nasiharta
da burinta yana nan a tsakar kanta.
Farida, Ibrahim, Sabir tare suka tashi, suka girma
cikin so da shakuwa, ya yin da farida ke musu
komai a matsayinta na babbar yayarsu.
Sun taso kuma sun girma a Canada, anan suka
yi, karatunsu, daga Farida har; Ibrahim Medicine
suka karanta, don dukkansu wannan' ne burinsu.
' ‘
Haka- tana da burin ta dawo gida Nigeria ta yi
aiki a'Asibitin.‘ Mahaifinta.
Kullum tana; cikin .katu bin.cike akan Mata; ta
kware akan sanin ciwon Mata da matsalolinsu
Ya yin da’ 'Shi kuma Ibrahim ya karanci bangaren

fata bayan ya zama cikakken ,Likita ya Sake kOmawa karatu na, ‘ shekara uku don kwarewa akan sanin ciwon Fata
Shi kuwa Sabir, bayan ya gama Secondary - School dinsa da yaki karatun ma sabo da duk-abin da yake'so a duniya yana da shi, kuma zai samu sabir
Mutum ne Wanda ya ki jinin wahala k0 kadan, baya'son abinda zai Wahalar da shi‘. '
Cikin‘dabara 'Farida da Mahaidinsa suka sa ya fara karatu Da da farko Business‘ya soya'; karanta amma ; sai ' Farida‘ tace ‘masma" 'yana, da kwakwalwa ‘mai zai hana ya Zama Likita kamar:
yadda ita da Ibrahim suka karanta (Medicine) sai , su tari su riRe Asibitin Mahaifinsu. ,ta Kara nuna masa cewa burin Mahaifiyarsa ce hakan Sabir ya amince ya ; ‘ fara karatunsa na Medicine " a University of Albena da ke Canada. ’ ; ' Bayan gama karatunsa ne‘ Mahaifinsa‘ ya ~ shirya musu tafiya hutu tare dan-Shi, suka tafi yawon bude ido qasashe daban-daban suka yi Umarah a Saudi sannan suka Wuce Nigeria» Wannan karon shi ne karo na farko da Sabir ya zo Nigeria yaga 'yan uwansa da danginsa na gun Uwa da Uba. Basuf1 Sati ba ya daga musu hankali
suka koma Canada.
Zulaiha da Rufaida na tare da Mahaifiyarsu a Nigeria haka nan duk sun gama ‘ ‘karatunsu‘ suna aiki a Kamfanin Mahaifinsa
, kafin su yi aure.
dr Sulaiman ya kasance tsakanin Canada 'da Nigeria. _ Farida da Ibrahim na son dawowa Nigeria amma Mahaifinsu ya hanasu sabo da kawai su zauna da Sabir a Canada, .don ya ce shi ba zai dawo Nigeria ba, rayuwar da- Sabir ke yi a Canada yana mugun dagawa Farida hankali. Ta shiga‘ damuwa sosai saboda ‘ko ta hanashi bazai hanubA, haka Daddy ya hanasu’ takura masa k0 su yi mishi abin da’baya so. .
Sabir kyakkyawan Matashi ne, dogo fari tas sakalalle dan masu naira mai ji ‘da. ilimi 'da

kuma wayewa, wanda gata ta masa yawa, '
Yana yadda yake so da naira, ya shiga Mota mai tsadar da ya ga dama, ya sa mai tsada,' ya taka mai tsada, ba shi da wata rayuwa da ya. wuce na jin dadi da hOlewa.
Addini dai bai damesa ba, yana dai Sallah, lokacin da ya ga dama, haka 'yan mata kuwa canjasu yake'kamar riga.
' Duk wata 'yar mai kudi da ke ji da kanta wurin kyau da ilimi da aji irin wanda iyayensu , ke'turosu karatu daga Nigeria; ba wacce Sabir bai yi yayinta ya kyaleta ba. Tsananin suyi wata biyu zuwa uku da Mace ya yar da ita.
Haka ma sauran Matan fararen Fata, ba kalar Mace mai kyau da Sabir bai yi yayinta ya zubar ba.
Hat gobe 'yan mata binsa-suke, yana musu . yadda ya ga dama. A cewarsa shi yanzu ya gaji da 'yan mata . wai kyawawa sun kare, shi k0 mutum ne mai son abu mai kyau, komai nasa a rayuwa mai kyau da sha'awa yake so. _ Ya yin da yaki jinin mummunan abu, k0
da kuwa dabba ne k0 Sutura.
' A fili ya ke nuna kyamar mummunan abu.
Wani lokacin in ya ga mummunan dabba bayan kyamarsu ma'har da tsoronsu yake
' Akwai ran da yaje Asibitin da su Farida da Ibrahim ke aiki suka samu an kawo hatsari ba kyan gani, mutumin kansa ya kumbura " sosai, gaba daya halittarsa ya canja'. Koda Sabir - ya ganshi, ' ya yi tsananin firgita, sai da ya suma sabo da firgita. a
Haka ranar yakwana a tsorace yayi ba bacci haka ya qankame Ibrahim a jikinsa ya' kwana
Farida na masa addu'a. Da' taimakon Allurar Bacci ya'samu bacci da kyar
saida ya kusa sati kafin ya dawo daidai tun kuwa daga wannan ranan bai sake zuwa Asibitinba ko da wasa ba
. .' 'Wannan rayuwa ta'Sabir yana mummunan ,daga hankalin Farida. Sam bai san meye rayuwa ba
, 'Su tsoratar da Sabir ga ' mutuwa. ya san

kwanciyar Kabari, su inganta‘
. masa' rayuwarsa ta duniya da lahira _tun kafin
'~ ‘lokaci ya kure musu gaba daya. ‘
_ Wannan ne yasa ‘farida ta ‘fuskanci’"
Mahaifnsu ta sanar da‘ shi illar rayuwar da ya '
kyale Sabir yana yi, dole ya san na yi da amanar,
da Allah Ya ba shi na 'ya'yansa. ‘
Farida ta 'yi iya qokarinta sosai nason ganin jawo
hankalin Daddy ya fahimci ‘ halin da 'Sabir yake
ciki- ammai sai ya kasa ganewa har’ zuwa
lokacin da suka dawo Nigeria don yin auren
Farida da kannenta Rufaida-da Zulaihat.
Da‘kansa ya lura da rayuwar da Sabir yake ba
abin da ya tayar masa 'da hankali kamar yadda
ya ga Sabir yana shan giya kamar ruwa
.Haka nan Sabir sosai akan abin da ya ke so in
an hanashi
Ranar ‘da Daddy ya kamashi da giya ya hanashi
sha rana ta farko ke nan da ya fara hana
shi wani abu a rayuwa.
Ranar ko ya ga rigimar. Sabir, nan da nan. ya
birkice musu, 'ga Sabir da wani irin fishi da
zuciya mara kyau. '
' ‘Sai da ya dagawa kowa hankali a ranar. ' ‘ Tun
daga lokacin hankalin Baban nasu ya fara
tashi sabo da ‘yadda ’ya ga Sabir na shan
giya;ne kuma ya saba da' ita haka to zata iya
taba lafiyarsa~
' 'innalilahi' Wa inna ilaillinaju ’un Abin' da Daddy
ke fada kenan cikin tashin hankali. '
Farida ta matso garesa tare da Ibrahim 'ta ‘ ce,
"Daddy abin» da nake kokarin- ka gane ke nan
tun-tuni ka kasa. ‘
Dubi~ irin rayuwar da Sabir yake, wannan ‘ kadan
ma ka gani, mu da ke rayuwa da shi-mu muke
ganin rayuwarsa. ..
Daddy kai iyayenka sun maka yadda kai ina
Sabir'kuwa? Na yarda suna da wani irin ' akida,
amma ba‘ su hallaka ma ka rayuwa ba, don da
sun maka haka da yau ba ka kai matsayin da
kake ba. . ' '
- ' Kai mutum ne da ya san'me yake, mai ilimi,
hikima da basira. “

Kowa ya san kai dattijon kirki ne, kowa- ya San kai na Kwarai ne.
Daddy‘ ka dubi Sabir, kana ganin inya girma ya kai shekarunka ba za a dinga yi mishi kallon’ dattijon banza‘ ba?‘
Daddy wannan soyayyar da ka ke yiwa Sabir ta hallakar da shi, ta kashe masa rayuwa. - Daddy duba da sauran yaran Abokanka wandanda suke sa'annin juna da Sabir, dubi yanayin hankalinsu da nutsuwarsu, sunanjin maganan iyayensu‘, suna ginnama na gaba dasu ‘ ' Daddy ~ kana Mahaifin Sabir ammn yanzu baka isa ka sa shi ko‘ ka hanashi k0 ka tsawatar masa ba, sabo da tun yana yaro baka mai haka ba sai yanzu Daddy wannan' rayuwar ba shi ne wacce Mahaifiyarsa taso masanba da shi“ da mu. .duka, haddakai. Tana son nuna mana kyakkyawar rayuwa don! muci ribar duniya da lahira‘. . Ina jin takaicin rashin cika burinta sabo da baka bamu dama‘ ba, duk da na yi aure zanci gaba da rikon Sabir kamar dana,ne ,Mijina ba shi da matsala, ka san zai iya yiwa Sabir komai; zamu yi Kokarin gyara masa rayuwa "in har ka‘
amince".
. Hawayen nadama ya zubowa Daddy yace‘ "Tabbas na' tafka kuskure" babba, ’ zan-
yi"kokarin gyarawa. ‘ Ban san na yiwa Sabir illah ba; sai da._, na gani da idona Tabbas sa'anninsa sun masa, fintinkau A wurare da dama, duk da ya fisu da komai, ba abin da ya rasa tun daga kan dukiya, .asali, gata, kyan halitta." . Sai' dai Sabir yana sakarci, 'a gaba ba :zai' ‘ iya aiki ba balle kula da dukiyarsa, ga gadon da Mahaifiyarsa ta bar masa mai yawa, gashi dan' gadona dukda bamu san gawar far ba, amma - inna mutu na barsa duk da dukiyar nan haka komai .zai kare ba shi da dabara da hikimar zaman rayuwa. Asibitin ma ba‘ aikin zai iya yi ba, ba abin da ya sani sai dai kashe kudi Yanzu sai‘ a iya cutarsa‘ Sabir ko kansa‘ba zai iya karewa
subhanallahi Na cuci kaina, na cuci dana. idan ban baku Sabir ba, ba'zai iya kula da kansa ba
Nan Daddy ya fashe da kukan baqin ciki da Bacin

rai. Tsananin bacin rai da tashin hankali sai da yasa hawanjininsa ya hau sosai.
Da'kyar suka samu Sukai controll din Bp' dinsa, ya yin da suka yi ta kwantar masa da hankali cikin hikima da dabara, don in sun ce za su masa ta. "tsiya zai yi wuya su cimma manufarsu akansa: hummm sabir kenan
Sati biyu da biki 'kowacce ta tafi gidanta Rufaida America ta wuce da'Mijinta, sai' .- dai Gidanta na Kaduna sunje honey moon ne Zulaiha kuwa tana Abuja. ne'Farida kuma Canada suka koma don daman mijinta a can yake DA zama Likitane shima, tare
Yadda Sabir ya tada masu hankali akan su koma Canada ne ya tabbatar musu da cewa ba qaramar wuya za su sha ba idansun zo dawowa Nigeria ' gaba daya. _
Sai dai za su koma ta shirya masa. Sun sallama da Daddy, sun barshi cikin tashin' hankali da tunanin rayuwar Sabeer da hanyar da ' zai bi ta inda zai fara.
Bayan zaman Nigeria ba abin da Sabeer ya fi tsana irin maganar Aure, a takurashi ace ya zauna da Mace har abada. Sannan Macen ma ace. 'yar nigeri'a wacce ba ta waye ba, irin 'yan garin su.
'Don haka Mahaifinsa ya samo. hanyar da zai bi ya sa shi yin abin da ya keso, k0 kuma ya masa Auren da baya so, ya kuma sa shi dawowa nan da zama.
bAYAN KOMAWAR Su DA Wata
_ biyu Farida da Ibrahim suka yi iya kokarinsu amma Sabeer fa ya yi nisa don
Daddy din shi kadai zai iya lankwasa shi, ita kam tana da rauni daga ya soma mata shagwaBa da kuka sai tausayinsa ya kamata, haka za ta nemi wuri ta yi ta kuka ita daya. '
Ibrahim shi bai da ta cewa sabo da dama can bai isa yayiwa Sabeer wani abin ba na tsawatarwa sai ya hadashi da Daddy ya yi ta masa fada. - "
' Sai dai damuwar. Farida da tashin hankalinta na damunshi, ganinta cikin damuwa da qunci.
Sabo da Kaninta na daga masa hankali, don shi a

duniya ba shi da wacce ta fi Farida, ita ce
komansa a rayuwa, don haka zai iya yin
komai don ganin ya taimaka ma ta, don haka ya
yiwa Daddy Waya ya ce in yana so su gyara
Sabeer dole sai ya dawo Gida Nigeria kuma ba a
gaban Yaya Farida ba, don kuwa tana da rauni
Daddy ya ce, "Dama shima da na sa shirin Ya yi
tunanin haka don haka zai 20 ya ce su Shirya zai
taho da Sabeer. '
.Lokacin da Daddy ya 20 tafiya 'da Subir suka yi
ta tsiya ya ce ba zai tafiba.
Daddy k0 ya Bata rai ya ce, dole sai ya raba’sa
da Kasar nan da Abokansa na kasar ; da komai
nasa da ya shafi kasar, sabon rayuya ' zai zo ya
fara a Nigeria, idan kuma yana son' ‘ 'yancinsa
dole sai ya yi yanda ya ke so, k0 ya masa aure
ya kuma ajiyesa a Nigeria. ~
Sabeer hankalinsa ya tashi ya gudu ya Buya a
bayan Farida yana kuka
“Sister ki taimakeni ni ba zan iya tafia ba
keba....Sister ba zan zauna da Daddy ba! Ni da ke
zan zauna, Sister ke ne Mamana da komi na...ni
dai ki 20 mu tafi ko ki-cewa Daddy ya, : barmi in
zauna dake
Farida ta fashe da kuka ta rungumeshi,
tausayinsa ya kamata. ' "Sabeer ka yi hakuri ka
bi Daddy nima zan zo‘akwai aikin da zan gama in
zo in
‘ "Sister ba kya sona ne yanzu? Kinfi-son,“ aikin
ki da Mijinki? Ba kya son danki? . Sister kin ce fa
ni danki .ne shi ne za ki‘ rabu da ni, za ki hadani
da Daddy...Sisterr ni banason Daddy, ni wurinki
zan zauna". ' ' Kuka ta ke xuciyarta na rawa ta
tureshi cikin fada ta ce“Ya” zama dole ka tafi
Saber, idan ina sonka ba zan barka a nan ka
karasa
hallaka rayuwarka ba, _ dole ka ‘zama mutumin ,
kwarai, ka san Ciwon’ kanka, in kana so mu
shirya dole ka je ka gyara rayuwarka, in ba haka
ba ko magana ba zan sake ma kaba...in kana so
in zauna da kai ya Zama dole ka tabbatarwa da-
daddy za ka ‘gyara za ka koyi aiki, zaka rike
Asibiti, za ka zama (responsible) mutum mai ;

nutsuwa da sanin ciwon kansa. ' _ ' Kar ka sake'
min magana in ka san. ba za kayi hakanba". Zan
yi Sister' 'Ya' fada 'cikin sanyin murya da tausayi
yana kuka irin na sakalci. "Zan yi in dai za ki
kulani, za ki barni inzo zan yi duk yadda Daddy
'ya
ce...amma.ki fada masa kar ya min aure kuma
zai barni in dawo wurinki Nan ya juya ya tafi
Mota yana kuka, ga' fuskarnan jawur,yaune
rananr farko DA sabir Yayikukandabai taba
irinsaba Farida tayi ciki da gudu ta fada kan gado
tana kuka Ibrahim yabi bayanta ""Kiyi haquri
yayata dole sai kinyu haquri "Ibrahim Sabeer zai .
tafi ya bar ni,' zai je ya rayu inda bana'nan...Ibra
him don Allah ka bi su, ban san wane hannu
Daddy zai sa Sabeer ba, ban yarda; da Matarsa
ba, ban yarda da wannan 'Momin ba...Ibrahim'
kai kadai ne zai .kula min da Sabee'r.
ibrahim na baka amanar Sabeer, ka sashi a hanya
ka nuna masa komai. a hankali, na san za ka
iya".
Ya kalleta cikin kulawa 'ya ce, "Yayata ke ma
kina buqatar 'a kula da ke, kina cikin wani hali,
ya za,_a yi ki zauna ke kadai da ciwo' ki Boyewa
Mijinki bai sani-ba?
Dukda dauriya da jarumta irin'na' Ibrahim sai'
da'ya yi hawaye. '
"Yayata kin san ina tare da ke a cikin kowanne
irin hali k0 wuya k0 dadi k0 ciwo k0 lafiya;
' Kin" "San KAUNARMU "da SHAKUWARMU tun
muna Kanana ba abu ne mai sauqi rabuwarmu
lokaci guda ba. Yayata me zai hana ki biyo mu
nigeria?" Ta yi dariyar yake. "Kar ka damu
qanina, Zan iya kula da kaina, kuma bana son
kowa ya fahimci halin da na ke ciki.
Don Allah qanina ka rike min'sirrin nan, ,' sannan
kayi kokarin cika min burina na ganinSabeer ya
nutsu yayi hankali
Ya kau da kai yana share kwallah yace"Na miki
alkawari..." Harya soma tafiya ta ce "Kanina kai
ma ka kula da kanka, duk da kai babba ne mai
.- hankali, wani lokacin ka cika yarinta, ba ka son
cin Abinci, wasa kake da lafiyarka ka fadamin min

dukkan damuwarka kamar yadda yanzu nima make fada maka naws
Ya juyo yana mata murmushin Karfin hali
Bayan sun iso’ Nigeria yaqi sabawa da Momi da Sauran jama'ar Gidan, wasu 'yan uwan Momi‘,"'Wasu na Daddy ‘ . Haka nan bai saba da Kano ba, ba Abokai, ba 'yan Mata ba Giya',ba fita Yawon gun Shakatawa
Wannan yasa' Sabeer, kewada kunci har ya fara ramewa Ganin haka'Ibrahim‘ yaja shi a jiki Haka nan yana zuwa da shi ‘duk inda zaije, daga‘ Kamfanin Daddy har Asibiti. Sai 'dai fa ba .kullum yake zuwaba , Haka nan Asibitin bai shiga duk wai bai son ganin ciwon da
zai daga masa hankal‘i.
, Da haka‘ Sabeer ya fara sabawa da Garin Kano har ya samu Abokai biyu Wanda suke 'ya'yan Abokin Daddy ne; Wanda Daddy din ya yarda da daabi'unsu.
Bangaren Alhaji kuwa ma su dafa masa Abinci da kula da sha’aninsa na Gida ba ma ‘yan qasarnanbane.' Sai dai Abinci ba- irin kalar da ba su iya‘ ba, musamman ya Ware su don‘kula da Sabeer da‘ Abincin da ya ke 'so‘ Hajiya amina kuwa 'neman Kudinta shi tafi bawa Karfi, don haka ba' ta cika sa wa Sabeer ido ba, ba Ya gabanta Dr. Sulaiman din ma basu,cika haduwa ba, duk da suna'Gida‘daya, 'kuma a Mata da Miji...amma a wuni baif1 su hadu sau daya zuwa 'biyu ba, da Dare wurin Bacci ‘sai kuma satiya‘ business ‘ kawai, tasa a gaba sai harka da ' Kawayenta manyan Kusoshin Gwamnati ko Matan ma su Kasar. Ba ta wasa da harkan Kudi. ‘ '
Lokacin da ta dauko 'yan uwanta suka mata wata Cuta na Miliyoyin,kudi ya sa ta koresu ta soma neman bare wacce ba ta waye be don kula ma ta da lissafin Kudi da kayan da suka shiga suka fita, da kuma yi ma ta (Transfaring) Kudi daga wannan Banki zuwa wannan...sannan da kula ma ta da Bangarenta.
. Wannan ya sa ta sa Tabawa ta nemo ma ta Deeda, kuma ta sa aka bata (Special Trainining) na Wata uku kafin ta dawo daga tafiya, wanda

shima tafiyar na wani Kasuwancin ne tare da wasu Kawayenta da kuma Kanwarta daya.
Sannan tana son zuwa ta ga yayarta
Gidan Dr. Sulaiman BIRNIN GAYU Gida ne da kowa ke rayuwarsa, ba ruwan kowa da kowa.
Yanzu ne ma Dr. Sulaiman ke kokarin jan' Sabeer a jiki, tare suke cin Abinci.
Haka nan sukan yi Hira kadan ya bincika me ya ke ciki sannan ya barsa da Ibrahim Ya tafi harkokinsa. '
To yanzu dai Dr. Sulaiman ya yi. tafiya ya bar Sabeer hannun Ibrahim da kuma sharadi wa sabeer cewa in ya dawo ya samu bai canja ba to ba shi. ba komawa Canada, kuma sai ya masa' aure Macen da ba ya so.Kudl da komai hannim Ibrahim Suke ya ce bai yarda Sabeer ya yi komai ba tare da Da wannan sukai sallama, Sabeer na Mita' an takura rayuwarsa, bai 'san ta yadda zai fara; zuwa Kamfanin Daddy da sunan Aiki ba. - ,
.. 'Asibiti kuwa shi ' gaskiya tsoron wasu Ciwon ya ke. 'in'ya' tuno da Aure da kuma zaman Nigeria da za a 'sa' shi sai ya tashi, wani lokaci ma dai tsabar jin dadi 'har fasheWa ya ke da 'kuka in ya yi, ya yi ya kasa qulla komai a Kamfanin da Asibitin sai ya fashe da kuka.
Tabbas Ibrahim na fama da- Sabeer, ' ya rasa ta yanda zai Bullo masa saboda zuciyarsa da rashin-hakuri. '
Haka' nan duk girman Mutum sai ya ci 'masa Mutunci, ba shi da hakurin koyon Aiki. Haka ba shi da juriyar zama a (Office),kullum yana cikin yawo a Gari da Mata, k0 kallo k0 yin Games k0 ya ta buga Snooker Yana matukar .son (Sport) don haka kullum yana cikin Wasanni, ya yin da ya ,faki Idon Ibrahim ya sha Giyarsa amma a boye. '
Duk inda Ibrahim ya bi da shi sai ya zulle a hakan dai ya ke fama da shi, wataran yayi nasaran tafia da shi aiki, wani lokaci kuwa tafia; ya keya hakura ya kyaleshi. ' ' Haka nan bai son fadawa Farida 'ya daga mata hankali, haka ba komai ya ke fadawa Daddy ba, ya dage da Addu'a da kokarin neman hanyar da zai bullo masa. '
1 *'* *'* *'* ,

' Deeda ce zaune cikin daki ta baza ’ Takardu alamara ta yi nisa sosai. cikin karatunta, duk da yanzu hutu suke
ba ta da hutu, Karatu ta ke ha wasa, wanda in sun koma Hutu za ta shiga aji biyar na Sakandari kenan. ; » -; ‘ , ' _
Sai " dai ta san ba tabbas din‘ komawa don kuwa ta gama Computer Classes dinta, ta‘ samu (Certificate) kowanne lokaci za ta iya tafiya Gidan aikinta in Hajiyar ta dawo daga tafiya. . -
‘ * "Deeda!
" ~ Kakarta ta kwala ma ta kira. Ta'miqe
ta
fita ta sameta zaune, ta sa Kwallan Fura da Nona ’a gaba tana jimami.
'. Deedan ta kalleta.
"Lafiya Inna?’
"'Ke dai bari 'yar nan, kin ga masu Shagon nan har yanzu ba su zo sun dauki Furan nan ba, ga shi na dama da None na hada komai saura su dauka su zuba a Robobi su sa a‘friji, amma kin ga har yanzu shiru, kar ya kumbura ya yi TSami ya lalace mu yi Asaransa. K0 za ki dauka ki kai musu?"
“Kai Inna' in suna so za su zo su dauka, ana sayar musu cikin saukin ma sai an bi-su dashi Shago?" ' ’
"Inna ta hasala. . '
"Inzaki daukakikaiki dauka,inbazaki ba kuma sai in yafa Gyalena in kai musu. Ba mu ke neman Ciniki ba?" a
"A'a Inna. me ya yi zafi? Barn in dauko' Hijabi inkai musu, Amma gaskiya ki raba min shi biyu, nayi sawu biyu donba zan iya daukan wannan qaton Kwallar"ba "Na ji bari in raba miki dauko Hijabin"Nan Innan ta raba "mata,’ ia’kuwa ta dauko Hijabinta ta sa ta dauki kwanon Furan ta Tafiya take‘tana Mita a‘zuciyarta saboda bataso zuwa Shagon ba, don kullum cikeyake dajuma'a musamman Samari Matasa, shi yasa.
.'Bata ankare ba saiji tayi tayi karoda mutum, Kwanon Furar ya fadi,‘ ya ", Zuciyarta ya tsinke ta soma tunanin ya za ta kare da Kakarta? Wani

ihu taji ansa daya'firgitata tadaga kai ta kallesa 77 "Lafiya Malam Me ya faru? Ya yi-mata wani mugun kallo mai cike da tsana da Bacin rai da kuma jin ,haushi, idonsa ' sukayi ja suka ciko da hawayc. Ya ce"Ke Mahaukaciyar inane so kike ki karya min Kafa, kuma kin Bata min Jiki?"Yayi kwafa"Wawiya kawai Shashasha!!!"Kai Malam Saurara Ni ba shashasha ba‘ ce ni na hanaka kallon gabanka? Yanzu ban da tsabar wauta don dan wannan kwanon ya fadi a
Kafarka‘shi ne za ka yi wani ihu?" Ta dan kwantar da kai ta leka fuskarsa‘ta‘” zaro ido "Ba dai Kuka za kai ba, ~sai ka ce wani karamin Yaro? Amma ka ji kunya,‘ nima da ka min Asaran Fura ban Ce zan yi Kuka ba sai kai? Dadi ya yi ma ka yawa". ' . ' Nan ta sa hannu ta dauki “Kwanonta ta juya. Haushi ya cikashi, ya finciko Hijabinta. - "Kin yi min laifi maimakon ki ban hakuri za ki tsaya kina min Surutun banza Dama haka ku ke Talakawan nan 'yan rainin Wayo.. ' Yanzunnan ki san yadda za'ki yi ki goge min wannan Kazantar da ki ka sa min a jikina". Ta harareshi. "Ba za,a gogen ba sai ka yi abin da za ka
. Ta juya ta fara tafiya. Ya bita ya sha gabanta. bai saurara’ ba .ya‘ sa hannu ya fisge Hijabinta. Tsananin mamaki yasa ta bude Baki . ta kasa magana, . Hmm! Sabeer dai dama shi «ya‘ kware ’ Wajen yiwa 'yan Mata rashin mutunci, masu
Kudi da Aji ma balle Deeda da ya ke ganinta 'yar Kauye, kuma Talaka. _ 1
~ , Nan ya sa Hij'abin ya goge inda Furan ya bata masa Jiki, ya yar da Hijab din ya sa kafarsa da ke dauke da manya—manyan Takalma ya murkushe shi. Kallonsa ta ke zuciyarta kamar Wuta.
. ‘ Ya nunata da dan yatsa. Nan gaba kafin ki sake ma wani rashin kunya ki tsaya ki kalli kanki, ki kallesa, inkin ga irina ne to ki yi saurin shafawa kanki Ruwa don kuwa zan iya murtsike ki a maimakon wannan kaza'min Hijabin na ki..."
* Nan ya wuce ya nufi Mota ya yin da‘ Uncle IB

da Abokansa Nura da Salim suka tsaya suna kallonsu, 'haka jama'ar da ke wurin kowa ya tsaya yana kallon su. Ran Deeda ya“ yi mummunan Baci. Ba Hijabinta daya: murtsike a kasa ne ya Bata mata; rai ba, kamar yadda a,a yaye‘ ‘ mata' Hijabin DA yayi a' bainar jama'a da kuma kalamansa 'marasa dadi su suka fusatata.
' ‘Ta yi saurin shan gabansa hannunta riKe da Kwanon Furan nan. , ,."Kai marar mutunci Wanda bai san darajar Mutane ba. ‘ ' _ Juyowa ya yi zai kuma zazzaga mata rashin mutunci.
amman Kafin ya kai ga yin. ,wani abu k0 'cewa wani abu ta Wanke masa fuska _da jikinsa‘gaba saya 'da wannan Nonon da Furan- da yai‘ saura'a Kwanon, ta kuma Kara wurginsa da Kwanon
Ta yi Tsaki ta sunkuya'ta dauki Hijabinta ta wuce ta barshi Baki bude, tsananin mamaki da kaduwa da bakinciki yasa ya kasa-magana. Ya yin da jama'ar gurin kowa ya mayarda hankali yana kallonsa. '
Abokansa ko bubu wanda ya ko motsa daga inda yake
Ya yin da Ibrahim ya harde hannu a kirji yana murmushi yana. kallon Sabeer kamar zai tashi sama don azabar zuciya da'fishi
- Sabeer ya diga 'waige-waige bai ganta ba, bai ga inda ta shiga ba, ya yin da ya huce a kan
ya book dinne KO canjane baga bakwa comment ah shared a profile .
birnin gayu
chapter5
jama‘ar wurin 'da suka' taru_ suna kallonsa. Ya dinga Zaginsu da Turanci. " ' Wasu ko a jikinsu,"don ba suma fahimci me yake fadi ba, Ibrahim ne ya jashi suka shiga Mota da idonsa jawur kamar zai zub da hawaye. Ibrahim ya kalleSa’ ya ce, "Sabeer a dinga haquri, ba ,kullum“ za ka 'sami yadda'kake 'soba, “ Dama tsautsayine ya sa Motarmu' tsayaWa anan ya kalli Nura. ""‘tuqa mana mu ‘lallaba mu koma Gida, fitar dai tayautafasu
Sabeer ya harari Ibrahim cikin fishi‘ ’yacé "Tunda.

bayanta kake bi da alama ka' ji dadin abin da ya faru dani in kaje ka hada party Yayi wannan' murmushin nasa ya ce "Sabeer ke nan.
Tabbas 'naji dadin abin ba don". komai ba sabo da darasi ne na farko ga
rayuwarka.
Sai dai ba zanyi Party ba sabo da ina da abin yi da yawa , kaine keda lokacin Party ba ni ba". '
Sabeer ya , qara qulewa yaji- tamkar ya kamashi ,da duka, sai dai ba 'zai iya hakan .ba sabo da matsayinsa' da girmansa da'yake da shi
Bai sake furta: komai ba, sai dai kallo daya za kayi masa kasan yana cikin ,bacin rai da zafin zuciya.
Ganin haka yasa' "Ibrahim . ya soma lallashinsa amma bai kulashi ba.. '
" Haka su Nura k0 kallo ba su ishe shi ba.
Haka .suka haqura suka Kyaleshi, har suka isa Gida, 'ya fita ya nufi Dakinsa k0 Marfin Motar bairufe ba.
Ibrahim ya bi shi da. Ido yana tunanin ta ina zai shawo kansa.' Fatansa dai kar ya yiwa sister Waya ya daga mata hankali
*.*i ',*.*. _*.* -
_ DEEDATA ISA gida Itama rai bace Inna mai fura tace Deeda lafiya! Magana fa nake kinaji , meya faru na ganki haka, na ga kwanon furan a Bace?"
' "Inna don Allah ni ki kyaleni". Tayi Tsaki. "
' "Daman haka 'yan BIRNIN su ke wulakanta Talaka k0 mara karfi shi ne wayewa?"
' "Ke Deeda ba dai fada ki ka yi. da 'wadanda suka fi qarfinki ba k0? ' ,Kin ga fa nan Birni ne ki rufa mana asiri kar ki musu halin da ki ke mana a Kauye muna lallaba rayuwannu ki jawo mam masifa. ' ' Ni kam ki fito ki kai min daya Furan..." , "Ni fa Inna ki kyalemi, bazan."Iya daukan wani furaba"
Garam!! "Ta. ,_,rufe ,Kofa- —ta bar Inna da budadden Baki tana mamakin al'amarin Deeda. :-
" "Tomeya faru kumahaka?" ' Ta sungumi Kwanon Furan ta fita. , ' A can ta ji 'labarin abin da ya faru. Nan ta godewa Allah ,daba wanda'yanuna 'Gidan da» Deeda ta ke da sun

shiga wani tashin hankalin.
“ KARFE SHA BIYUN DARE
amma Sabeer‘ya‘kasa nutsuwa, k0 Abinci a:
wannari yammacin har zuwa dare bai iya ciba,
tsabar tafasar zuCiya, sai ka ce wanda akai masa
wani mummunan illa. K0da yake abin da bai saba
ba kuma baizataba. " duk lokacin da ya tuna
furkar deeda sai Ranshi ya Baci, yayi Tsaki
Banza»Mummuna Yar kauye Yar gidan matsiyata
Abin da yake’fadi kenan a harshen Turanci.Abin
da ya f1 kona masa‘zuciya shi ne, Mace ‘ce ta
ma‘sa wannan wulaqancin, waccé ba koman-
komai ba. '
"Shin Ina zai ganta ya rama wulaqancin datai
masa?" : ‘ ’
"Shin inya gantama ta'ya ya zai some rama
wannan wulaqancin datai masa?”
Lokaci guda Sabeer ya ji burinsa shi ne neman
yarinyar nan da 'kuma_ rama wulakancin da tai
masa wanda ya kasa samun irin wulakancin da
zai ma ta ya qona mata zuciya, Wanda ba zata
taba mantawa da shi ba har qarshen rayuwarta
Ibrahim yana hangosa ’yana ta. kaiwa da
komowa da alama har yanzu bai huce ba, abin na
damunsa. ‘
yayi qoqarin lallashinsa yaci abinci koda kadanne
amma ina wannan dare. Abincin
ma daci yake yiwa sabeer. Da kyar ya sha rabin
Kofin juice
' " Ibrahim tare ya kwana da‘ shi, ‘kowanne
juyi yayi sai yaga Sabeer na zaune ido biyu. ‘
‘ Shi dai tun da .ya ke bai taBa ganin abin da ya
hana Sabeer Barciba a rayuwarsa sai yau. K0
Jarrabawa bai taBa hanasa bacci
' Haka baitaba ganin Sabeer yadauki wani abu da
muhimmanci haka ba. A wannan dare ya kira
Farida. '
Ta dauka a gigice. ‘
‘Lafiya‘ Kanina, Waya yanzun nan?" 7‘
yi haquri Yayata
"Kanina ai ni ba ni da, matsala a kowanne: lokaci
zaka iya kirana damuwata. dai shi ne naga dare.
ne_,yanxu a naija lokacin da kowa ke baCci, dole

inji tsoron ,~ ganin Wayarka a wannan
IokaciHaka ne Yayata, kasa haquri nayi gari ya
waye, na ‘ga ,abin da ban taba ‘gani ba a tare da.
‘sabeer daga ni har ke har Daddy 'abin 'da mu ke
so mu gani a tare da shi kenan.“ -
"Kanina fada min mene ne don Allah?" "
Ta fada cikin zumudi da dokin sonjin mene ne
"Yayata‘ yau Iokaci‘ na farko da naga Sabee‘r .ya
zama (Serious) akan abu, ya dauki wani abu da=
muhimmanci da gaske har ma ya kasa bacci‘
yana ta (Planing) ta‘ yadda zai bullowa'
al'amarin, 'yana ta ‘ Kullawa da kwancewa. Kin
tuna Yayata ko Jarrabawa‘ k0 Ciwo ba ya hana
Sabeer Bacci?"
Haka ne Kanina. Amma na ji dadi ba ka ji wani
farinciki ‘da ya mamaye niba. Akan (Business) ne
ko Asibiti?"
Ibrahim ya dan yi shiru sannan yace "Karki damu
zan fada miki in kin zo k0 ma akan mene ne dai
shi ne yadda ya zama (Seriou) ya bada
muhimmanci akan abin
"Haka _ne qanina, ina mana addu'a‘ Allah Ya
mana jagora, ya kawo sanadin kimtsuwar
Sabeer".
"Haka ne Yayata, da alama Allah Ya kawo sanadi.
Ke dai ki ci gaba da addu'a da fatan samun
nasara ga abin da na yi niyyah
"Zan ci gaba da addu'a qanina, Allah Ya
taimaka". .
"Amin". Ya amsa.
Bayan tambayarta Iafiyarta ’ :da wasu al'amura
suka yi sallama.
Ya dawo ya samu har yanzu Sabeer na kaiwa da
kawowa. -
Ya isa gareshi ya jawo hannunsa ya ce "Sabeer
20 ka kwanta dare ya yi".
Ya Bata fuska. _ , ‘
"Uncle IB ya ,zan yi in iya bacci?" ‘ '
Idonsa ya kada.
"Ka ga wulaqancin da yarinyar nan ta min.
Please'Uncle IB ka taimaka min in nemo ta, ka
san ni yanZu k0 Unguwar ba zan iya sake
ganewa ba".

"Zan taimaka maka. Ina dai yarinyar ka
ke son sake gani?" ’
"Sosai don, ba zan iya kyaleta ba", ‘
"To kar ka damu za ta 20 har inda ka ke ta
sameka..amma dai yanzu ka kwanta gobe muna
da fita Asibiti". ’
Da kyar ya IallaBashi ya kwanta ya dinga juye-
juye ya kasa baccin har sai dab da Asuba - Bacci
ya sace shi. ~
Juyin duniya kuwa Ibrahim ya yi Sabeer ya tashi
su je Sallah amma yaqi, haka ya hakura dole ya
barshi.
Bai tashi ba sai wurin sha biyun rana. Nan ma sai
da Ibrahim ya je Asibiti ya dawo ya tashesa suka
fita tare.
*.* *.* *9*
tun qarfe shida na safe deeda da Inna mai Fura
ke layin ganin Likita, duk kuwa sammakonsu bai
sa sun ga Likita da, wuri ba Saboda wani Tiyata
na gaggawa da ya Shiga, sai da ya fito sannan
ya soma ganin marasa lafiya
Deeda ta bata fuska cikin Kosawa ta ce, "Dama ai
duk abin da aka ce ma kyauta ne sai. ka ga
wulaqanci. . ,
Ni dama tunda na ji Tabawa ta ce mu zo wannan
Asibitin kyauta ake ganin marasa lafiya na san za
a wahala.
Aik0 Asibitin gwamnati ana dai siyan Kati..."
"Wai me ya sa kin fiye gajen hakurine?" Kakarta
ta fada a hasale. .
' "Ke da ki ke neman lafiya k0 ma kwana za ki yi
ai sai ki hakura ki jira su ba mutane ba ne? Haba
kin fiye mitan tsiya.
Duba Asibitin nan da kyau kin san ya sha
karfinmu ba don alfarma muka samu ba"
' ‘ Deeda ta yi tsit! don ba ta son musu k0 wani
sa'insa da Kakarta.
Nan ta canja maganar da cewa, "Inna duba
hannuna fa ya wartsake, jikina ya mike ba kamar
da ba, sai ina ganin kamar yanzu ba ni da
bukatar ganin Likita".
"Kina da buKata". Kakar ta katseta.
"Ki ka san ko ya sake dawowa? Ai gara ki yiwa

Likita bayani in da Magani a ba ki da zai hanashi dawowa.
Kama ma ai ba duka jikinki ne ya wartsake ba, har yanzu ta ciki, ta wani wurin akwai inda ya ke yamutse". . ' ‘
"Shima a hankali ai zan washe kamar sauran
"Ki min shiru tunda har munyi haqurin jira har wannan lokaci kuma mun20 to ba'abin da zaisa mu koma...” 7
Kafin Inna ta rufe Baki wacce ta shiga din ta fito ta ce Deeda ta shiga. Ba ta Bata lokaci ba ta kutsa kai ya yin da Inna ke jiranta a waje.
Zaune ya ke akan (Table) Tebur din da ke cikin Oflice din, da alama shi ne Table din Likita. SABEER NE! !!
Hannunsa riqe da Game yana ta bugawa, gefensa kuma Fruts ne da Juice yana ci yana Game hankalinsa kwance. Hakan ba karamin nishadi ya ke sa shi ba.
Deeda ta turo. Kofar ta shigo tare da sallama. '
K0 daga kai bai yi ba daga Game din da ya ke ba balle ya amsa ma ta sallamar
Nan ta je ta tSaya a gefe gami da cewa, "Ina wuni Likita?"
Har yanzu bai dago kai ba sai dai ya amsa mata da cewa, "Likita na (Washing room) Bayi, ki jira ya fito
Nan ya ci gaba da game dinsa. Ita k0 _taja kujera ta zauna tana kallon yadda’ ya bawa game"‘ din muhimmanci. ‘ ’ "Lallai wannan bai da matsala a rayuwa "ta fada a ranta. ‘ ' Sai ihu yake yana dariya shi daya yana buga game yana morewa abinsa. 'Mutum babba dashi qaton Saurayi kamar Wannan' yana abin Yara Kai Allah Ya 3“ kyauta. - ‘ - T 0 ma wai shi ba Likita bane me ya keyi a nan?
Wai a gabansa zan ga likitan? KO shima Likitan ya 20 gani? Bari dai in tambayesa'
Ta mai da hankalinta gareshi ta ce, "Mallam kaima Likitan za ka gani ko in fita sai ka gansa in shigo?"
Har yanzun bai kulata ba. Haushinsa ya kamata.

Ta ce, "Wai kai ba ka jin kunya Kato da kai kana abin Yara?" '
Nan da nan ko Sabeer ya fusata, ya dago kai .gami da juyowa da sauri don ci. mata mutumci. ‘ Carab k0 suka yi ido biyu da juna. Ya mike tsaye cikin mamaki kuma a fusace, itama ta mike, ta Iura da haushinta da ya ji amma ita ba ta ' ma gane shi ba. .
"Na Iura yarinyar. nan ba ki da kunya, ba ki da mutunci! Uban wa ya kawo ki Asibitin nan?"
Ta kalleshi sama da kasa ta buga mai Tsaki tare da Harara ta ce, "Sa'a ka yi ban iya
Zagi ba da na ma ka wadanda ya fi naka ciwo. Kuma karka'yarda ka sake zan min Uba".
Sai an Zaga me ki ka isa ki yi? Dama nemanki na ke, yau sai na miki rashin mutuncin da ba za ki manta da shi ba".
"Banyi tsammani ba".
‘ Ta ba shi amsa kai tsaye.
"’Me kike nufi?"
Ta kada mai Idanunta wanda sai da ya sa yaji gabansa ya fadi. '
Wannan ne lokaci na farko da bama Mace ba, lokaci na farko da aka taBa kallonsa ido cikin ido ba tare da shakka k0 tsoro ba.
nace, "Ban tsammanin zaka iya ba. Ina nufin yanayinka da alamunka bana zaton ka Iya rashin mutunci , sabo da a yadda na ga alamarka girman jiki ne kawai kayi, amma har yanzu tunaninka da ayyukanka har kwakwalwarka ta yara ce ba su girma ba.
Yaro k0 ban tsammanin ya san meye rashin mutunci balle ya iya, sunansa kawai ka sani, don haka ka bari in Kwakwalwarka da tunaninka sun gama girma sai Ka zo mu kara rashin mutunci, in ka gwada min na 'YAN BIRNI ni .kuma sai in gwada ma ka na 'YAN KAUYE":
Tuni Sabeer ya kara harzuka, idonsa ya kada ya yi ja ya kasa furta ma ta komai, kuma ya kasa ma ta komai, sai azabar zuciya kamar za ta kashe shi. .
Tun-tuni Ibrahim ya ji hayaniyarsu ya fifo ya tsaya a kofar ya -harde hannu yana kallonsu

yana murmushi. . -’
Cikin qunar zuciya Sabeer ya Ce ma ta, "Fita Asibitin nan tun da ba na Ubanki ba ne, ba zakiga Likitan ba, kuma yau sai na nuna miki halin yarint Ya- zaro- Belt dinsa da karfin tsiya ya kai ma ta duka, ta yi saurin sa hannu kuwa ta tisge.
Mamakinta ya‘sa shi bude Baki.
_ "Bi a hankali Yaro kar (Body bulding) din da kayi ya yaudareka; kar ka ganni Mace ka raina min Wayo daga Kauye na ke, na ci Tuwon Dusa na ci na Dawa, kar ka nemi raina ni.
Kuma da na san Asibitin nan na Mahaifinka ne da ban soma takoshi ba."
Ta ja mai dogon Tsaki ta juya za ta fita, wani kololon Bakinciki ya. tokare masa zuciya, ya rasa me zai ma ta.
Ba ta ankara ba ko ta taka Sunul ta fadi qasa ta daku. . -
"Wash Allah". Ta fada
"Wayyo! Bayana".
Sabeer ya Kyalkyale da. dariyar mugunta yace,"Su Budurwar Kauye masu karfi an sha Kasa".
Ya matsa dab da ita yasa kafa ya' takéta .sai da tayi Kara yace"Duk karfin Budurwar Kauye ba ta isa ta kai Namiji ba, musamman na Birni, BIRNIN ma na GAYU Ya Kara taketa da Karfinshi ya ce, "Dama neman‘ki na ke tun rashin mutuncin da ki ka min ban manta ba, kin hanani sukuni kin hanani
Bacci' kin hanani cin Abinci, kin sani yawan tunanin wannan mummunar fuskar taki, har ta zauna a kwakwalwata.
Yau wannan hannun da ya watsa min Nono sai na Balleshi".
Nan ya kai daya Kafar ya danne Yatsun da qarfi"
‘
Ta sa ihun Azaba, sai da hannun yayi jini sabo da irin takalman da yasa ba na wasa ba ne.
"Wayyo Inna zai kasheni
Ibrahim ne ya matso wurin da sauri ya janyesa.
"Kai- Sabeer ba ka da hankali za ka kashe- 'yar mutane?"

"Kyaleni in ma ta illa, gobe idan ta. ganni za ta canja hanya. Kuma wannan kadan ma ta gani." ‘ Ibrahim ne ya taimaka ma ta ta tashi gami da dressing din hannun cikin . gaggawa ya samu jinin ya tsaya, amma bai yi nasarar tsayar da jinin ba.
Hankalinsa ya tashi, gaba daya ya rude, bai taBa tsammanin abin nasu zai yi tsanani haka ba da bai bari hakan ya faru ba. '
Nan ya sa hannun cikin qankara ya sa ma ta Magani sannan ya daure da Bandeji ya nufi ciki don dauko Allura ya mata.
Bayan fitarsa Sabeer ya harareta ya ce, "Kalli 'yanda ki ka zama abin tausayi...azaba kadai ta canjaki."
"Allah Ya isa Ta fada cikin zafin zuciya.
- "Kuma kai ne abin tausayi ba ni ba, don ni kam ban iya bin 'yan fage in yiwa mutum illa ba sai ‘dai in fuskance "shi. Ka ji kunya da ka nuna qarlinka akan Mace".
Ta ja Tsaki gami da matsawa dab da shi, bai ankara ba ta ja farar Rigarsa ta goge Jinin da ke zuba a hannunta gaba daya ta bata masa Rigar. ' ‘
Ya daga hannu zai Mareta, tuni ‘ta manta ciwon da ke hannunta ta cafke Hannun ta gantsara masa Cizo ta fita da gudu. " i
. Inna dai ba ta ankara ba sai ganin Deeda tayi ta fito da gudu a rude ta bita. "Ke Deeda!!!”. ' Can kuma sai ga Sabeer ya biyota da gudunsa. ‘ ‘ Inna fa hankalinta ya tashi, ta bisu tana,"Deeda! Deeda!! Deeda! ! !" Daga qarshe dai ta gaji ta hakura don ba‘ za ta iya gudunsu ba. ‘ - Sai da suka yi nisa sosai har suka fita Asibitin sannan Sabeer ya yi nasarar kamata ‘ Ba ta saurara masa ba' ta yi na ‘maza turesa da qarfinta. ' Sai da ya fada cikin wani ruwan dake a bakin hanya. . Tana' ganin ya' kai qasa kuwa ta arta ana Kare, ba ta tsaya k0 ina'ba sai da ta kai Gida, ta nufi daki ta rufe tana haki gami da tuno abin da ya faru kamar a wani Mafarki k0 Almara. . Inna dai hankalinta a tashe ta nemi abin hawa ta kOma bayan ta gama neman Deeda ba ta

ganta ba, ta tafi tana addu'ar Allah Yasa ta koma Gida.
Sabeer ya mike cikin takaici da bakin ciki da Bacin rai, duk’ Kunya ta kamashi da ya ga Yara da wasu Mutane suna kallonsa.
Wasu 'yan Mata kuwa har dariya suke suna mai da‘ yadda abin ya faru, da alama a idonsu aka yi.
Da kyar ya iya daga kafa ya miqe ya wuce kai sunkuye takaici da kunya sun IulluBesa, ya rasa ma ina za shi.
Shi 'dai bai gane hanyoyin ba, don haka dolensa ya koma cikin Asibitin, ga‘ shi 'ba Waya a hannunsa, haka' dolensa ya sunkuyar da kai yana Boye fuska ya koma cikin Asibitin yana kaucewa jama'a yana kulla tsiyar da zai ma ta Ibrahim yana ganinsa ya fashe da dariya
ya ja shi wani Office da ba kowa ya ce, "Sabeer kai ne haka k0 Ido na ne?"
Cikin zafin rai ya ce, "Wannan Aljanar Yarinyar in na kamata k0 sai na harbe yar banza! Ni zata yiwa haka?"
"Ya isa haka Sabeer. Yanzu dai abin da ya faru ya faru ba yadda ka iya, ka koma Gida ka canja Kaya ka barni in yi aiki Please tun da na san yau ma kai kam ka tashi'ba za kuma kayi aikin ba"
Ya Bata fuska.
"Uncle IB ka san ni ban gama sanin hanyoyin garinnanba, Please ka 20 ka mai da ni
Ibrahim ya cira kai ya kallesa ya ce, "'Ka yi hakuri Sabeer ba zan iya barin aikina in yi naka ba, yanzu mafa marasa lafiya na dakatar ina sauraronka.
Please har yaushe komai sai an maka kai ba Yaro karami bane, in ba zaka iya komawa ba zan ma (Diver) din Office magana ya mayar da kai Gida, amma ni dai ba zan bar aikina ba".
Sabeer ya yi fishi ya fisge Key din Motar ya fita, Ibrahim ya bisa da kallo sannan yaci
gaba da Aikinsa da niyyar in ya gama’zai je inda suka hadu da yarinyar nan ya nemi Gidan su.
%%%%%%%%%%
Sabeer kuwa, sai da ya gama zagaye_ kafin ya kai ga gane hanyar Gida, ga shi ba dama ya kira

Abokansa za su masa dariya.
Haka ya yi ta shan wahala kafin ya isa Gida ya koma ya samu Momi ta dawo, wato Hajiya Amina, sai dai bai bi ta inda ta ke ba ya wuce ya cire kaya ya shiga Wanka. .
Ya jima kwance cikin Ruwa a (Bat Tap) yana tunanin irin abin da zai ma yarinyar nan da inda zai sake ganinta, sai dai hakan ya gagara, tunaninsa bai samu maganin matsalarsa ba.
Nan tunani ya fado masa, kawai ya kira Abokansa don su tayashi nemanta da kuma ba shi shawarar irin rashin mutuncin da zasu ma ta.
Bayan ya fito ya ji kiran (Door Bell) na Bangarensa, bai kula ba sai da ya sa Kaya ganin an matsa ya fita ya bude.
Momi ce tsaye tace, "Lafiya Saber tun dazu ina tsaye, ina ka shiga?" ' ' Ya dan sunkuyar da kai yace, "Momi ina Wanka ne Shigo mana,'dama ina shirin inna fita zanje in gaishe ki. Kin dawo laflya k0?" : "Lafiya kalau". Ta amsa masa lokacin da ta ke zama ta ce, "Yayunka duk suna gaisheka.' .
- ' ' Daddynku ya fada min komai' game da_ dawowarka, sai ka dage ka koyi 'Aiki, in da hali ma harka Karo ilimi a fannin da kafiso, duk da Asibitin muna da Likitoci, amma akwai bukatar ka a Asibitin. _. Ina so ka daukeni kamar Mahaifiyarka, duk abin da ya shige ma duhu ka 20 ka sameni Bangarena na Shawara k0 wani abu. _ Sannan ina fatan ba ka da matsala da Ma'aikata masu kula da Bangarenka da Abincinka suna gyara ma ka Side dinka ya kamata, yadda kuma ka ke so?, duk abincin'da ke bukata order kawai za ka yi..."
"Na sani Momi ba sai kin bata bakinkiba Ya katseta. "Nan Gidanmu ne Gidan Ubana ba sai an bani ko ance in tambaya ba. . Sannan Sister ita ce Mamana ita ce komai na, kar ki yi qokarin zama Mamana ki zauna a matsayin .Matar Babana ina ga hakan zaifi mana ni dake Sannan Uncle IB yana tare da ni, duk - bukatata shi kadai ya isa ba sai kin sa Baki ba' In koyi aiki k0 kar in. koya, wannan ba matsalarki bane Batayi mamakin halinsa ba, ta yi wani murmushi irin ta

manyan Mata da idonsu ya bude tace To shi ke
nan tunda haka ka ke so, muje a haka-tun da kafi
son in, rikeka a matsayin dan ‘Mijina‘ Fine, ni
kam na kware wajen iya,rike ‘dangantaka tunda
rikon dan kishiya kakeson nai maka ina
maraba'da hakan. inaso ka ,sani bani da matsaia
da kai, bazan cutar da kai,ba amma fa kar ka
shiga gonata kayi kokarin tsayawa a matsayinka".
"Kema ina son ki tsaya a iyakarki".
"Da kyau".
Ta fada tare da girgiza kai ta fita. Ya bita da
wani matsiyacin kallo gami da rufe gofar Falon ya
koma ciki. ,
Wani radadi yaji ya ziyarci" hannunsa, nan ya mai
da kallonsa kan hannun, ya yi jawur har ya soma
kumbura. '
Ya ja dogon Tsaki, haushin Deeda da tsanarta ya
Kara shigarsa, don gurin da ta gantsara masa
Cizo ne.
"Amma wannan akwai 'yar rainin wayo...ni 2a ta
fadawa bafar magana? Me take nufi da na girma
amma hAlayena ba su girma ba?
Tana nufin ni yaro ne
Nan ya mike yana kallon kansa a Madubi tun
daga sama har Kasa, duk ta yamutsashi
kwana biyu kawai.
banzar yarinya yar KAU YE mummunar yarinya za
ta sani a gaba... zan mata rashin mutunci To
amma me zan ma ta?”
Waya ya dauko ya bugawa Abokansa yana musu
neman gaggawa.
Cikin minti talatin suka hallara.
"Lafiya Sabeer irin wannan neman gaggawa?"
"Ba lafiya ba
Ya fada a qule.
"Wata Aljanar Yarinya ce ta sani a gaba, ta daga
min hankali",
Salim ya kalli Nura sannan ya kalli Nura sannan
ya kalli Sabeer din ya ce, "Ba dai mutuniyarka da
ta watsa ma No... ."
Wani mugun kallo da ya masa ya sa shi gum da
Bakinsa bai Karasa ba.
Ya ce, "Na ganota".

Sabeer din ya ce,"Shawara na ke so ku bani. wane rashin mutunci zan ma ta?"
Nura ya ce, "Me zai hana ka yiwa banza lahani, wato ka banke banza da Mata sai 'ta Karye ta dawo me Kafa daya?" ,
Saber ya girgiza kai.
"Not Bad Kai kuma ,fa Salim, me ka ke gani?"
Salim yace, "Hakan da ya fada dai-dai "ne" k0 ka kadeta ko ka yi hayan wasu su saceta ta, Bace Bat na kwana biyu a rufeta inda k0 Hannunta ba za ta gani ba don Duhu, ta Yini kwana da Yunwa.." ' .
Sabeer ya ce, "1 Hope shawaranku ya yi aiki,
Nura ya ce, "In dai har muka yi yadda na ce dole ya taBata. In ta zama Gurguwa ai ta .nakasa".
Sabeer yace "Ba wannan ba, samun inda take ma bala'i ne". "Zamu nemota a same aren da muka hadu da ita
zamu nemota, zan mata ,abin da ba za,,,,'yan Samari". Muryar Ibrahim ne
suka mai da hankalinsu garcshi. 'yana wannan murmushin nasa ya ce '-'.da;abin da zaku yi a rayuwa kuke ku ke planing tsarawa da yafi muku".
ya yi dariya gami da fadawa jikin unless ib yace kaida Sister ’kune rayuwata (My whole world) ya yi, murmushi ya ce kadai fadi, amma ba Uncle IB bane zai zauna ma. da Mata 'yar KAUYE ba. Ka tuna
ya fada tare da murmushi ya Bata fuska.
Ya ce, "Uncle IB karka Bata min rai, kasan na tsani 'yar Kauyen nan da aure amma nafi tsanar yarinyar nan (I hate her the most)". .
Ibrahim ya ce, "Ni zan fita dama na leko dubaka ne zan fita ni ina da abinyi bani ’da' lokacin tsanar wasu k0 daukan fansa, in kuma ba'ka bar maganar ba sai na fadawa Sister". '
Ya langaBe kai. "
’Yace Uncle IB kar ka min haka mana".
"Na dai fada ma ka ka zaba daukar fansa .ko Bacin ran Sisiter".
Nan ya fice ya barshi. Ya maida kallonsa kanSu
Salim ya ce,‘ "Guy plan cancel"

Nura ya ce, "Wai kana nufin kana tsoron Uncle IB da Yayarka?"
Sabeer ya ce, "Sabeer bai tsoron kowa, bai kuma shakkar kowa just that ina son Sister da Uncle IB (and 1' respect them a lot) ban san Batawa Sister rai, kuma sabo da wannan Aljanar ba zan 'Batawa Sister rai ba, sai dai duk randa na hadu da ita sai na ma ta illa fiye da wanda ta min".
Yana magana yana kallon inda ta dankara masa Cizo.
££££££££££££
da tambaya da bincike a Unguwar, Ibrahim ya gano Gidan Tabawa inda'
Deeda ke zaune. Tana daki k0 tana shirya kaya ranta a Bace
sabo da washe gari za ta tafi Gidan Aikinta.
Yaro ya shigo. "Wai .ana sallama da budurwar da ke
Gidan nan".
' Inna mai F ura ta kallo Yaron.
",Waye ne
"Wani me Mota ne". Yaronn ya bata amsa a takaice.
"Jirani". ' '
Nan ta shiga ciki ta dauki Hijabi 'tabi bayan Yaron.
"Mu je
Yana zaune cikin Motarsa a Kofar Gidan ya hango Yaro da Inna. Mamaki ya kamashi. Ya yi saurin fitowa daga Motar lokacin da suke isowa. Innan ta kalleshi kallon tambaya. Kallon da take masa ya sa ya sha jinin Jikinsa. Tabbas ko k0 ba a fada masa ba ya san ko Uwarta ko Kakarta ce. Ya kalli Inna da kyau, ya ga irin shigar: da tayi ' '
A ransa ya ce "Lallai wannan yarinya ta san inda ta yi gado..." . Inna ta katse mai tunani ta ce, "Gani; naji an ce kana sallama da Budurwar Gidan". . Ibrahim ya kalleta da kyau ya rasa ma me zaice mata. ' Tsayuwar da ta yi ta riqe kugunta yasa yaso tuntsurewa da dariya amma sai dake yace "Budurwa' na'ce ba tsohuwa ba
Ta kallesa da kyau ta 'ce, "A Gidan nice budurwa k0 kana musu ne? Me ya kawoka, me ka ke?

nema?" '
ta tsareshi da ido. Gaba daya ma ya rude ya rasa me zai ce ma ta.
yanata.soshe-soshe da kame-kame, can dai ta tausaya masa tace, "jikata ka ke nema me za kai mata ya sauke numfashi ya ce, "‘Dama ta je Asibiti ganin Likita ne to sai suka samu saBani da kanina ta taf1 ba ta ga Likitanba na 20 in ba ta ha'Kuri kuma in ji meye matsalar don ni Likita ne". ‘
ta zaro Ido ta washe Baki. "Aiban sani ba.
‘ wannan ciki za ka shigo. Dama haka Likitocin-suke na birni har Gida suke biyi marar lafiya? Ikon Allah, ai Deedan tana Ciki shigo
‘ har ciki. A tsakar gida ta shimfida masa Tabarma sannan ta shiga Ciki‘ ta kamo hannun Deeda.
ke fito ga Likita har Gida ya 20 duba ki". ‘
Deeda ta kalleta cikin mamaki.
"Likita?"
"EH". Ta amsa ma ta a takaice.
"Ashe da rabon za ki ga Likita kafin ki tafi Zo mu je". ' ' Ta ja'ta har Tsakar Gida wurinsa.
"Likita ga Jikar tawa”.
Deeda ta kallesa cikin mamaki.
"Likita har Gida?"
Ta ja Kujeran- zama na tsakar Gida ta zauna, ya yin da Innar ta zauna a gefensa.
Deeda ta gaisheshi Sannan ta tambaya.
"Anya ni kuwa ka zo nema? K0 ka Bata ne?"
"A'a ke na 20 nema. Sunana Dr. Ibrahim, ni ne Likitan da ki ka zo gani da safe ku ka samu saBani da Kanina".
' Ta girgiza kai.
"0h!" Gami da dan yamutsa fuska.
"Wannan qanin na ka?"
Ya yi murmushi gami da cewa, "Ina ji dai kuna da (Allergy) da juna, duk lokacin da aka ambaceki sai launin fuskarsa ta canja, ‘kema haka tun randa ku ka' hadu jininku bai zo daya
Na 20 in ga hannunki ne in ba ki haquri sannan in ji me ye matsalarki
Kallonshi ta ke tana murmushi. A ranta ta ce,

"Akwai bambanci tsakaninsa da qaninsa.
Shi mutum .ne mai sanyin hali da kirki. Haduwar farko na gane hakan.
Shi ko wancan haduwar farko na gane halinsa 'mara kyau.
'Jin tayi shiru ba ta amsa ba Inna ta yi carab Ta amsa.
"Likita hannunta dai da sauqi, mu Mutan Kauye ne muna da. dabara da namu Magun'gunan irin wannan CiWon. -
Zan dai' yi ma ka bayanin babbar matsalar duk da yanzu taji sauki ciwon da kansa ya baje".
Nan ta soma zayyana masa ciwon Deeda tun tana karama har zuwa girmanta da shigowar su Birni ya soma bajewa da kansa a hankali.
Ya dan yi shiru na tsawon lokaci 'yana kallon Hannayenta.
Ya so ya fuskanci matsalar sai dai duk da hakan sai ya yi bincike.
Ya ce, "Na fahimta Kaka, sai dai duk da hakan tana buqatar zuwa Asibiti sabo da a can ne zamu yi duk wasu gwaje—gwaje don gane ainahin ciwon, duk da dai yanzu ya washe ba matsala, amma 'gaba zai iya dawowa, duk da ban tabbatar da wane ciwo bane, amma dai ba abun damuwa bane, in ma ta sha Magani to da yardar Allah za ta rabu da shi.
Don haka gobe in Allah Ya kaimu ta sameni a Asibiti karfe goma."
murna ta lulluBeta. ,
:Na gode Likita."
Mun gode, duk da goben zata tafi amma" zata ganka. kafin ta tafi".
Ya mike yana fadin allah ya kaimu goben, Inna tana ta godiya, deeds kuws kallonSa take tana mamakin' kirki iron nasa
"ya mike ya kalleta ya ce, 'miss Deeda inga hannun naki?" .ta-' sunkuyar dakai ta mika masa hannun ya kalla ba tare da ya taBata ba ya ce,
"Kina da jiki 'mai kyau don bai kumbura ba, in dai yana miki radadi ki sha (Pain Reliver)
Paracetamol da
,to"Na gode"

Nan ya yi sallama da su ya wuce.
Deeda ta bishi da kallo ya yin da Inna ta rakashi har iofa. Ta dawo ta samu Deeda zaune ta yi-Tagumi. '
tace, "Deeda kina tunanin tafiya ne? Karki damu Allah na tare da ke ina tare da ke
idan kin‘ ga ana saki abin da ba dai- daiba ko ba kya so zan dauko ki mu dawo ". Ta“ dan yi murmushi ta ce, "Inna haka ne, ina tunanin tafiya sai dai na‘ fi tunanin barin karatuna duk da na koyi abu da yawa na iya abubuwa da yawa karatu da rubutu, turanci da ma abu da yawa. Haka na samu ilimin Addini‘ sosai a Makarantar wanda da ban san su ba..
- Alhamdu lillahi da zaman da na yi a {Gidan Tabawa da gatan da ta min, sai dai ilimi ba ya qarewa, yanzu na soma dandanarshi zan so in ci ~gaba'da samunsa.
Sai dai ilimi ana samunsa ta kowacce fuska, duniyar ~gaba dayanta Makaranta ce, kamar yadda na koyi wani abu yanzu na fahimta, akwai mutanen kirki akwai na tsiya.
Inna duba bambanci tsakanin wannan Likitan da qaninsa.
Mutum mai nutsuwa mai kirki mai mutunci. Kaninsa kuwa..." ‘
Ta ja dogon numfashi. "Bana son ma tunashi balle maganarsa.
Inna kar ki damu ina maraba da sabuwar rayuwar da zan shiga, a wurina wani sabon Makaranta ne na koyon wani sabon i‘limin
rayuwa. Idan Allah Ya kaimu gobe zan je Asibitin zan roqi Tabawa mubiya tacan» sai mu wuce. Insha Allahu akwai‘haske a tattare data tafiyar da zan yi". ' .Inna ta yi 'murmushi. ‘ :"Na ji dadi Deeda yadda ki ka kwantar da hankalinki ba ki daga hankalinki akan tafiyar ba. Allah Ya taimaka ya sa alheri. Muna gari daya, zan dinga zuwa dubaki, za ki dinga zuwa kema in kin samu dama". Haka suka kusan kwana- suna hira gami da tsara yadda tafiyar za ta kasance. . Innan ta ci gaba da yi ma ta nasiha da bata shawara akan zaman rayuwa da kuma sababbin

mutanen da za ta tarar ta yi mu'amala da su.
ya kuke ganin zaman deeda DA saber zai kasance a birnin gayu anyama zasu hadu kuwa?
h shared a profile .
birnin gayu
chapter6
Deeda kuwa ita ya fara gani, duk da kuwa akwai wadanda suka rigata; sabo da ita ya fara cewa a kira masa.
. Tare suka shiga da Inna. Ta yi sallama, ya dago kai yana murmushi ya amSa ma ta sallamar.
Ya kalli Inna ya yi dariyar tsokana ya ce, "Su Kaka 'yan mata, an iso?" .
Ta yi dariya ta ce "Ya ka ganni ras da ni, duk Budurwar da mu “ka jera sai a 'daukeni an barta". . Yace, "Kwarai kuwa..Ai Kaka-“kin yi fice , 'Deeda dai kallonsu take tana dariya Kwarai halayen Ibfahim yana burgeta, duk da‘ alamu sun nuna dan masu hali ne ga ilimi ga wayewa amma ba shi da girman kai sai saukin kai sannan, 'ga dukkan alamu mutum ne mai halin kwarai. ‘ ‘ ' ' .
Bayan ya gama barkwancinsa da Inna ya mai da hankalinsa kan Deeda ya ce, "Malama Deeda zan fara da miki tambayoyi kafin in kai ga ‘ maganar Ciwonki. ‘
Tambayoyin da zan miku kamar cikakken sunanki, shekarunki da sauran‘ su, sabo da ina son bude miki (Folder) don rubuta komai game da ciwonki, ne nan gaba in kin zo sai a dauko koda
ba ni zan ganki ba wani Likitan ne in ya karanta zai san komai game da rashin lafiyarki. Ina fatan kin fahimta?"
Ta girgiza masa kai.
"Na .fahimta".
Cikin‘nutsuwa ya ke ma ta tambayar tana ba shi amsa har suka gama, ya dinga ma ta tambaya game da Tarihin ciwon na ta tana ba shi amsa, amma wani lokacin Inna ta kan tsoma Baki har suka gama suka je ya ma ta gwaje- gwajen da ya dace sannan ya ba ta magani ya kalleta ya ce, "Kar ki damu ba wani matsala ba ce na tashin hankali, kamar yadda ki ka gani yanzu Fatarki ta fara washewa in kin Sha maganin nan zai

taimaka miki sauran duk ilahirin jikinki ya
wartsake.
; Sannan' irin ciwonki ba a cika samunsa ta nan
ba, yana wuya a samu masu irin wannan
Ciwon, shi yasa ma ba za a fahimci mene ne ba
sabo da ba kowa ya san ko ya taba jin irin ciwon
ba sai Likitoci irin mu.
Jikinki da fatar jikinki baya son inda ki keda
yanayin wurin da ki ke zaune, misali;
Ruwan Garinku, yanayin Abincin wurin da irin
Iskar Garin da aka Haifeki ki ka girma, kina da
(Allegy) da wannan garin yankin wurin gaba daya,
don haka da ki ka bar garin ki ka shigo nan sai
aka yi dace jikinki ya karBi yanayin inda ki ka
dawo, don haka fatarki da jinin jikinki ya fara
washewa ya mike da kansa daga yamutsewar da
ya yi.
Ga mutum mai irin jikinki ba .kowanne irin Abinci
da ruwa zai karbe ki ba.
Kai hatta kaya zuwa mayukan da 2aki dinga
amfani da .,shi ba kowanne Jikinki zai karBa ba,
dan haka a duk lokacin da ki ka fara cin wani abu
ki ka fahimci canji a jikinki ki yi saurin kiyayewa,
haka kaya da sauran abin da ya Shafi‘ jikinki.
Daga.kin yi amfani da abu ki ka ga ya canji a
jikinki to ki yi saurin barin abun, in kin kiyaye
insha Allahu ba za a samu matsala ba.
Yanzu» ga Magani‘ da kuma sunayen irin Abincin
da ’za ki kiyaye cin su da kuma irin abin da ya
kamata ki dinga ci, duk ba wani abu mai ' wuya
bane da zai gagara". . Nan Deeda ta yi shiru tana
jinsa tana kuma tunanin Ciwonta
Wane irin ciwo ne da ba ta taBa ji k0 ganin me;
irinsa ba? Ikon Allah! Allah mai yarda ya so!!
"Allah Ya kare ya kuma ba ki laflya Deeda".
"Alhamdu lillah, Likita ina godiya, yau na samu
haske akan abin da ya shige mini duhu.
Na gode, Allah Ya saka ma ka da alkhairinSa". ' .
Deeda ta fada‘tana' kallonsa. Ya ma ta murmushi
yace,’ "Karki damu Allah Ya Yi
mana jagora ya bamu LAFIYA, sai ki kiyaye kuma
ki dinga shan magani".
"Zan kiyaye insha Allah. Na gode".

Inna mai Fura tace, "'Likita Kudi fa? Kamar nawa za mu biya?"
Ya yi dan'daria ya ce, Kaka 'yan Mata nan Asibitin ai, na kyauta ne, k0: farkon zuwanku ba a fadi muku ba
"An fada mana Likita, sai dai in magani ma kyauta ne da kudin Katin
Ya yi' murmushi yace, "Duk kyauta ne sai dai in bamu da maganin mu rubuta a siya a waje". ,
"Ikon Allah! To yanzu Likita da kudinka ka ke siyan maganin?
' Inna ta fada, kuma ta sa masa ido alamar amsa ta ke jira.
Ya yi dariya sosai ya yin da Deeda duk kunya ta kamata saboda tambayar Inna.
Ibrahim ya ce, "Kaka 'yan mata ai nima biyana ake, ina na ke da kudin daukan nauyin Asibitin nan? . '
Ai Likitocin 'muna da yawa, 'kowa da fanninsa. Ni dai ina fannin Fata ne, wato masu matsala irin na su Deeda da makamantansu.
Me Asibitin shi ke biyanmu da kuma sauran masu kudi masu neman Lada, sukan ba 'da gudunmawar .Magunguna da sauran abin da :Asibiti ke bukata k0 kudaden biyan Ma'aikata da sauransu don neman Lada da taimakawa Talakawa marasa hali."
"Ikon Allah!" In ji Inna.
. "Irinimu ke nan? Kai! Allah Ya saka musu da alkhairi, Allah Ya yi musu albarka, Allah Ya sa sauran masu Kudinmu su yi koyi da hakan 'Amin". Ibrahim ya fada yana dariya. Suka mike, Inna ta ce, "Mun gode Likita, Allah Ya yi ma ka albarka".
Ibrahim ya amsa da, "Amin' Ya kara da cewa, "In dai akwai wani matsala ku dawo, in kuma babu sai bayan sati shida ku dawo".
"To Likita zamu kiyaye, mun gode".
Har bakin kofa Inna na masa godiya ta fita, ya yin da Deedan ta juyo ta yi masa murmushi ta ce, "Gaskiyar Inna kana da kirki.
duk da ban san sauran ba, na san dai kafi kowanne Likita kirki a Asibitin nan". ' "Thank you

are, welcome". Ya fada yana murmushi. Sannan ta fita. Ya yi dariya hade da girgiza kai yana dariyar Inna a ransa ya ce, "Tsohuwar nan akwai magana, ga shi har ta sa shi Surutu don harya manta yaushe rabonsa da ya tsaya surutu haka k0 a Gida ko a Asibiti.
Lokaci guda kuma ya shiga tunanin ciwon Deeda.
"Allah Ya sa iyakar wahalarta ke nan, don kuwa in hakan ya ci gaba to a gaba za a samu. matsala, baya fatan abin da ya ke gudu ya faru".
Shigowar mara lafiya ya katse mai tunani.
Nan ya ci gaba da aiki ya yin da ya ke tunanin yadda zai sa Deeda ta masa aikin da ya ke so duk da k0 ya san abu ne mai wuya.‘
%%%%%%%%%%
deeda ta isa Gida cike DA farinciki
zuciyarta a sake ta tsinci kanta cikin
nishadi haka kawai zuciyarta ta ma ta haske, sam ba ta jin bakinciki ko Bacin ran tafiya, sai ma tunanin sabuwar rayuwa da sababbin mutanen da za ta tarar take yi. ‘
Inna mai Fura ma zuciyarta ta yi ma ta dadi, ganin yau ta daina ganin kunci a fuskar Jikarta. Haka kawai ta dinga jin duniya ta 'dawo musu sabuwa.
A kofar Gida Tabawa k0 suka tarar da Mota da direba har ya iso yana jiransu.
Tuni har Tabawa ta gama jibge kayan Deeda a Mota ita kawai suke jira.
Ko cikin Gida Tabawa ba ta bari sun shiga ba ta taresu da su taf1 kawai don duk abin da zu su buqata ta 'dauko.
Inna ta kalleta ta ce, "Tabawa saurin me kike haka, k0 ciki ba za ki bari mu shiga ba kamar wanda ake kora
' ."Ba‘ haka bane Inna, Hajiyar tun " dazu tai Waya ta ke ta dada'min kinsan ita ba a ma ta wasa, komai na ta kan qa'ida ne.
Kin san fa kun dade a ASibitin nan har na yi dana sanin tafiyarku
Deeda na jinsu ba ta ce komai ba. Tabawa ta bude musu Motar suka shiga baya ya yin da ita

ta zauna a Gidan Gaba suka tafi
Inna mai Fura an shiga Mota mai tsada sai.
washe baki take tana zuba Kauyanci.
Ya yin da Deeda ta fada duniyar tunani da sake-sake. ‘-
Ta yi nisa cikin tunani ba ta ankara ba ta jii
Motar da suke ciki ta tsaya da alamar sun iso.
Ta daga kai ta gansu a Kofar wani ‘- makeken
Gida mai girma da tsayin gaske, da alama Gidan sama da qasa ne, kuma komai na Gidan fari ne tas! ba Surki. ‘
Tun daga kan gate din Gidan har kalar fentin
Gidan da komai na ciki fari ne tas. Tana nan ta zurawa Gidan Ido ‘tana kallon irin kyansa da tsarinsa tana mamaki.
"Dama ashe za a iya samun Gida irin wannan?"
,' Can ta hango saman Gidan an rubuta; 'BIRN IN GAYU’. .
Tana cikin karantawa ta ga gate na bude da kansa, don ita dai ba ta ga wanda ya 20 ya bude ba, tana mamakin abin suka kutsa ciki, har yanzu ba ta ga wani kalar abu a Gidan in ba Fari ba, hatta Ma'aikatan Gidan da ta lura suna kaiwa da kawowa fararen Kaya ne a jikinsu.
Tabawa dai ko a jikinta, da alama ta saba zuwa
Gidan, Inna da Deeda aka bari da kauyanci.
Tafiya su ke Deeda da Inna na bawa idonsu
Abinci har suka kai' Bangaren Hajiya wanda
Gidan sama ne, don kuwa ta (Lifter) suka tafi, wato
Rana ta farko da Deeda ta taBa ganin lifta kuma ta shiga.
Inna dai sai addu'a ta ke har suka fita suka fada falon Hajiya.
_ Nan kallo ya koma sabo, sun sameta 'tana harde a kujera jama'a na kewaye. da ita ana gaisawa.
Nan ta mike ta ja su wani falon don ganinsu a can, da fara'arta ta karBesu. ‘ Tabawa ta yi mamaki kwarai don ta zaci Hajiya za ta Bata rai sabo da jimawar da suka yi ba su iso ba.
Derda ne ta soma gaisheta, ta amsa tana dariya sannan ta gaisa da su Inna.

Ta kalli Dceda ta ce, "Na san dai k0 ba a fada
min ba‘ wannan ce 'yar Gidan tawa k0?"
Tabawa ta amsa da, "Eh ita cr Sunanta Khadija,
amma ana kiranta da Deeda, amma ke kuma kina
iya kiranta da duk sunan da ya yi mi ki". .,
Hajiya ta ce, "Zan kirata da duk sunan da kowa
ya santa da shi. Ina fatan dai zamu samu
fahimtar juna?"
"1n Allah Ya yarda Hajiya, jikata ba ta da
matsala".
Tabawa ma ta karBa, "Gaskiya ne Hajiya Deeda
akwai gaskiya 'da rikon amana yadda kikeso.
haka Deeda ta ke".
Hajiya ta yi dariya ta ce,"Da kyau abinda nake
son ji".kenan ‘ Deeda ta yi shiru tana kallon
yadda masu Aiki ke kaiwa da kawowa, motsi
kadan Hajiya za ta dau waya (Intercom) ta kira
mai Aiki tana ba da umarni. ' ' Kamar Hajiya ta
san me ta ke. fadi a, cikin zuciyarta ta ce,"Deeda
ba aikatau zatai ba". Inna mai Fura ta ke yiwa
bayani. ‘ ‘ ' "Kamar yadda na fadawa Tabawa- ,
’yar daki na ke nema wacce zan yarda da ita, zan
iya bata amanar dakina, za ta iya sanin sirrina
ba, tare da ta cuceni ba. "ta Kula min da daki da
kuma wasu sirrika na kasuwanci na wacce zan
iya amince ma ta 'da dukiyata da sauransu. Da
fatan kun gamsu da bayanina”. ,. "Na gamsu,
kuma ina tabbatar miki da Dceda ba za ta ci
amanarki ba. Sai dai don Allah nima jikata na
damka miki, ita amana Deeda ita kadai ce dani
yanzu haka itama haka da fatan duk abin da za
zai shafi addininta da al'adarta ba". - ‘ "Kar ki
damu Inna," na karbi amanar Deeda zan riketa
amana muddin ta rikeni da amana da zuciya daya
to zamu ji dadin zama da
Sun jima suna tattaunawa wanda Inna mai Fura
.ta gamsu da maganganun Hajiya __, ta kara
yiwa Deeda jan kunne Sannan Hajiya da kanta ta
kaisu inda Bangarenta ya ke Inna kam ta kasa
yarda wai Deedanta ne za ta zauna a“wannan
dakin
Tun daga nan hankalin Inna ya soma kwanciya:
ganin yadda Hajiya ta dauki Deeda ta amsheta'

hannu bibbiyu ba kyama. .‘
Ba su jima ba suka yi sallama, lokacin ne ' idon Deeda ya ciko da hawaye, lokaci na farko ke nan a rayuwarta da za ta rabu da Inna tun tana karama har ta taso su yi fada su yi wasa su yi dariya. '
Fadawa jikin Inna ta yi tana kuka.
Inna ma .sai da ta yi kuka tana lallashi, ganin hakan ya sa Hajiya ta ce kar ta damu za a dinga kaita ta ga Kakarta, kuma Innan ma za ta iya zuwa ta ganta a duk lokacin da ta ke so. Haka dai suka yi ta kwantar ma ta da hankali har suka tafi sun yi akan za a dinga tarawa Deeda kudinta na aiki sabo da Inna tace sana'ar da ta keyi ya isheta na buka'tun yau da kullum ‘ita kuma kudinta sai a tara ayi aurenta da su.idan har lokaci yayi
()()()()()()()()()()()
kwana-a-tashi, a hankali Deeda ta Asoma sabawa da rayuwar BIRN IN GAYU, haka Hajiya ta dinga nuna ma ta komai da komai yadda ake aiki da shi. Deeda ta lura Momi mace ce mai fara'a da jan mutane a jiki ta hanyar Siyasa. a Haka nan ba ta da matsala da mutane ko sa ido da takura, kullum tana cikin fara'a. Sai dai abu guda Hajiyar muguwar 'yar kasuwa ce me son kudin tsiya, duk da tana da kudin amma ba ta son ta ga ta yi asaran k0na Sisi, haka nan bata bari kudadenta su makale, duk rintsi sai ta sai'n ayadda za su fito. , Tun da ta fahimci Deeda yarince mai'wayo, dabara da saurin fahimta saita jata a jiki yadda Deeda ke hada ma 'kudi na kayan da suka shiga suka flta bata' kuskure shi ya fi birgeta, yadda Deeda ke aiki da Computer lokaci guda tana ma ta Transfer na kudedenta da ke Bankunan qasashen waje zuwa na Gida naija yana burgeta, ta lura yarinyar
Bayan wannan Deeda ke gyara ma ta Dakinta don ba ta yarda wasu masu aiki suna mata gyaran daki sabo da tsoro da rashin yarda sai '- -
a yanxu, duk wani me harka da Hajiya ya san Deeda,‘ ta kan bata wasu: shawarwarin wani lokaci ta yarda

kasuwanci kala daban-daban; take Wani Iokaci
Deeda takanyi‘ tunani da mamakin yadda Gidan
yake ' ba ruwan wani da wani, kowa harkar
sa yakeyi ba sabo ba shaquwa tsakaninsu wani
Iokaci sai ta yi kwana biyu .bataga wani
mahaluki ba daga Hajiyar sai 'yan Aiki,‘ _ duk
zaman da ta yi a Gidan bata ga
'yan Gidan ba, ta dai ga »
Hoto, Wanda aka ce ma ta sun yi anre amma
bata taba ganin sun 20 ba. '
Bayan maganar kasuwanci da wani aiki ko
shawara ba abin da ke hadata da Momi, haka ma
su aikin Gidan ba mai mata magana balle ta yi
sabo da su, kowa harkar gabansa ya kd ‘ Wannan
ya sa Deeda ~ta tsinci kanta cikin kewa daga ita
sai TV sai Camputer wanda sune Abokanta masu
debe mata kewa anba ta komai;
Ci da Sha da Sutura komai ta sameshi a wadace,
zama cikin ni'ima da cima mai kyau yasa ta
murje ta yi Haske ta yi Kyau, sai dai ba wani
farinciki ko nishadi a tare da ita, jikinta da
yanayin rayuwarta ya canja: sai dai cikin zucin ba
wani canji, zuciyarta tana nan kamar~yadda ta
ke da, Karatunta ya tsaya sai dai ta godewa
Allah‘da ta samu wannan dama. ‘ ‘
‘ Abu . guda ke sa ta farinciki in tana gaban
Computer ko in Hajiya ta ba ta wani aikin don da
alama Deeda tana da sha'awar (Business)
kasuwanci wanda a zahiri shi ne burinta ta
karanci Business ta Zama babbar Yar kasuwa
wata rana.
Lokacin da maganin Deeda ya kare ta cewa Momi
za ta gai da Inna, ba ta musa ma ta ba kuwa ta
bata Driver ya kaita akan da yamma zai dawo ya
dauketa.
//////////////
iNNA ta ji dadin ganin Deeds sosai, musamman
yadda ta ga ta goge ta murje tayi kyau, ga Kaya
kamar wata 'yar Mai kudi ' ta fito fes! Fes!! da
ita, Inna Baki a washe. -- Tare suka je Asibiti.
Yadda Ibrahim ya ga Deeda tabbas akwai canji
sosai a tare da ita, tun daa yanayin shigarta,
yanayin maganarta da wayewarta ya bam-banta

da yadda ya taBa ganinta. Anya zai iya ma ta wani magana game da "' Sabeer‘.’ . Ga Sabeer abin nasa sai gaba ya ke, ga Daddy ya kusa dawowa har yanzu ya kasa Control din Sabeer. ' Deeda ta katse masa tunani. "Likita lafiya kuwe? K0 akwai matsala ne?" " "Ba komai ina dan wani tunani ne amma ba a
game da keba
' A halin yanzu ke dai ba ki da matsala don haka ina ga ba sai kin Kara shan wani magani ba, da :alama inda ki ke zaune ya karbeki don, na lura ya taimaka gurin gyara fatar jikinki.
Yanzu za ki iya tafiya, sai dai in akwai wani matsala nan gaba ki dawo". ;
"Na gode Likita, zan wuce
"To ki gaida inna".
“Za ta ji, tare da ita ai muka zo tana waje
Ya mike yana murmushi ya ce, "Bari in 20 in gaida 'yan mata kar ta fasa auren
Dariya sukai duka suka fita a tare. Inna na ganinsu kuwa ta mike tana dariya, suka gaisa ya ce "Na 20 gai da Kaka 'yan mata kar wani ya min shigar sauri”.
"Oh to da ba ka 20 ba sai in yi sabon saurayi don samari har sun min yawa".
wayar da ta yi Kara ya ja hankalinsu.
Bayan daga wayar ta yi sallama ta dan ja
gefe sannan ta'dawo wajensu tana cewa Inna mu tafi
Nan suka yiwa Ibrahim sallama, har sun fara tafiya Ibrahim ya tsai da ita, ya iso garesu ya ce "Miss Dddda in ba za ki damu ba zan iya samun lambar Wayarki in Saurayinki ba zai damu ba ya fada cikin zolaya. ‘ “ Ta yi dariya ta ce "Su Likita manya, Saurayina ba zai damu ba, ga lambata Ta rubuto masa, ya yi godiya gami da cewa zata lya Jin kiransa kowanne lokaci. Ta so tambayar' nasa lambar sai . ta kasa da ya koma ya zurawa Wayar tasa ido yana kallon lambar
Karfe biyar ta‘yi sallama' ‘da. Inna da Tabawa don dama dazun Hajiya ne ta yi mata Waya ta tambayeta karfe nawa za a 20 daukarta. _
''''''''''''''''''

Wani dare Deeda na zaune‘ gaban
Computer bayan idar da’ Sallar Isha'i ta‘
mai da hankalinta sosai kan Computer
din sabo da wani Bussiness School da, ta shiga
online(P. C Training and Business Collage) tana
jin
dadin Karatun sosai da koyarwan, haka nan tana
ganewa da yake tana son abin. ‘
Wayartane yayi kara, ta yi mamaki kwarai don
kuwa da_ wuya Momi ta kirata a wanna lokaci.
Haka nan tsira‘run wanda takeda Lambarsu masu
siyen Kaya yana wuya su ma ta Waya a irin
wannan lokaci.
Ganin an matsa da kira yasa ta mike ta nufi inda
Wayar ke Chaji ta dauka, ta ga sabuwar Lamba
ce. ‘ .
Nan ta daure ta danna 0k. tare da yin Sallama.
Muryar Namiji ce.ta ji an amsa ma ta sallamar
nata. __
Yayi dariya ya ce, "Na yi sa'a kenan da har
inatunanin ba za a dauki Wayata ba
Da fatan dai ban matsawa ranki shi dado ba?"
" wace ni?" Ta amsa masa.
""Na so in fahimci' muryar".
"Dr. Ibrahim ne. Ya ba ta amsa.
"Likita Bokan Turai, barka da dare”. Ta fada tana
yin dariya, da alamar kuma ta ji dadin kiran nasa.
"Lafiya, Alhamdulillahi".
"Dama bugowa na yi mu gaisa in ji ya jikin
naki?;Da fatan dai ba wata matsala
"Ba komai, jiki da sauki na warware, ina godiya",
Sun jima suna hira sannan suka yi sallama.
Tun daga wannan rana Ibrahim ya kan yi ma ta
Waya a duk lokacin da ya samu saukin aikinsa.
Haka nan itama tana kiransa sabo da shakuwa ta
shiga tsakaninsu., duk da ba ganin juna suke ba a
, Waya ne’
Sau da dama Ibrahim ya kan nemi shawara
wurinta, haka itama ta kan bude masa
damuwarta da matsalolin da ta ke fuskanta na
rayuwar yau da kullum, domin Deeda jin Ibrahim
take ‘Kamar Aboki, Dan uwa,
Bayan Kakarta ba wanda ta taba kusanci da

shakuwa da shi sai Ibrahim.
A hankali Ibrahim ya fahimci Deeda da ’yadda take, yanayin rayuwarta da tunaninta duk mai sauqi ne.
Haka idan ta samu dama za tai abu da yawa a duk lokacin da ya tsinci kansa cikin damuwa k0 wani Bacin rai to Wayar Deeda da kalamanta ke kawo masa sauki, yana samun nutsuwa sosai ,da : kullum sai ya tambayeta Inna mai Fura.
,Yawancin wayarsu yakan mata magana akan halayen Sabeer, don har yanzu ya kasa shawo kansa kokarinsa Sabeer ya'fahimta.‘ ta kance ita laifinsu take gani DA fun farko suka kasa controll dinsa said yanxu
' ' Ibrahim ya kan yi murmushi ya ce, "Deeda ba za'ki fuhimta ba a hankali,'wataran zan warware miki zan fahimtar da ke dangantakar da ke tsakaninmu da Sabeer da Gidan su halin yanzu, mu barshi a yaddaki kace . Ta yi ajiyar . zuciya tace, To.shi ke nan 'Ibrahim, ni dai ‘na san kai mutumin kirki ne (Very good human being) wanda wannan halin na ka na daya daga cikin abin da yake hurgeni ina ganin girmanka da dajarka, ya yin da Kaninka.,.." ‘ .~
"Ya isa Deeda, ba zan jure yabon dakike min da kushe Sabecr be, mu bar maganar". Ajiye Wayar ta yi ba tare da Sunyi 'sallama ba, saboda ta fahimci maganar da ke had'asu fada . ‘kenan Ta kan yi mamakin irin yadda Ibrahim ke qauar Sabeer baya Kaunar abin da zai taBashi, baya iya jure jin. lafin Sabeer daga bakin wani. A hankali Deeda ta fahimci cewa ta yi wani irin shakuwa da Ibrahim cikin kanqanin lokaci. '
&&&&&&&&&&&&&&&&&
Karfe biyun dare amma Ibrahim ya ‘kasa ' . rintsawa yanata kaiwa da kamowa, komai ya masa Zafi. Ya tuno yadda suka kwashe da ' Sabeer sannan damuwarsa shi ne wasu sababbin ABokai da ya ga Sabeer din ya sake, ba su da aiki sai kashe kudi yawa zuwa Party da neman; Matan tsiya Maimakon .Sabeer ya gyaru sai kara dauko hanyar-lalacewa' yake
Ya kasa rikon Sabeer, ya kasa kula da shi, ya

kasa riqe amanar da aka bashi, ga aiki yayi masa yawa ga nauyin Asibiti a kansa ga na marasa lafiya ga kuma Kamfanin Alhaji, Kudade da yawa sun bata wanda bincike ya nuna da Hannun Hajiya ciki, komai ya masa zafi, ya ma rasa abin yi, ga nashi Personal Problem din.
Ya dauko Wayarsa ya kira Farida idonsa jawur "Kanina". Ta kirashi muryarta qasa qasa
Hakan ya fadar masa da gaba. '
"Yayata lafiya na ji muryarki haka?” "Kanina na yi aiki ne kawai na .gaji, kaina ke dan min Ciwo”.
"Yayata Please ki dinga hutawa kinsha Magani ko‘ in20 ne?
Ni fa yadda na ji ki ya jefani cikin tashin hankali‘da damuwa". .
"Kanina kar ka damu na fadi ma gajiyace kar ka damu zan kula da kaina”.
Sabecr da da Daddy suna bukatarka , ke ba kya bukatata Yayata". ' "Ba haka bane Kanina".
"Haka ne Yayata?" .-
"To in kc ba kya buqatata ni ina buqatarki Yayata"
Ya fada cikin murya mai rauni.
"Kanina ka yi hakuri na sun ban maka adalci ba. ka yafe min kanina, ka yi qokari ka fahimci matsalata".
Tuni har hawaye ya wanke ma ta fuska Kanina akwai matsala k0? Me ke faruwa?
"Ba komai Yayata". Ya yi dariyar dole don kwantar ma ta da hankali.
"Kar ki damu, kawai dai na tsinci kaina cikin kcwarki ne ina missing dinki, kar ki damu, sha Magani ki kwanta". .
"To .Kanina na gode. Ina nan zuwa very soon”. ‘
"'Allah Ya kawoki lafiya . Na san in kin zo da yardar Allah komai zai dai-daita".
'Ka kula da kanka kanina da Sabeer da Daddy gaba gaba daya. Sai da safe".
Ta yi saurin ajiye Wayar. Ya jima yana kallon‘ Wayar sannan ya soma danna lambar .Deeda sai kuma ya fasa, qarfe ukun dare me zan ce ma ta?"
Ya nufi dakin Sabeer don ganin me yake ya yi Bacci in bai yi ba zai masa magana da gargadi

ya qara tuna masa abin da Mahaifinsa ya ce, ya kuma sanar dashi Daddyn ya kusa dawowa.
Hango qofar dakin ya yi a bude Wuta a kunne abin ya ba shi mamaki sosai, ya isa dakin da sauri, gabansa ya yi mummunar faduwa, Sabeer ne ya gani kwance da Kwalaben Giya, kwance a gefensa baya cikin hankalinsa yana sake da kayansa da Takalmansa da wasu Kwayoyi a gefensa.
innalillahi wa inna ilaihirr'jiu 'un.'.'" Ibrahim ya fada cikin tashin hankali.
Wani irin baqinciki da tashin hankali ya bayyana a fuskarsa. " ' " "
Ya isa' gareshi da wuri.
"Sabeér" Ya kira sunansa da karfi. ' *
"Wato abin na ka har ya kai haka?"
' ' Idanunsa suka kada suka yi jawur, kukan ma ya kasa, ya lura Sabeer k0 hannunsa bai iya dagawa balle bude ido sai surutan banza
Cikin takaici da bakinciki ya cire, masa Takalma tare da gyara masa kwanciya, ya tattara kwalaben ya bude wani Raramin Fridge da ke manne a bangon Dakinsa.' Kwalaben giya ne masu tsadar qaske a cike a ciki. '
Nan ya hau bincikc k0 ta ina a dakin, haka ya dinga yin karo da kayan maye kala-kala. Bai taBa shiga tashin hankali da bakinciki irin na wannan Dare ba.
"Ya aka yi na yi sakaci haka. na ci amanar Maman Sabeer na ci amanar Farida ban rike Sabccr ba ban kula da shi ba".
Nan yakama kai awurin yanakukan bakinciki da takaici tare da tausayawa rayuwar Sabeer in ya mutu a wannan hali ya yi asara babba ' .
- Sam' ba shi da nutsuwa _a duniya balle ya samu nutsuwar neman lahira. ' ~
A wannan dare Ibrahim bai rintsa ba ya kwana yana sallah yana kai kukansa gun Allah tare" da Addu'o'i sosai.
Hakan ya dan ba Shi nutsuwa. Da Asuba ya kira Farida amma ba ta dauka ba, ya sake kira, wani Likita ya dauka ya masa bayanin tana Asibiti gaskiya bata da lafiya, amma ta ce ba ta son ya

sani, amma Likitan ya tabbatar masa da cewa
jikin na ta da sauki.
Tashin hankalin da Ibrahim ya tsinci kansa ya.
munana. ‘
"Yayata ba lafiya ga halin da Sabeer ya shiga, ga
Asibiti ga Kamfani, ga Daddy baya nan Duniyar tai
masa zafi ya rasa abin yi. ,
"Shin da wanne zaiji? Ba zai' yiwu ya tafi wurin
Farida ya bar Sabeer, a wannan haliba , ga Asibiti
da kamfani duk suna buqatarsa, yana kaucewa
kadan komai zai tsaya.
Yana cikin wannan halin nan ya hango Sabeer ya
tashi cikin fishi ya nufi inda yake ya hau fada ta
inda ya ke shiga ba ta nan ya ke fita ba.
Nan Sabecr ya zuciya shima ya amsa masa
cewa, "Uncle IB zan yi abin da na ga dama ba
wanda ya isa ya takura min ko ya‘ hanani. To me
ye in na sha Giya? Me ye a ciki za ka zo kana
min fada? - '
Ni fa ba zan Yi aiki irin ka ba kullum Asibiti
kullum kamfani, zan rayu yadda na keso, Kudine
Uwata da Ubana sun tara min domin jin dadin
‘rayuwa, to me ye damuwarka
dadin rayuwa , ba za ka
Ka matsa min ka sa min ido. Ina kyale ka ne
albarkacin Sister.
Ka rabu da ni, zan yi rayuwata yadda na ke so,
kuma Giya ba wanda zai hanani in sha. Mene ne
in na sha Giya?"
"Tas" Ibrahim ya wankeshi da Mari.
"Meye in ka sha Giya? Ba ka san me ye ba in ka
sha Giya kana dan MusUlmi kana irin wannan
maganar?
Kai da ka san illar shan Giya da muninta da ko'
sunanta aka ambata sai ka ji tsoro da kyamar
kiran sunan na ta. .
Duniya kawai ka _sa a gaba, ba ka san zaka
mutu ba, k0 ba ka san RAYUWA BAYAN MUTUWA
BA? K0 ba ka san kwanciyar Kabari ba ne?
. Ji bi kanka, ba ka jin‘ kunyar zama cikin duhu
ba'ka san addininka ba? '
Ada ina ganin abin na ka kamar yarinta amma
yanzu na lura ya zama ganganci;

To bari ka ji, daga yau na rufe duk wani Account
dinka na kudi, duk wani hanyar Kudi na toshe
maka ita, Makullan Mota babu su, kuma tun da
ka ce ba za ka yi aiki ba, to ba kai ba fita. kana
nan
cikin Gidan nan, ba Waya ba Abokai duk na
rabaka da komai sai ka zaBa k0 zaman Gida a
kulle ko ka bini Office qafata-Kafarka duk inda na
shiga, zabi ya rage na ka".
Nan ya ja kofar dakin ya rufe ya tafi ya kyaleshi
yana ihu yana kwalla masa kire.
"Uncle ib please ka budeni ba zan iya zama a nan
ba.
Please Unclc IB ba zan kara ba, zan yi duk yadda
ka ce‘
Wayyo Uncle iB to ka mai da ni wurin Sister".
Haka ya yi ta ihu amma bai saurareshi ba ya
wuce ya figi Mota.
A wannan lokacin mutum daya ya keson gani ita
ce Deeda, sai dai ya yi rashin sa'a yana zuwa
Gidan ya samu Inna ta ce masa ai Dccda ba ta
nan, ba a nantake zama ba. . ‘
Bai Kara ce ma ta komai ba ya fita ya kira
Wayarta. Sai da yaiyi qara' sau‘ uku kafin ya kai
ga ta dauka, kafin tace Wani abu ya tambayeta.
"Kina ina?"
"Lafiya?" Ta tambaya.
"Ina son ganinki ne yanzu-yanzu! inda hali ki
fada min inda ki ke yanzu zan 20 in sameki, kar
ki min wata tambaya sai na 20".
Ta lura yana cikin zafi da Bacin rai, don haka- ba
ta sake masa wata tambaya ba.
Ya sake tambayarta, "A wacce unguwa ki
ke?"
"Ka san BIRNIN GAYU?" "Birnin Gayu‘?" Ya
maimaita cikin mamaki. Ta ce "Eh inkazo Gidan
ka yi min waya". "Kina nufin a Unguwar ki ke?"
Ta amsa da, "Eh". "To shi ke nan gani nan
zuwa". Ya 'ajiye Wayar ya tafi yana tunani. Shin
wane Gida Deeda ta ke a unguwarsu? To koma
ina nevdai yanzu burinsa ya ganta k0 za ta
taimaka masa ya samu saukin matsalarsa. Haka
Deeda ta dinga kaiwa da kawowa yanda taji

tashin hankali a muryarsa yasa ta cikin damuwa, sai ta ji itama na ta hankalin ya tashi. Momi ta. fIto ta ce "Ta kula da Gidan 2a ta shiga wani miting a Office ana jiranta". Nan ta ma ta sallama ta fita, ya yin da Deed: ta kasa zaune da tsaye, Wayar' Ibrahim ya shigo, ta yi saurin dauka yace ma ta, "Ga n'i a BIRNIN GAYU, ta ina ki ke da Gidan?"
"Jirani a wunrin gani nan fitowa";
Nesa' da Gate din kadan ya yi parking yana jiranta, ya yin da ya zurawa wurin ido yana jiran ya ga ta ina za ta bullo. '
Bude Baki ya yi mamaki ya bayyana a fuskarsa lOkacin da ya hangota tana fitowa -daga BIRNIN GAYU, wato cikin Gidansu. :
Tsaye take a qofar Gidan tana kalle kalle.
Ya lura da hakan hakan ya sa ya fito daga cikin Motar ya nufo gareta, itama ta ganshi ta isa. gareshi fuskarsa cike da damuwa ta kula ta ce ,"Laflya Likita, me ya-faru haka .ka ke son ganina?" "
Ya kalleta cike da mamaki ya ce, "Deeda dama a BIRNIN GAYU ki ke?"
"Eh, labarin mai tsayi ne a Gidan na.' ke amma fa ba Gidanmu bane, aiki na ke a Gidan".
' "Aiki? Wane irin Aiki?" ' ' Ta ja dogOn numfashi. , a i "Zan, fahimtar da kai a hankali. Yanzu dai ka fada min mene ne?"
Mu je can mu Yi magana".
Ya wucc, ba ta bishi ba sai dai kallon mamaki. Nan ya dawo ya jawo hannunta har suka isa bakin wani karamin Garden yaja kujera ya ce, "Zaunai ' Ba ta musa ba ta zauna, ita dai ya zame ma ta- abin kallo da mamaki.
Ganin haka ya sa ya kalleta ya ce, "Yanzu zan ba ki dukkan wani amsar tambayarki.
Deeda ina cikin damuwa da tashin hankali ' wanda na ji ina son ganinki don duk duniya a yanzu bani da wanda zan zauna in fada masa matsalata.
Deeda k0 ba ki min maganin matsalata ba zan samu saukin zuciyata tun da na bayyana miki damuwa—ta.

Deeda ki taimaka min koda kalaman karfafa
guiwa ne da kwantar da hankali don ina
bukatarsu".
Hawaye ya gangaro masa wanda hakan ya daga
hankalinta, Ibrahim da kullum murmushi ke
shimfide a fuskarsa wanda murmushinsa ya isa
'ya kwantarwada duk Wani mai damuwa hankali,'
ta ji - kamar ta rungumeshi ta ba shi baki, sai dai
ba halin hakan.
Ya lura da yanayin data shiga hakan yasa yayi na
maza ya daure ya yi ma ta wannan murmushin
sannan Ya ce, "Kar ki damu Deeda (1m
okay),'nasan kina mamakin shigowata Gidan "nan
haka? To nan dai Gidan mu ne
"Gidanku?" Ta fada tare da mikewa tsaye tana
dubansa cikin mamaki.
"Tabbas haka batun ya ke muna Gida daya amma
bamu taGa sani ba?
Sai dai ba abin mamaki bane in kin yi la'akari da
girman Gidan nan da yanayin rayuwar Gidan nan
ba ruwan wani da wani; musamman Momi da ba
shiga bangaren mu take yi ba".
Ta kallcshi ta ce, "Amma Ibrahim na yi mamakin
kasancewarka dan Gidan nan, halinka ya bam-
banta da na sauran jama'ar Gidan nan.
Ibrahim halayyarka da dabi'arka ta bambanta da
ta su."
"Deeda ke nan, kowa da yadda Allah Ya yi. shi,
kowa da irin halinsa da tunaninsa.
Yau zan ba .ki labarin-DANGANTAKATA da Gidan
nan da matsalar da na ke ciki, ina buqatar
taimakonki da tallafawarki
"Ina jinka Ibrahim. Ni kuma na yi alkawarin
taimaka ma ka in dai bai f1 karfina ba". »
Ya kalleta sosai, itama ta kalleshi a hankali. Ya
labarta mata komai. '
Lokacin da ya gama ba ta labarin sai ta yi ajiyar
zuciya ta ce "Lallai Ibrahim kana cikin tsaka mai
wuyar fita.
To sai dai ba abin da yafi karfin Allah, mu yi
Addu'ar Allah ya kawo mafita.
'Sannan Ibrahim me zai hana Yaya Farida ta
dawo Nigeria sai na ga kamar idan tananan

komai zai 20 da sauki tun da Sabeer ma ya fi jin maganarta, haka nan za ku taru tare da Daddy‘ ku rike Kamfaninku da Asibiti a tare, amma barinka kai daya da wannan nauyin ba abu bane mai sauqi". "

‘Y a yi murmushi ya ce, "Deeda ke nan, yadda ki ka dauki abin ba haka bane, akwai dalili mai Karfi da ya sa Yaya Farida ta nesanta kanta da mu, wanda ba ta so mu sani, "kuma 'wani sirri nena daban tsakaninmu da ita.

Sannan Daddy shi ya Bata Sabeer tun farko, wani ma yana hukuntashi wahala yake masa, ba zai jure ba balle shi da kansa. . '

' Deeda a yau in na samu Sabecr ya kimtsu ya san me ya ke to ina mai tabbatar miki da matsalata za ta zama kadan. Sabeer shi ne babban damuwarmu da matsalarmu a yanzu. Deeda ki taimaka min".

Ta kalleshi tace "Da me Zan taimaka ma ka Ibrahim bayan kaima ya gagareka balle ni da jininmu bai hadu 'ba, wanda kaima ka san hakan, "Deeda naga Hope akan Sabeer lokacin muduwarku ta farko, yadda ki ka yi (Handing) dibsa cikin kankanin lokaci ya burgeni, rana ta farko da naga Sabeer ya zama (Serious) ranar da ki ka fara 'haduwa da shi, tun daga wannan ranar na ganki a wata aba ta hanyar taimaka min mu canja rayuwar Sabeer mu inganta rayuwarsa . Deeda za ki taimaka min?"

! Ta kalleshi a karaye cikin sanyin murya da tausayawa ta ce, "'Ibrahim zan so taimaka ma ka, zan iyA komai don in kawo kwanciyar hankali a rayuwarka.

Kaine mutum na farko da ka kalleni da qima da daraja har ka ga wani abu na dabam a tare da ni. Dukkan rayuwata na taso cikin tsana da tsangwamane wanda Mahaifina ma da ya haifeni sai da ya gujeni- ~,

Kaine namiji na farko daya fahimci 'ni mutum ce har ina da wasu (Qualities) k0 dabi'u,‘ halayya masu kyau da har zan tallafl rayuwar wani, zan yiwa wasu amfani, nima mutum ce mai amfani. Na gode da wannan karramawa taka da

mutuntawa ta ka. .
Ka yi Abota da ni lokacin da bani da ,kowa, na ke cikin rayuwar kewa.
Ka tausaya min ka taimaka min lokacin da na ke cikin hali na rashin lafiya, ka mayar da ni mutum wacce ta isa ka nemi shawarata k0 share min hawaye.
Ni din nan da ba komai ba kowa ba har na isa ka nemi taimako a wurina.
Tabbas Ibrahim dabi'unka, halayyarka abin so
Ni Khadija zan iya komai sabo da samun nutsuwarka muddin bai kaucwwa Addini ba.
Sai dai Ibrahim bana jin akwai taimakon dazan maka, don kuwa Sabeer bai daukeni mutum ba maba balle ya bani damar kawo wani gyura a rayuwarsa
Irin su Saber Mace mai kyan gaske 'yar masu kudi ma basu isa ba balle ni Deeda 'yar Kauye wacce ba ta da komai a rayuwa daga ranta sai “Ify sai kuma godiyar Allah, wacce don in rufawa kaina Asiri da 'yar Tsohuwata na baro Garinmu da Kauyenmu don rufin Asirinmu ni da ita duka.
Ina yiwa Momi aiki, haka. aikin da na ke.wa Momi mai kyau ne da tsabta, ta rikeni Amana,~ haka.
Ka ga k0 bani da hanyar taimaka maka kuma bani da abin taimaka maka da shi".
Ya‘ harde'hannuwansa a kirji tare da sakar ma ta murmushin da ta ji ya saka ma ta nutsuwa yace "Deeda kenan, ni na ga abin da ba ki sani ba a tare da ke ‘
Ke kanki kinsan Allah ne mai kyauta da bayarwa, Ya yi miki baiwa ta hanyoyi da dama wandaba ba kowa zai iya saurin ganinsu da fahimtarsu ba lokoci guda sai ‘wanda Allah Ya nufa. .
Idan Allah Ya bawa wasu baiwar na dukiya, to kema fa akwai wani sirri da baiwa da ya miki, wanda ke kanki ba ki sani ba.
"Ke kuma kin iya nunawa matum ba kya jin baushi da wuri ke shi yasa ki ke iya zama da Momi”. . .
Ta yi dan'dariya, "Ai ko Momi ba ta da matsala".
‘

"Hakane a wurinki, sabo da ba kya taBa ma
ta Kudi, kuma ba ki sawa dukiyarta ido
Kin san yanzu ba ta da matsala da ni da Sabeer,
in dai ba shiga harkar Kamfani zamu yi ba, ta
barmu da Asibitin, ita ta rike Kamfani.
Kinji fa tun Daddy yana da Rai take son rabon
Gado.'
Tana jin dadin yadda Sabeer baya zuwa Office sai
kokarin turashi Asibiti ta ke don kar ya 20 ya Sa-
mata Ido wanda shi duk ba su dameshi ba, da
Asibitin da Factories da Kamfanonin Alhaji duk
basu gabansa". ‘
Ya kalleta ya ce, "Bari dai in yi shiru don kar in ci
gaba in bugo Gangar Kusa da Dirom. ME YE
DANGANTAKARKI da- Momi?"
Ta yi mutmushi ta ce, "Yanzu kaima za ka ji".
Nan itama ta labarta masa. ‘
Ya ce, "Na lura Deeda za mu yi babbar Business
Woman (You have PasSIon in business)".
Ta yi dariya ta ce, "Kwarai (Business is my
Passion) ni da bani da k0 KWANDALA!"
Ya yi murmushi ya ce"Ni na gani a tare da
ke? Kuma in kin bincika tarihin manya-manyan
'yan Kasuwa masu Kudin yanxu, to ba su dako
Kwandalar suka fara har suka samu suka zama
manyanmu a yau".
"Ibrahim ke nan, haka dai ka ce, amma ni dai bani
da wannan bukatar".
"To na ji, yanzu mu bar wannan maganar, zan
wuce 0fdice ina da abin yi da yawa. Ina fatan za
ki yi nazari akan maganata?"
” "Maganar Sabeer Ibrahim na fada maka ba abin
da zan iya".
"Za ki iya, ki bar komai a hannuna".
"Na ji, zan tafi nima ina da abin yi
"Toshi kenan
Suka mike a tare. ' '
"‘Sai mun yi Waya k0 in ce sai haduwa ta gaba,
zan zaga da keki san BIRNIN GAYU da kyau". tayi
murmushi gamida cewa Allah shi kaimu
to nima nace Allah shi kaimu gobe donjin ci
gaban wannan qayataccen Ibrn.
ah shared a profile .

birnin gayu book2
chapter7
lokacin da IBRAhiM YA KOMA
dakin Sabeer ya budeshi hankalinsa ya yi matukar tashi, saboda‘ da ganin yadda Sabeer ya yi kaca-kaca da ‘- dakin, komai ya rusa ya fasa na fasawa ya zubar‘, da na zubarwa. .
Harda Cystal Glases dinda aka yi decoration. . da su a dakin da Glass na Windows sai da ya fasa ya zub da kayayyakinsu, Dakin ya dawo'kamar na Mahaukata. ‘
bayan ya gama fashe-fashen da rushe- rushensa ya kwanta yana ta kuka yana fada da' masifa shi daya. . . '
Ibrahim ya tsaya cak ya rasa abin yi. Shin ya zanyi da yaron nan ne. Sabeer? ‘ ‘
Wannan wane irin rashin hankali ne, ko .shaye-sbayen da ka ke yi sun soma taBa ma ka kwakwalwa ne?" 1
Ya fada cikin fishi.
eh"Sun taBa min kwakWalwa Rayuwarka ,ko nawa? ‘
Kana min Shisshigi 'ka matsa, min ka. takurawa Rayuwata, so ka ke ' in .mutu, ka Rufeni a daki ka kwace komai ka‘rufe ni a daki so ka ke in kwanta bakinciki ya kasheni? Na rasa abin yi That Why 1' keep my. Self Busy ".
"'Ibrahim yace, "Oh! Ta nan. kuma ka bullo
Ai da aiki'ka ke 'son‘yi da ba haka' ba, amma tun da ka Samarma kanka mafita shima aiki ne a wurinka' at least ka samu abin yi, .ci gaba ka ‘zo ka fasa na falo , ga su nan
Sai daifa ka sani yadda 'ka Bata ba 'mai gyarawa k0 ka zauna a ciki haka k0 ka gyara' da kanka; '
'
Sannan- 'Ma'aikatanka duk zan' sallame su in canj‘a-muSu‘ wurin aiki ba‘mai sake maka komai tun daga kan gyaran 'dakinka, falonka komai'naka ba mai yi, kai za ka share» ka goge’ kayi komai abu daya Zan ma ka shi ne zan dinga kaWo maka abinci, zan sa a kaWo maka, don na san baka iya Girki ba. '-
Bayan Wannan k0 Wanki ba mai .sake. maka, ci

gaba da Barnarka in ka gama ka in kaga zaka iyazama haka a ciki ‘shi ke nan, in kuma ba za ka iya ba’ Sai ka gyara kamar yadda ka bata , ba yawo ba Mota da Waya, sannan, na yiwa (Guard) magana. kar wanda ya bari ‘ka fita sabo da umarni nane Kar ka manta Daddy ya ban' wannan (Power) idan bayanan nan nine'mai bada' doka da umarni. , ' - . . Kuma’ magata akebi a ‘Gidan nan duk wani side da ka ke jin, za ’ka je ka zauna na rufesh-nan 'side dinka- da ka Bata nan za ka zauna kaka gyara‘ko ka zauna cikin datti. ' Yana fadin hakanya juya ya tafi abinsa ‘ba tare da ya saurareshi ba, Sabeer' ya bishi‘cikin fishi yana masi fa. ' ‘ , "Me ka dauki kanka, kai wayeda za ka hanani yin yadda naga dama ka isa kace ni zan yi Shara da goge-goge? ' '
Wallahi ba ka isaba (Wh0 the hell are you?)
Nan Gidan Ubana ne, Kudi na Ubana ne zan yi yadda na ga dama.." ,
Ibrahin bai 'saurareshi bayaje ya shiga Motarsa ya fita. .
, Sabeer ya bishi .zai bude daya daga cikin Motocin da ke wurin, tuni ya gaga Security sun tsareshi sun hanashi taba kowacce Mota, haka ba Driven daya saurareshi, saboda ko wacce ‘ Mota da Driver nta
Motarsa kuwa Ibrahim ya kwace Key din.‘
Sabeer ya dinga tsawa da' ‘fada yana ihu yana kiransa. "
Zagi ba kalar da bai musu ba da Hausa da Turanci' duka, amma kansu sunkuye ba . su kulashi ba haushi ya ishe shi, ya nufi Gate. Zai fita nan ma (Guard) suka tareshi.
Duk kofar da yabi zai fita ba hali, ya dinga masifa da fada.
"Nan 'Gidan’Ubana ne, ba Wanda ya isa ya hanani”fita duk sai NASA an koreku inDaddy-ya dawo,
Ku su way‘e masu Gadin banza TalakaWa kawai matsiyata -' " Kash! Amma na- tausaya maka; Wannan shi ake kira (POWér less) Juyowa ya yi cikin fishi don ganin mai ‘ maganar. ~tsaye take ta harde hannu tana masa dariyar tsokana;

,. fuskarsa ‘cike da-mamakin‘ ganinta, ' yace
"Ubanwa' ya kawoki Gidan nan?
Waya' baki, matsayin shigowa Gidan nan?
daman haushinki nakeji dana hakura saboda .
Sister, amma Yau kin kawo kanki
'"Me 'zakayi Ba‘abinda zaka iya
min,“don baka'da'- Wannan matsayin,=-baka da
wannan‘pOWern bata rufe bakiba ya‘cafko
wuyanta zakiga abin da- Zan miki
Masu gadin ne suka yi saurin janyeshi da gani
ranshi yai mugun Baci ya hau fada da masifa
‘tsabar zuciya da Bacin Rai 'bai san yaushe
Hawaye‘ya soma zubo masa ba ta matsa gefensa
tana mai kallonTsokana da Tunzura ta ce "So ba
zaka iya komai ba sai dai ka yi ta ihu. kana kuka
(Just like a baby) gentle Sabeer, kyakkyawan
Matashi mai ji da kudi da naira young men
handsome. ‘guy
'yau ya zama Abin tausayi yanzu (He is nothing
but a powerless_ baby) ko ni yar Kauye "Talaka
mummuna na fika matsayi da. power a Gidan
Ubanka (HOW sad) Umarninka baya aiki; k0 ni
yau na fika power a Gidan nan".‘ Wani mugun
kallo yake mata. Tabbas da zai samu Bindiga da
zai iya harbeta, tsanarta da qinta ya qaru a
zuciyarsa. - .
Ta ce, "Na san haushina ka ke ji, amma bari na
gwada maka, kana son fita ko?‘ Guard ku bude
gate". .
' Tuni' ko-ya'ga sunbude gate din.“ ., "How dare
you? ” Ya wankesu da Mari.
"Ku har kun isa in muku magana kuqibi wata
banza ta baku arder kubi? - " yau sai kun rasa
aikinku, sai nasa Daddy ya koreku a Gidan nan." ,
‘ Ta matsa gabansa ta miqa masa Ruwan
Paro."Sha ruwan'sanyi Saheer .ka yi aiki da
kWakwalwarka-‘Me ,zaisa Daddy ya koresu? Why
‘ not you? Gidanku ne Gidan
Mahaifinka ne ka ce, amma duk da
haka ’baka da wani amfani yanzu, baka da
Power nemawa kanka power kana da . Kudi ba ka
ko'wanne motsi ita yakeji, ita ya ke gani.‘
Ibrahin na' kallonsa amma bai. ce masa komai ba
dun ya san ba shi da maganin matsalarsa a
yanzu. ..
Tsaki ya ‘yi ya naushi gaban- motar yaji kamar
ya fashe da kuka... '
’ "Yi'hakuri 'Mallam sabeer karka fasamin Mota".
‘ - ’ Lokacin ya bude-idonsa ya gansu Airport,
Wani irin kara Sabcer ya saka, ya kalleshi. '
"Sister ta iso?" - . Ibrahim ya. yi darin yace Aina
.fada maka you Will bé happy". WayyO Sister". ~
Tun kafinn Ibrahim ya karasa yin parking din
Motar Sabecr ya bude murfin Motar ya fita da
sauri ya nufi inda . zai sameta. Shima Ibrahim
bayan ya yi parking ya kulle Motar ya biyoshi a
baya, ya riskeshi a hanya. . ' to, "Mallam’ basu-
sauko..ba tukunna sarkin suuri. sai mun jira”. "
haka Sabccr ya 'dinga kaiwa da kawowa cikin
kosawa, ya yin da tunanin .deeda~“ya cika
zuciyarsa da kwakwalwarsa' ba,a jimaba jirgin ya
sauka Sabeer sai raba idanu yake‘ Can k0 ya
hangota, tsananin murna: ya .rufesu, ya sa‘ka
dariya mai hade dairin'ihu yana”kira Sister
OyoyO!! itama Adariyar take tsananin murnar
ganinsu, dariya,. "Sabeer. yake yace sistér 20 mu
je Mota, sai' mu yi magana a can hannunta yaja
suka bar gun, Ibrahim ne ya‘ “tsaya ya yi
(Cleaeing) din Kayansu sannan ya taho yana
kallonsu yana murmushi. koba komai Sabeer ya
dan sake" ‘ "A baya suka zauna tare, Ibrahim na
tuqawa yace Yau dai na zama Drive"; Suka‘ yi,
dariya. Sabccr dai kwanciya-ya yi, a Cinyar
farida..Sister nayi missing dinka, sai dai kin dawo
lokacin dana ke buqatarki".Sister zaki laimaka
min k0?" Ba ta. ankara. ba -sai ji tayi hawayensa
na jika‘ta. 'Ta' dago shi da sauri hankalinta a

tashe. '
"Saber menene?"
Bai iya cewa komai ba, sai kuka.
‘ Nan Suka hada 'ido da' Ibfahim ta Madubi
Ya' girgiza mata kai alamar 'kar ta yi masa wani tambaya.
hakan‘ yasa ta fara: lallashin Sabccr kamar wani_qaramin Yaro har suka iso gida. ' '
Daddy ya fito dakansa ya tari 'yarsa farida tare da Momi da sauran 'yan uwansu' yana- mai 'murnar ganin 'yarsa.
Sun kasance tare daSu Ibrahim ,da sauran family, Sun sha ‘hira sosai tare-da labarai da ya shafi Asibiti da' kuma sauran .harkokin rayuwa na‘yau da kullum.
. Sabeer dai 'na manne da"farida har
La'asar lis‘ Sannan suka Watse kowa ya kama ‘gabansa, lokacin Ibrahim ya samu damar kiran'deeda a Waya, duk’da tana . cikin fishi da shi amma‘ .tana "matukar son magana dashi don maganar Sabéer na cinta har yanzu
‘ibrahim ina‘son' magana da kai"..Ta fada cikin damuwa
‘ "Me yasa ka ke min -haka, baka daukar Wayata kuma ba ka kirani 'ba, mena yi maka Ibrahim?" ‘
Sory Deeda ina da abin yi da yawane ‘amma dai yanzu zaki iya samuna ‘a ,BIRNIN ' GAYU a Side dina saiki saiki fadamin abinda kikeson fadamin din
"ina nan zuwa‘ yanzu".‘ Ta fad‘a cikin zumudi'da murna. _ .
A cikin 'minti kadan ta shirya tana ‘ Allah-Allah ta isa. . Sabeer ,ya kasa zaune ya tashi ya nufi Bangéren su Deeda' amma har yanxu. ba tata dawoba; ” Inna ranta bai mata dadi ba
‘ mai yasa Deeda ke gudun Sabeer? ya Fita ya nemi' wani Wuri inda ba jama'a . 'ya je ya zauna ya hada kai da guiwa, duniyar tai masa zafi ya rasa me ya ke masa dadi, zuciyarsa ta dinga yi masa kuna
“ a wannan halin Farida ta sameshi. Sabccr ya dago kai'.
'"Meke faruWa’da kai haka?" , . ‘ Ya girgiza

mata‘kai"Ba komai". , ' ' Taja hannunsa. . TaShi Sabccr'm mu shiga ciki ka'fada min méye malsalar, ka Sister dinka‘?" cefa 'har daki suka shiga Ibrahim .na jinsu, ta ~dago kansa.‘ . ~
"Fada min me ne ne damuwarka?" .,
hawaye'ya'gangaeo masa ya‘ ce "Sister, “deeda Sister nayi kokarin in'mantata na kasa". -deeda" Farida ta maimaita' sunan _‘ Ta ‘ yi murmushi ta kalleshi ta -ce "Kyakkyawa ce?"Ya gir‘giza ma ta kai alam‘ar. a’a.‘ classy ce" Yasake girgiza mata kai. , , . ,Ta yi. masa kallon mamaki
" ya tsuke fuska'yace"No Sister, amma duk da hakan Sister, deeda ce rayuwata
Sister ki taimaka min tun jiya ban ganta ba.
duk da inason‘ ganinki da
dokin son ganinki amma da ki ka zo na kasa murna ‘ . na‘kasa control din 'kwakwalwata
Shiru tayi' tana ‘kallon yadda Sabccr ya yi nisa cikin soyayya, gaba daya ya canja mata kamar ba Sabccr din data sani ba
"Deeda"; Ta fada sunan a ranta
Ta mai da~ kallonta kan Ibrahiiri,_‘data lura
. shima yana cikin damuwa da matsala. Ta sake kallon ‘Sabeér. ‘ _in . Deeda ce damuwar Sabecr, to shi kuma Ibrahim fa? :sister Sahccr ya katse mata , tunani. "Siste zaki bani deeda‘?" Ta yi murmush. - . . ,"Saheer Deeda mutum ce ba Kaya ba ita keda ikon. bawa'kanta-abinda ta ga dama"
' ' "
tana 'kula da ni,‘ kayana, .Side dina, ta dafa min Abinci.
Sister har Karatu tana koya min, tare muke karatu a wurin Mallam. .
Sister ko a office ita ke,kula dani,-'.she take care of my .world everything; Sister- dole in so
.deeda.’ Sister Deeda abar‘ so ce.
Sister, kullum ina Cikin farir ciki bani, da matsala, (she made my: world beautiful) yanzu _ kuma ta gudu ta bar ni.‘ SiSter ya zan yi‘?" zata daWo Sabccr, kar ka damu, zanje inga Dccda, Zan fada mata irin sonda kanina ke mata, zan‘iya ka komai,‘ donka samu abinda ka keso,zaka sameta Na. gode Sister"; Ya fada cikin tsananin murna. '

Ta yi'masa murmushi. ~ "Kwanta' ka huta donka gaji da, yawa".; Nanta dinga, Ial'IaBashi tana kwantar masa da hankali har 'Bacci ya daukeshi, sannan ta fito daga dakin ta samu .Ibrahim a falo yana Waya, deeda ya ke ,fadawa'«inda ya 'ke ta sameshi. ' "Ibrahim". Takira sunansa. . '"
Ya juyo dasauri ya' nufota tare da batA kyakkyawar runguma ba tare da ya ce .komai ba' itama rungumeshi .tayir sOsai. na tsawon Iokaci sannan ya ce, "Yayata nayi ' mising dinki sosai'
' Ta' qara bashi kyakkyawan tace Ni kuma na yi 'missing din mijina sosai, 'sannan kanina". . Ya Yi murmughi 'yace."Nima na yi rashin' yayata- kuma matata. Baki san'irin rayuwar kewa da kadaicin da nayi ba tare da keba, 'baki san .yadda rayuwa tayi min wahala da? kunci a kwanakin nan ba, rashinki kusa dani ba qaramin wahalar dani yayiba tunda kika zo na ke son kebancewa dake in jiki ajikina amma jama'a sun hana' yanzu na'samu. Dan Gidan Sister yayi bacci'?" ' Murmushi ta yi tace 'Yanzu dai gani' kwance 'jikin kanina Mijina, gaya min dukkan matsalarka ina' tare'da kai yace
: abinda zan fada miki shine ina' sonki Yayata Dagake ba.wata,a zuciyar ,Ibrahim wani kyakkyawan kissing ta Kai masa sumba
' kafin tai sa,ar hada bakinta da nashi sukaji karan faduwar tire a tare suka juya don ganin mene ne.
Deeda ce tsaye a wurin ta zaro ido baki bude jikinta 'ya'.hau' rawa. Wayar hannunta ya fadi 'gumi Mai zafi ya_'dinga tsiyaya a fuskarta, numfashinta ya soma neman daukewa;
' .wayyohhhh Allah na ni deeda na shiga uku na Ialace
"Wai dama Ibrahim na da aurc, kuma dama farida yayarsa ita ce Matarsa'? Wayyo ni deeda dame zanji
Wani irin sonshi 'da tsananin kiShin Farida taji sun IulluBeta,~ Iokaci guda' taji wani abu ya tokare mata zuciya, idanunta suka saka sukai ja.jir
deeda Ibrahim-ya kirata. "

Hmmmmmmmmmmmmmmm
yau ya kamata ace na kammala muku book2
dinnan Amman me?kunqi ban hadin kai DA
ah shared a profile .
birnin gayu
chapter13
'Dedda". Ibrahim ya kirata. ' "Shigo mana'Da kyar
ta iya daga kafarta'ta shigo 'falon. ' Ya yi
murmushi ya ce'_"Kinjini Shiru k0? Ina 'basu'ga
zuwan Yayatane shi yasa muka kasa haduwa.
Wannan ita ce Yayata' farida kuma Matata rabin
rayuwata, Sister din Sabecr da ya keji da ita". da
kyar ta iya bude Baki na rawa tace"Ina yini'.'" '
Lafiya lau Deeda".ta fada hade da dariya. ~ Taja
hannunta tare da cewa, "zo in kalleki da kyau
Deedan Sabeer Nan ta sunkuyarda kai-
tana'kokarin hadiye kukan da ya'ke kokarin kufce
mata" ' farida tace"'Sabeer baisan kyau ba da na
tambayeshi kinada kyau yace a'a. Deeda na
naji labarinki 'a bakin Sabccr da Ibrahim, Ina yi
miki godiya gareki sosai kin kula da Sabéer da
Ibrahim duka, na ji labarin ma kece. (Suctarey)
dinsa kina taimaka masa SOsa'i.
- Maganar gaskiya'~ Sabccr.yana' matukar
buqatarki just imagine Likita da zama business
man kinga k0 hanya basu hada ba; amma sabo
da tsoron Asibiti da'Sabeer yake ya dage a
Kamfani, Thanks
deeda'ta sunkuyar da kai, hankalinta ma ya yi'
nisa, batajin mema take fadi
"Dccda". Ta dafata
Ta mike da sauri; tace Inna na' nemana". ' ' .
bata saurari 'me zata ceba ta fice
'Tana fita waje ko 'ta fashe da kuka mai
karfinngaske; Ibrahim yabita da kallo yaji tamkar
ya bita amma ya kasa faridan ta lura da halin'da
ya shiga, sai___'dai bata ce maSa kOmai ba
' A lOkacin 'Sabccr ya lura yace, "'Unclc ib kamar
muryar Deeda. naji yanzu'? Sister Deeda tazo nan
yanzu ne'?" . .
eh yanxu ta fita
Nan ya fita da' gudu ya bita yana juye-juye ko
zai ganta. . falon ya yi tsit, Ibrahim ya kalli farida

yayi murmushi "Ina; zuwa". . ' . "To sai ka dawo
Bari nima in shiga ciki in yi shirin Sallar
Magariba". _ ~ .- ' . .
Deeda -kuwa bayan fitarta ta nufi can wani _
'lungu 'inda ba _jama'a.ta durkusa 'a'wurin tana
wani 'irin kukan bakin'Ciki da Bacin rai da
karfinta kuwa, saboda Ibrahim ya mata» bazata;
tayi niSa cikin 'sonsa,. dukkan' wani- burinta,'
Mafarkinta 'da. tunaninta na Ibrahim,ne a
matsayin ABOKIN RAYUWARTA, mutumin da .bai
taba~sonta ba,' mutumin ,dabai ma san tana yi
ba,-yana~da' Matarsa da ya ke matukar so
batada waje 'a zuciyarsa ,da rayUWar Ibrahim. _'
"Wayyo Allah! _Y'a zan yi in' cire Ibrahim: a
zuciyata?" Deeda me ya.samek'i ki ke kuka'?'
Daman: nasan nan zan sameki
Dccda me ya sameki?" KI yi shiru '.don
Allah'
Saheer ne, shima ya durkusa a gabanta kamar
zai ma ta kuka, ganinta a wannan halin ya daga
masa hankali fiye da wanda ya ke Ciki.
"Deeda mene ne?" '
Nan yakai hannu zai share mata hawaye ta bige
hannunsa. . ka Kyaleni bana so Ta fada Cikin
daga murya'.
"Kuka na ke son yi,.kar ka yi kokarin tsai dani
. "Sorry". 'Ya fada cikin sanyin murya. - ;"'Yi
hakuri _ ba' Zan 'sake hanaki ba, kiyi' kukanki da
karfi tun da kina so ba zan hanaki va", Nan kuwa
_ta kara fashewa da kukan, kukan bakinciki,
kukan takaici -Yasata a gaba yana- kallo, ya rasa
ya zaiyi, kawai shima sai ya soma tayata kukan.
haushinsa ya kamata ta tashi zata tafi, ya Sha
gabanta. "Deeda na miki laifi ne.' . ' Nina saki
kukan Deeda'.' Ki' yi hakuri deeda I like u kukanki
na daga min hankali"'.— "Sabeer ka'kyaleni .da
a'bin da ke damuna", "'Meke damunki Deeda?" . .
' "Nayi rashine na yi rashin wan'da na keso, na
fahimci bai taba sonaba yana da Mata
yau na fahimci 'kuma bani da 'fili a zuciyarsa da
rayuwarsa, don haka na ke yiwa kaina kukan
halin da 'na tsinci 'kaina". .- ,Sabeer-ya kalleta. a
rude hankalinsa a tashe ya cé,' "Amma Deeda ai

ina
"sonki...
‘ deeda _na., fada miki kece rayuwata deeda Aure
na keSO mu yi har [htha S-na fada maka "Sabeer
bana sonka - Ta kalleshi "Sabccr ba ka fahimci
'me nake fada bane? Na rAsa’ wanda nake
s0,hakan ba ‘zai sa in auri wanda bana so ba.
Sabccr na fada maka ban taba
sonka ba, na fada maka tunda kuma yanzu ma
na maimaita. Ibrahim shi nakeso ba Sabeer ba".
Dccda kar ki yi' min haka Dccda me nene
ba kya so a halina in canja
Babu Sabccr, your are a changed Parson shi
ya sa nafada .maka' gaSkiya,‘bana so in
ya‘udareka.
don ina ganin girmanka da mutuncinka, amma
‘bana sonka, don haka‘ka kyaleni please na
rokeka
ka rabu dani bana sonka".
‘ ,tana gama fada ta- wuce zata karya kwana
kenn suka hade da"Ibrahim,»yaYin da Saheer‘ya
kasa koda
motsi, maganganunta sun tada’ masa hankali.
haka ya dinga jin sonta yanzu ya fara jinsa sabo
a ransa. Ibrahim ya tareta‘. ‘ ' ' ‘ "’Meye haka »
Deeda? Wannan wane ’irin magana naji kina
fadawa Sabeer
- Ya’ ma za a yi- kiyi tunanin haka ni’ 'dake? Kin
san tsakaninmu ,mutunci ne tsakaninmu, Likita ne
da marasa lafiya".
kwarai”. Ta amsa masa cikin’ takaici. . - 1 "Yama
za a yi na yi tunanin 'haka tsakaninmu k0? -' ‘
Saboda ni bani da Zuci'yar son ‘Namiji k0, sabo
da ni ba mutum me. rai bace
' ‘_ Lokacin da'na ke tare‘da kai. na ke yin duk
abin da kace baka tambaya me yasa na .keyi ba,
lokacin da na jure duk wahala da wulakanci sabo
da kai, duk baka tambaya me' yasa ba sai‘yanzu
da na ce ina Sonka za ,ka ce me ya sa‘? -
Ni zan tambayeka me yasa ka yi min haka Mai
yasa duk 'tsawon lokacinnan da’muka yi da kai
ba ka' tabaa fada min kana da Aure ba;? ‘
, ” Baka fadamin farida Yayar Saheer Matarka

bace meyasa kamin' haka?
Ka bari na zolayi kaina, na‘ yaudari kaina, na za ta kaima za ka soni, na dasawa zuciyata sonka, ya ka keson in yi Ibrahim?
Ta fashe‘da kuka. Ya ji tausayinta sosai, amma sai ya daure ya yi ta maza ya Bata rai ya ce, "Ni ban taBa kallonki da haka ko daukanki a haka ba, don haka ki yi saurin cireni a ranki"; ‘
Ya ja hannun Sabeer.
"Z0 mu tafi Sabecr";
Kuka ya ke, ya fada jikinsa.
- "Uncle 1B me ya sa.ba ta sona sai kai? Me yasa Uncle IB, ina son Deeda." ' , ’ "Na ji Sabecr, zo mu tafi a yanzu Deeda na cikin fishi ne in ta huce sai mu dawo mu yi magana a nutse. ’
"Ba sauran magana a tsakaninmu”. Ta fada cikiu tsiwa
"Kamar yadda kace in cireka a zuciyata, ka fadawa kaninka ya yi saurin cireni a nasa zuciyar tunda na rasa Ibrahim ba zan taBa auren wani ba, haka‘ba zan taBa sake‘ son wani ba, a rayu har abada a haka, dama can haka na ke rayuwa, zan koma inda na fito
Jin haka ya sa ya juyo ya kalleta ya ce "In zaki iya tunawa dama ba ni na kawoki BIRNIN GAYUBA
ba, Kaddara ce ta hadamu a Gidan nan, don haka kima kanki adalci..
Kiran sallah ya katse masa maganar, ya ja hannun Sabeer. -
'zo muje Masallaci". '
' Bai masa musu ba ya bishi, 'sai dai' ya juyo yana kallon Deeda tana tsaye .hawaye na zuba a idanunta, ya ji zuciyarsa kamar. wuta'
Sabee‘r ya dinga jin sabon sonta mai Karfi na shigarta Haka ya dinga yi ma ta wani mayataccen .KALLON so har suka bulle
.; MasallaCi suka wuce'kai tsayé'"suka bi Jam'i, ya yin da Deeda ta. koma ciki da tsananin' fishi da kunci da kuma Bacin' rai.
Bayan ta idar da sallar ta kife kan Sallaya tana wani irin kuka tana addu‘o'i tana neman dauki da saukin zuciya a wurin Ailah. '

Inna ne tazo ta eungumeta tana bata baki da‘
lallashi. ‘
Bayan Ishsha Ibrahim suka koma- ciki tare da
Sabeer yana, riqe da hannunsa. ‘
Farida ta‘taresu Cikin murmushi da dariyarta tace,
"Kun shigo? Yau namana girki da hannuna zamu
hadu mu ci kamar yadda muka saba". '
Gamin yanayin ,Sabeer ya sa ta fahimci .abin da
ke. faruWa, sai dai ,ba ta ce masa komai- ba, sai'
matsowa kusa da shi da ta yi ta ja hannunsa tare
da ja masa Kujera ta zaunar da shi’ta sa masa
Abinci.‘
"Sabeer yau Sister ta ma ka girki, fara ka fada
min ya kaji? Bari in‘ -je in kira Daddy yau tare za
mu hadu mu ci Abincin harda Momi'
Nan ta fice ta barsu; Ibrahim ya sa masa ido ya;
rasa ta ya zai bullo masa har yaga gara ya yi
kuka dayin magana ‘akan wannan shieun nasa,
Allah kadai ya san guguwar da ya binne a
zuciyarsa. ‘
Ya zura masa ido a ransa yace, "Sabeer ba ni da
abin da‘ zan maka yanzu sai. dai ka yiwa‘kanka.
Shigowar Daddy _da Momi ya katse masa tunani.
Wurin ya yi tsit kowa na cin Abinci. Dady
yayi dariya-yana yaba' Girkin, Farida,
‘qaran da Cokali‘da Plate din da Sabeer keyi ne
yaja hankalinsu gareshi. Abincin ya keci da sauri
yana kokuwa da Cokali da Plate din yana ci da
sauri tamkar wani zai Kwace 'mai Abincin.
_ Bai ankara. ba har Abin‘cin' ya kare, sai kai
Cokalin Baki ya yi yaji babu komai;-Ya mike da
sauri ya sake bude Kular Abin'cin ya sake
zubawa yana ta‘ci ba k0 sassauci.
Nan suka zuba mai ido .suna kallon ikon
'Allah
wannan ya kalli Wannan. Farida ne ta' yi- Karfin
hali‘ ta taso ta ‘zo‘ ta sa mai Ruwa _a Cup ta
mika masa, ya karBa yana sha da sauri' duk— ya
juyeshi a jikinsa, ya yi wurgi da ‘ Kofin yana
numfashi da Karfi tamkar wanda ya yi tsere.
Farida ta shafa kansa. - "
(Relax) Sabeer (Easy) daukeshi a; hankali,
kwantar da hankali"- H/

Kwantar da kansa ya, yi ‘a. jikinta, ya rikota
hawaye ya zubo masa
"Sister ya zan yi? Sister ya zanyi? Sister ina, son in fita daga halin da na shiga, .bana son za'ma cikin wannan hali Sister! Kirjina ciwo, zuciyata na zafi. Sister ki taimakeni".
' Daddy ya. mike hankalinsa a 'tashe. "Sabeer lafiyar ka? ‘ Me ke, faruWa, me ke damunka, me ‘kake
SO?" : ~
Nan ya mike da sauri ya nufi gun Mahaifinsa ' ya fada jikinsa yana kuka. "Daddy Deeda na ke so Daddy Deeda na ke so Daddy ka bani Deeda
‘ Ina son zama tare da ita, (I like her) Daddy ina son in Aureta. Daddy ka aura min Deeda".
Baban ya rungumeshi sosai zuciyarsa ya masa zafi ganin dansa cikin yanayin da bai taba ganinsa.ba
Momi ta mike cikin mamaki. ..
"Sabeer Deeda ka ke so?"
Ya girgiza mata kai.
"Deeda na keso, amma ba ta sona".
"What?" Daddy ya fada cikin zafin zuciya da bacin rai.
"Ba ta sonka, ita waye?"
Sabeer ya kalli Daddy.
"Kae ka yi mata tsawa in ka ma ta tsawa zata gudu ta barni, nima fada nake mata da tsawa shi yasa bata sona, zan je in roki Allah ya huci zuciyarta ya sa Deeda ta soni". .
‘ Da gudu ya bar Falon’ ya je ya yi Alwala yazi ya tada Sallah cikin nutsuwa da kaskantar da kai, cikin Sujudi ya dinga kuka yana Addu‘a yana kai kukansa gun Allah,.yana rokon-Allah ya bashi Dccda, . Dukkansu suka koma kallonsa ' Dr. Sulaiman ransa ya yi mammunan baci, . hankalinsa ya 'tashi,‘ bai taba ganin dansa a kwatankwacin wannan yanayi ba. . .Momi ita kanta sai da ta tausaya masa. -"Ibrahim". dr. Sulaiman ya kira‘shih Cikin babbar muryar yace‘, "Ina Deedan take? Ina son ganinta yanzu". - Ibrahim Zuciyarsa ta harba. Me Daddy zai yiwa Deeda? "Daddy bari in: kirata". "A'a". Ya tsai

dashi zan je da kaina". " Tare suka fafi duka
. ‘ ******
' ‘deeda na ;, kwance tana kuka sai ‘ hayanniyar jama‘a taji. ‘ . 'jikin Inna Mai fura ya hau rawa tana tunanin ‘lafiya kuwa, ganin
shi da kansa mai BIRNIN GAYU a gabanta, hakan ya firgitata. Mutumin da ba ta taba tunanin zata ganshi a gabanta ba, 'duk'da k0 tana cikin gidansa; bata da matsayin ganinsa.
zo Deeda Alhaji zai yi magan'a da ke. ' .
‘ momi ta fada lokacin data ke kokarinjawo. hannunta zuwa‘gaban‘Daddy;' " ‘Daddy ya kalleta ya ce "Kece deeda'?"
Ta girgiza masa kai alamar eh "Kece wacce ki ka kai ki ka isa ki Batawa dana rai‘? . Dana gudan zuciyata, gudan jinina da 'ni ban taba kuntala‘ masa ba sai ke"_' . Ya fada gami da nunata da yatsa cikin tsawa yace, "Ba a yi‘ wani'mahaluki 'da' zai kwana ya tashi ya ci ya sha ya tufata ya samu lafiya a BI'RNIN GAYU ba ya ce zai Wulakanta gudan dana. Ba ke a qasarnan baki daya . Ke ba ki isa’ba". . Tsawan da ya sake sai da ya gigitata ta rude . ta tsorata gaba daya ya cikamata ido. - Ya ci gaba da cewa, "Tun da na ke ban ga‘ dana ya S0 wani abu haka ba, ban taba ganin sa .cikin wannan hali ba, ban taba ganin ya so mallakar wani abu haka ba, ban taBa ganin (Desperation) a
tareda shi irin na yau ba. Sannan rana ta farko da ya so abu har cikin Zuciyarsa tsakani da Allah,"kuma bai nema da fada, tsaWa k0 karfi ba. Don haka Sabccr zai samu abinda yake.so k0 da kuwa kece ' - A kullum ina cikawa dana burinsa ina ba shi ‘ abin da, ya'nema." haka'kwanaki alkawari na ‘masa zan bashi duk abin da ya nema, don haka zan cika alkawarina, dan bawa Sabeer abin da ya keso, zan 'auraWa dana .abin, da .ya keso”. ‘ Cikin dakakkiyar murya .deeda ta kalleshi tace"Bana Son danka, don haka ba zan aureshi ‘ba, ni ~ba Kaya bace da za ka bawa danka, mutum ceni. mai rai ’mai Zuciya, ba yadda, za a yi in rayu'da' abin da bana so”,, Ba Daddy kadai ba, koWa ya yi mamakin kalamanta.

> ' Daddy ya kalleta, "Ke waye'? 'Yar Gidan uban waye? meye asalinki? -zuri'arki da har ki ka isa_'ki 'kalli tsabar idona ki fada min'haka?" Ya yi murmushi. Zan nuna miki isata zan aurawa dana ke. Yanzu na kara fahimtar me. ya Sa Sabeer ke sonki.
lallai zan nuna miki isata da' yadda zan bawa dana abin da yake so; ,za ki ga yadda zan mallakaWa Sabeer abin'daya keso Yanaa gama fadin hakan ya juya ya tafi Ya kira MOmi da Ibrahim yace su biyo shi yana son magana 'dasu-yanzu, 'sannan yace Farida'ta lallashi 'Sabeer ta'kwantar masa da hankali ta .fada masa gobe''babansa zai mallaka masa abin da yake .so." 'Duk suka amsa masa da, "To". Suka fice. ~ Ibrahim hankalinSa ya tashi, damuWa ta 'bayyana a fuskarsa. ~ '- " Bai' 'taBa zaton' Wannan alamanein zai 'kai' matsayin da ya kai a yanzu ba. - ~ Suna fita Deeda ta fashe'da'kuka. cikin kukan take cewA "Inna mu tafi mu bar Gidan nan. Inna mu koma '"Kauye!' Inna bana son BIRNIn 'Inna mu
. Kakar ta fashe da kuka.
V"Gaskiyarki Ddeda, mu, tafi ,; Wannan alamari yaban .tsoro; mutanennan za' su iya. yi... mana komai. Yanzun nan zamu bar'musu gidansu."'"
Abin da ba su sani ba, Daddy ya riga da ya bada ordar rufe kofofin BIRNIN GAYU gaba daya,
a sa guard ba mai shiga ba mai fita sai da saninsa. "
Haka suka 'dinga bin Kofofin BIRNIN GAYU amma ina ba hanyar fita, haka suka hakura suka dawo Duk da hakan Deeda ba ta' Karaya ba ta nemi Wayar Ibrahim da ya taimaka musu, amma ba hali sabo. da yana tare da Daddi.
. Sabeer " kuwa Wayarsa ba ta 'shiga haka suka' rungumi juna ita da Inna suna kuka. ' _
* **
a can cikin Gida kuwa Daddy 'ya sa . Momi' da Ibrahim gaba da tambayoyi
akan Deeda da asalinta da inda ta fito da yadda aka yi taxo BIRNIN GAYU. ' '
Komai da suka sani suka 'fada masa': A lokacin

ya yi, Waya ya hada Ibrahim tare da wasu mutane su‘ je Gidan Tabawa su dauketa a daren su je Kauyen su Deeda: a dauko masa ‘Mahaifinta da duk wasu danginta in akwai su a Kauyen.
Ibrahim dai badon ya so ba ya tafi, sai don‘ biyayya‘ da ladabi dabin umarni da ya ke
- Tabawa dai ta ga ikon' Allah, da daddaré ta ji tsayuwar motoci Jeep a Kofar Gidanta sun- 20 sun tattarata a Mota. . '
Ibrahim ya karasa ,gabanta ’ya mata bayani. ‘
"'Ikon Allah, Wani abu sai masu kudi :da .mulki ‘ '
Ta fada a ranta. V
*********
, alamarin Sabeer kuwa bai san meke faruwa ba. Farida, ta je ta sameshi amma bata fada masa komai ba taci gaba da bashi Baki da lallashi. _ ' .
Daga abin ya mintsineShi sai ya tashi ya yi ta. Sallah. ' Faruda_tasa masa ido'tana kallon ikon Allah.
'cikin ranta taji tana sOn Sabeer .ya
mallaki Deeda, ta ji tana Son ‘Deeda ta auri Sabccn ‘ ,-"Bana ganin damuwar‘. kowa sai ta‘ dan uwana. - '
Burina Sabeer ya ‘samu abin da yake So Sannan Deeda alkhairi ce ga rayuwar‘ Sabcer, ita ce Macen da zata iya kula da Sabeer
_ Mace ce kamila mai. nutsuwé Wacce abin duniya ba ya .gabanta, Mace ta'gari.
Haka nan za ta zamewa 'Ya'yan Sabeer. uwan ta gari wacce za ta haifar da al'umma na gari cikin tarbiyyarta.
A cikin Birnin gayu za ta kawo canjin rayuwa da tarbiya a BIRNIN GAYU. ' .
. "Ya ~Allah , ka. tabbatar da alkhairi
-*v* *v* *Q* '
washe gari da sassafe aka iso da
Mallam Audu da Matarsa da- wasu
tsirarun Danginsu da suka rage cikin BIRNIN KANO. , ‘
Sun saki baki suna kallon ikon Allah. .Cikin wani dankarérén Gida aka yi musu-Masauki, inda ba su taBa zato k0 ganinsu aciki ba a rayuwarsu;

' Wanka' suka yi aka basu » Sutura da kyakkyawar Karyawa.
Abinci iri-iri. Duk wannan 'hidimar' Ibrahim keyi dasu. . Bayan sun nUtsu sun kintsa Alhaji yasa aka kiran malam Audu dOn ganawa Ya kalli .Malam Audu yace ,"Na San dai baka sanni'ba, amma bazaka rasa jin su'nana'ba? Ba ka kuma ~San dalilin kiran da na maka ba? ', Naji labari baka da wata sana'a k0 Wani aiki sai na Zuma,'_shima' yanzu baka da halin yi, don 'haka nake son'maka Wani habban gata in bar kana so". " ' Mallam AudU'ya sunkuya jiki na rawa yace 'Alhaji ina godiya, ban san Wane irin godiya zan maka ba, mutumin da ke cikin wahala ai ba'zaiqi 'rayuwar dadi ba. ; ' " Alhaji ya yi murmushi yace da kyau Mallam Audu. Ka ga Wannan gidan da ka ke gani duk girmansa duk kyansa naka ne na mallaka maka, shi halak malak Ka yi rayuwarka da 'iyalinka har abada a~ 'cikinsa da'sauran 'yan uwanka. , Kuma. k0 mutuwa kayi sai dai Magadanka su gaji gidan; ' Sannan ga' tSabar .kudi zunzurutu har naira miliyan goma zan baka ka soma kasuwanci. ' sannan 'duk wani abu da ka kake bukata kazo wurina kai tsaye. ,
Malam Audu da ya ji numfashinsa na shirin tafiya don gigita ya ga kudin da- bai taBa ganin yawan su ba k0 a Mafarki, ga dankararen Gida"
Ya mussuke ido don ya' fahimci k0" dai Mafarki ya ke Ya kwantar da kai yana ta godiya shi. Sannan ya ce, "Wai Alhaji meye dalilin kyautar nan? Inba zaka damu ba". '
. Alhaji ya yi mirmushi ya ce, "Ka yi tambaya mai kyau, .akwai dalili kwarai
Ni dai dan kasuwa ne, bana yin abin da na san ba riba. ' ' '
Ba wani abu nakeso ba illa iyaka auren 'yarka deeda da dana Sabccr a yau Laraba din nan nake sonka bani. Ina fatan ka fahimci dalilin kyautar? '
'
Ni babban 'mutum ne mai kudi da suna, mai girma da 'mutunci. '
Don haka na yi' kokarin yi 'maka wannan kyautar

ne kar jama'a su fahimci halin-da Surukina ya ke ciki na talaUCi, kazanta da rashin ‘abin yi.
Kaya komai .gashi nan, daga yau ka yi 'sallama da lalauci". ‘ wohoho kudi kudi kudi masu gidan gidan rana
' Mallam Audu ya washe baki yace "oho! Ashe Deoda gidanka take Aiki?
Ai tana min aike nadan abin kashewa, yarinya 'yar albarka, ta dalilinta mun sami abin arziki. ' ,
' Allah Ya mata albarka, muna godiya Alhaji ko yanzu ka ke so sai a daura auren". '
Alhaji ya yi murmushin samun nasara sannan ya dubi Malam ' Audu ya ce "Amma fa akwai wala 'yar malsala kadan, ka yi kokarin fahimtar da 'yarka cewa ya zama dole ta auri dana, kuma ta sashi farinciki, idan ba haka ba zan kuntata rayuwarta da ma ku da na kakarta‘ gaba daya, gara ta yarda duka mu zauna cikin ,farinciki.
' Ya mike, "dan tafia zan sa a kawo maka su ka yi saurin fahimtar dasu
"To Alhaji an yi an gama. Ai wannan mai sauki ne yadda ka ce haka za a yi". '
"Da kyau! Ni na tafi
Har bakin Mota Mallam Audu ya bishi yana godiya. kamar zai masa sujjada
Ya dawo ya dinga murna yana washe baki yana zaga Gidan ya kasa yardarwa‘ kansa cewa wannan Gidansa ne.
"Ashe Deeda alkhairi ce agareshi ya koreta ya wulakantata? , . - .- Shin ta ya ma zai soma fuskantarta‘?_Taya zai soma sata har ta yarda da ‘auren? ‘ To amma fa ba'zai‘ yarda ya rasa wannan. dukiyar‘abanza' ba."Ni Ubanta ne, kuma ya zama dole ta yi abin. dana keso k0 tana s0 k0 ba ta so." -
Daddy na komawa gida ya‘ cema Ibrahim yaje .ya dauko Deeda da Kakarta ya kai ta can wurin Mahaifinta, ya kuma tabbatar da tsaro' a Gidan don kar su gudu. ‘"To Daddy". Ya_fada Cikin ’ladabi,’ ya ‘nufi side din su Deeda. - Lokacin ' da. ta 'ganshi ta yi tunanin taimakonsu ya zo yi, don haka bata musa. masa ba suka shiga motar ita da Inna suka tafi ' ' ' Tun da suka shiga

Motar kuka take, idonta ya kumbura luhu-luhu
wanda hakan ba karamin kona zuciyar Ibrahim ya
yi ba. , ' Ya ji wani .irin bakinciki da tsanar kansa
ya kamashi. Ya ji kamar ya sa hannu aka ya yi
ihu.
cikin fishi da Zafin rai tace"gidan Tabawa za ka
kaimu daga‘ nan zamu shirya mu wuce Kauye".
Ya daure fuska ya kau da kai ya
ce Ba umarninki nakebi ba, don haka zan kai
‘ki‘inda aka
umarcenida in kaiki." ' '- . "Me ka ke nufi, ina
zaka kaimu?" . ihu tasa masa amma kO kulata
bai' yiba. Inna ta sa hannu la rufe mata Baki
tace, "Deeda rufe bakinki karki‘ Bata muryarki da
hawayenki a banza, tunjiya kuka ki ke lamarin
nan ya wuce saninki da tunaninki; ' . ‘
’ Yanzu Ibrahim ihunki k0 hawayenki ba zai
tabashi ba, yanzu‘ Kaninsa da Uban gidansa
sune'kawai,a‘ gabansa".
Dole ta haqura suka iso 'gidan, ya shiga 'har ciki
ya bude musu kofa suka fita ya ja motarsa ya
tafi ba tare da ya sake k0 da kallonsu ba. '
Ya kara jan kunnen Maigadin gidan akan kar ya
yarda_ ya barsu su fita.
Nan Deeda da‘Inna suka tsaya ‘juye-juye suna
kallon ikon Allah, ba su san inda su‘ke~ ba, ba
kuma Susan me yake faruWa ba. ‘
"Nan a ina muke Inna?" Deeda ta fada cikin kuka
cikin gidan ubanki kike sukaji an fada cikin firgici
DA tashin dankali daga ita har Inna Mai fura suka
zuyo don tabbatarwa DA tantance muryar DA
sukaji shin gaskia ne kokuwa gizo kunnuwan
nasu ke musu
Hmmmmmmmmmm
a zallah shared a profile .
birnin. gayu
chapter14
deeda la kalleshi cikin mamaki.
"baba" Ta fada cikin mamaki.
Inna ko kasa magana ta.yi tsabar kaduwa. Du
kyar ta ce,‘ "Wai meke faruWa ne, me ka keyi
yaushe ka shigo Kano kuma‘?
"Ku iso ciki zan mukubayani

Kamar za su shiga kamar bazasu shiga ba, haka suka shiga. .
Nan ya fara, yi musu bayani, ya~ kare da kwantar da murya yana neman gafara da rokon su yafe masa kan abin da ya musu tun shekaru masu. tsawo da suka shige
Anan fa idon Inna ya kada,ta hau bala'i ta inda take shiga ba ta nan take. fita ba.
Ta zageshi tas taci masa mutunCi tace yanzu ma nadamar ba har zuci bane 'ganin abin duniya- ne yasa ya nemeta. '
Ta ce, "Kuma duk bala'insa Deeda ba zata auri wanda' bata soba". ‘ ‘
Nan fa eikici ya kaure yace, "inba ta auri Sabeer ta dadi ba za ta aureshi' dan dole, gara ma su‘
sani aure daram'ba fa shi". . ‘
Ran Inna ya" Baci, 'suka dinga sa'insa ya’yin da aka bar Deeda da kuka kamar ranta zai fita'
"Wannan wane irin tashin hankali ne?
' Sabeer Ubansa ya saya masa farin cikinsa, ya yin da ita nata Uban ya siyar da na ta farin‘ cikin.‘
’ Wannan shi ne. abin da ya ke faruwa a "rayuwarmu na yau, a .duniya yanzu masu kudi da Mulki suna amfani da talaucinmu da rashinmu suna sayan abin da sukc so wurin‘ Talakawa. ' .
Ta Tashi tasa kuka. ‘ " ' "Shi' kenan Alhaji ya gama da ita, ya gama
’nasara Akanta tun da ya hadata da Mahaifinta".
. _‘ "Inna ki ‘rabu da shi, ba yadda na iya". Deeda ta fada Cikin muryar kuka. .deeda ba zan bari ya yi miki auren dole-ba akan .abin duniya".
‘ "Idan ki ka nemi _shiga tsakanina da 'yata k0 hanata abin. da na keso ta yi Zan rabakida ita, zan kwace'yata". Mallam Audu ‘ya fada cikin halin ko in kula. ' .. '
Wanda wannan. maganar ya .Sa.Inna ,tace zata tafi ta bar masa 'yarSa.
Deedan ne ta durkusa har 'kasa tana ROkona akan kar ta tafi ta barta. '
’ Ba yadda ta iya don koba komai, bazata iya lafiya ta kyaleta ba, haka' suka shige cikin gidan

zuciyarsu cike da baqin ciki da’.baci.rai.
. Mallam Audu yayi dariyar "samun nasara ’gami dasa mata albarka. -shikam rayuwa sabuwa a wajensa
**** ** .
'bayan Sallar azahar Mahaifin Sabeer da abokansa sun hadu yaje ya kai masa manyan Kaya _- .masu kyau'da tsadar gaske; .ya bashi yace yasa
’ . Shi ’da Ibrahim suka. taimaka‘ .masa ya-shirya, ya yi matukar kyau; dama can shi mai .kyau ne
’ Sabeer ya ‘fito Ango 'sak Mahaifinsa ya masa albishir dacewa yau daurin aurensa Deeda ta“ amince da aurensa. ‘
Wani irin‘ ihun murna yasa Ya rungume Ubansa cikin tsananin farinci’ki.
"Na gOde daddy thanks YOU So much ka min “albiShir din da baka taba minba a duniYa da 'gudu' ya rungUme yayarsa .yana .murna- ’ «sister Deeda ta amince da auréna”. . " Ya fada kan Ibrahim
_ “Uncle iB'Deeda tana-‘sona yanzu ta amince da aurena. 'Yanzu ni Deeda keso Saboda ta. san nafi kowa Sonta, Allah: Ya amsa‘ Addu’ata Allah- na gode maka
hawayen ‘farin ciki ne ‘ya zubo ma Mahaifinsa ganin farinciki da kwanciyar hankali ~a tare da Sabeer‘ yafi kOmai‘ dadi a wurinSa.
'Ya kamo hannunSa
zo muje inda za ka ga cikar bUrinka".
Mota daya suka zauna tare da Baban naSa, suna baya Ibrahin na'gaba, Driver na tukawa. '
Sabeer ne keta Waya yana fadawa 'Abokansa ’yan. uwansa na‘wurin Uwa da Uba, har. ya .rasa' inda zai'sa kansa don murna, sai kwanciya? yayi a jikin Uban yana daria yana masa godiya.
Ba Shi “da ‘wani buri k0 ab‘
in da .ya keSo illa ya ganshi a jikin Deeda, ya ganshi tare da ila.
Karfe uku dai-dai aka daura auren Dccda a cikin gidangsu Wanda dr. Sulaiman- ya'. bawa

Mahaifinta, kasancewar ba ayi shiri, ba mutane ba yawa Abokan kasuwancinsa. da wasu kusoshin Gwamnati da ‘yan uwansa na kusane kawai
Bangaren Dccda kuwa, Mahaifintane kawai~ sai wasu 'yan uwansa guda biyu suka shaida daurin auren Dccda da Sabccr.
Jama'a da dama suna mamaki, sai dai basu- da damar magana, abin ka da masu Mulki da Naira, kafin ka ankara manema Labarai sun cika kofar gidan kowa da irin famhimtarsa da fatan alkhairi .da taya murna da suke musu. _ .
haka Sabccr ya dinga jin wani irin farin ciki tamkar ya .mallaki duniya da’ abin da ke cikinta,- gaba . kana ganinsa ,ka san yana cikin tsananin farinciki da jin dadi
Nan ya hadu dasu Nura da Salim suna. ta masa tsiya sabo da tuna yadda suka hadu da Dccda da irin tsanar daya mata ada.
Ya yi murmushi
yau zan ga Dccda a matsayin Matata: Shin taya ma fara zuwa wajenla? :
Me zan fara ce mata? Kuka zany‘i k0 dariya‘?’ " . Suka kwashe da dariya.
Nura ya ce "Runguméta zakayi tun da yanzu Matarka ce" .
haka sukai ta wasa da dariya, ya yin da Alhaji ya-kasa daga idonsa akan dansa ganin ,yadda ya ke,tsananin mamaki, dun haka ya‘ yi niyyar‘kara masa akan‘wanda ya‘ ke ' ' .
Sai da Sukayi sallar la'asar sannan jama'a suka watse su kuma suka nufi Birnin Gayu,‘ inda.
Alhaji ya cewa Sabeer‘kae ya damu, zai.samu Deedansa a gidansa da ya shirya’muSu a nan cikin Bienin Gayu; , ' ‘ ' '
Gida ya cika da 'yan'Uwan dr Sulaiman anata taya Sabeer: murna‘yayinda wasu ke mamakin‘ aurensa 'lokaci‘ guda, da irin tsananin ‘son da ya‘ke yiwa matar‘ wanda har ya kasa boye.shi ya fito karara a fuskarsa. ' _ V
‘ farida ce ta nufi gidansu Dccda kamar yadda Daddy ya ,umarce ta, taje ta. shirya Dccda tayi kyau fiye da ko wacce amaryah

Tare da masu kwalliya da kuma dressing ta tadi Inna ta tarbesu ba yabo ba fallasa, duk da Dccda batason .auren. a zuciyarta, taji dadin ganin ranar daurin auren Dccda, wanda 'shine burinta a zahiri‘.
' Aurcn Deeda’yaxo, "abazatar da batai tsammanintaba'tun kafin a daura auren Deeda ‘ke kuka har aka gama daurin auren.
Inna keta faman yimata nasiha da nuna mata‘
. ya "zama’dole ta dau kaddara ta rungumi mijinta hannu bibbiyu, ta rungumi aurenta, ta yi :sa’ar mijin dake matukar sonta
Ta fashe da kuka’ tana'fadin "Inna ya za,ai na Iya zaman aure DA wanda banaso
A wannan hali farida ta'shigo ta same su, ta fahimci halin da Dccda ke ciki, kuma abin da- ya faru ba mai sauki'ne a gare taba',‘amma sai ta daure taci‘ gaba da yin abin da ya kawo ta, tamkar- ba ta san meke faruwa ba ’ .
‘gyara saka yiwa'deeda sosai, tun daga kan Jiki, gashi, har Sutura zuwa Takalma‘
Ta fito marya sak Ta yi wani irin haske da kyau,’ duk da k0 Fuskarta ba a shafa'mata komai ba, saboda hawaye dake zuba mata "
Nan Farida ta sallame su, sannan taja ta gefe guda cikin sanyin murya ta dinga ba ta haquri da nuna mata cewa, ta san ba ai mata dai-dai ba.
Ta kalle ta da kyau taga irin kukan da take, "Na‘ fahimci irin halin da kike ciki deeda,_na san ba a miki adalci ba_, amma Dccda abin da ya faru ya faru, ba mai canja shi. ' , ,
Deeda na ' san bakya' son 'Sabeer, amma Sabeee na sonki tsakani da Allah da zuciya daya he is innocent, ba shi da laifi, abin daya faru Daddy ne ya miki, Sébeer bai‘ San dole aka miki ba
. halayyar Sabeer na san za su dame: ,ki‘, litinannéne a kan abin da yake so. ‘ '
Dccda ba Ashi‘da laili, haka ya' girma ya' taso, « bai san'ya‘ nemi abu 'ya rasa ba, ’bai san wahalar” neman abu ba. .
Saboda ni Daddy da Ibrahim muna nema 'masa duk abin da yakeso, ’kece abu na farko da ya nema 'bai. samu a dadi ba. ‘

Deeda dan Allah ki kula da Sabccr, karki hUkuta shi a kan laifin da banasa ba,na san na zama mai-son kai, ~ba' yadda zan yi Deeda, sabccr shine rayuwarmu, farin cikin mu— ni da Daddy da sauran family dinmu. Ya yin da ke kece rayuwar Sabeer- . '"
Dccda' ta dago jajayen idanunta ta kalle ta, tace "Ni kuma na wa rayuwar fa? ' . Ya ki'
keso in yi da 'shi? Ya kuke so in yi da na wa rayuwar da farin cikina'?(I'am not that great) da 'zan sadaukar da rayuwata na'ba da farin cikina. akan naku in tambayeki
Zaki iya bani Mijinki, ' za ki iya bani Ibrahim?" ' ' falida ta zaro idanu tana kallonta.
' "bani amsa".
Rana ta farko kenan 'da Farida ta nemi amsar wani abu da ta rasa. 'hankalinta ya tashi fiye dana da
Ta kau da kai tace, Lokaci yayi da zamu wuce, na 'lura. hawayen- idonki sun daina zuba, idonki ya bushe don haka zan gyara miki fuska mu wuce" ' ' .
"Gyara mu wuce kun. 'riga da kun busar min da'hawayena Idona daga yau, daga'yanzun nan ba za ki. sake ganin hawaye a idon Dccda ba
_ Ku shirya' zubda hawayenku dukkanku ~kamar yadda ku ka sani' zubda' hawaye, yanzu lokacinku ne, nawa ya wuce za ku 'ga ,yadda xan sa ku zubda hawaye zakuga yadda_ zan kuntata rayuwar wanda- ya kuntata rayuwata
Yi min kwalliya da kyau Sister'mu wuce Birnin gayu, ina matukar sauri da zumudin ganin Mijina Sabccr". '
Kalaman Dccda suka sa jikin Farida ya soma bari, kamanninta sun razanata, yanayin Dccda ya bata tsoro. '
Cikin sanyin jiki da tunani ta karaSa ma ta gyaran suka tafi hankalin farida a tashe, ya yin~ da inna mai fura tayi kuka, ta yi- kuka har ta gode Allah.
Ta bi Dccda da addu'a'da fatan alkhairi, ya yin da tayi niyyar komawa Kauye'washe gari.
Kai tsaye suka wuce gidan da Daddy ya' shiryawa

saber a BIRNIN GAYU,‘gidan da babu irinsa' kaf
BIRNIN GAYU.
' faridan tayi mata rakiya bar cikin daki sannan ta
filo, k0 sallamar kirki ba su yi ba. ‘
Deeda ta tsaya tana kallon tsarin gidan da dakin
da irin dukiyar da_ aka kashewa' gidan da yadda
aka tsarashi very classic.
Nan ta kifa kai ta fara tunani. . .
Bayan Issha,i Daddy da kansa ya jaWO
Sabccr ya rakoshi har kofar gidansa, farida tana
son
yi maSa magana amma ba hali sabo da yadda ta
ga yana tsananin muena da dokin zuwa ya ga
Dccda.
Ciki ta koma tana neman Ibrahim don fada: masa
abin da ya faru, amma ta nemeshi ta'rasa a
Gidan. '
Kofar Gidan Sabeer, Daddy ya kalleshi ya ce, "Ga
gidanka Sabccr, ga Dccdanka, ga farincikinka goto
ur happyness
Sabccr ya rungume Daddy yana dariya. "Na gude
Daddy, Allah Ya barni da kai Daddy".
"Amin". Daddy ya fada yana dariya.
Yace "Jeka (g0 and injouy ur self
Nan Sabccr. ya sakeshi ya yi ciki da gudu.
Daddyn ya bi shi da kallo yana dariya.
A lokacin yaji kewar Mahaifiyar Sabccr ya ce
"Allah Yaji kanki Fatima."
Nan ya juya ya tafi yana jin wani 'irin nutsuwa
da kwanciyar hankali ya bawa Sabccr abin da
ya'keso‘ .
*v* *9* *9*
tun daga falo yaji wani irin kamshi‘mai dadin
gaske mai tada hankali da kashe
'ciki Tafiya yake yana lumshe ido yana jin son
Dccda a ransa. .
Kai 'tsaye.ya wuce. dakinda ya san zai sameta.
" . " Can koya hangota a tsakiyar Gado tana
zaune Deeda ya kira sunanta cikin rudani da
SHAUKTN SO. ‘ ‘
Ta dago kai ta kalleshi. ‘Ido ya sama ta ya ga
tayi masa wani .irin kyau da kWarjini ya kara jin
ta shiga ransa ya Kara jin wani irin sonta na

shigarsa yana tsumashi.
Da .gudu ya isa gareta ya fada jikinta, yana" hawayen farinciki yana shaKar Kamshinta yana jin sonta na‘taBa ruhinsa, ya‘ dinga ji tana taBa masa ' zuciya da sonta da kaunarta;
,Deeda' ina sonki? Deeda kece rayuwata": ‘ Ya fada cikin. murya kasaskasa
Ya kai Bakinsa dab da Kunnenta yana fada ma ta Maganganu masu' ratsa zuciya da kashe jiki yana sauke numfashi a ‘hankali.
Ya sumbaceta a Kunne. Tsigar jikinta taji yana tashi, kamshin Turarensa mai Ramshi da dadin tsiya ya soma kashe mata jiki.
Bata ankara ba taji yana shafarta yayi kokarin kai Bakinsa'kan nata,_ a take taji wani hanzari ya Zo mata,ta tureshi da'Karfi ta mike.
Ya tashi a rude hankalinsa a tashe kamar zaiyi kuka yace menene meya faru deeda?"
tace"Bana‘son abin da ka kemin". Ta fada cikin Bacin rai
.Bana son kana taBa min jiki' "Deéda yanzu munyi aure, ba kamar 'da ba Deeda'ke, Matata ce"; ' .. , Ta kalleshi ta yi' fnurmushin takaici tace"Ni Matarka ce, amma bana sonka kana ji k0?" , i . "Please Dceda, karki yi min haka Deeda! Kece rayuwata Idan' ba kya‘ son' in taBa ki ba‘ zan sake ba I Promise ba zan sake ba, kar kice ba kyaa sona"Gaba daya ya‘ rude ya rikice. 'kada ki~tafi ki barni".
Tausayinsa_ta ji sosai,har taji ba zata Iya aiwatar DA niyyarta akansa ba
Ta kalleshi lokaci 'gUda har fuskarsa tayi ja, Ta jawo hannunsa.
"zo :Sabéer zoka. kwanta". ‘
Nan ta dora kansa akan Cinyarta tana shafar gashinsa, ya yin da'ya damke (daya hannunta ya hada da nasa ya manna a fuskarsa. '
Tausayin‘sa taji kamar ta masa kuka, a hakan‘ har Bacci mai nauyi' ya daukeshi tana kallonsa tana tunani. '
‘ *v* *v* *v* '
bayan Farida ta gama duba duk inda ta take tsammani-sai dabara ta fado mata, da sauri ta

nufi Side dinsa‘ Anan ta yi ' sa'ar samunsa yana kwance ya ‘
dukunkune’ guei' guda yana wani irin kuka mai tada hankali.
A rude ta isa gareShi.
"Ibrahim!
Ta fashe da kuka ta dafashi. Ya juyo da sauri, ya rungumeta. .
"Ibrahim yaushe ka fara boye min hawayenka? Yuushe muka' fara haka da kai‘?" ‘
‘ “Bai ce mata komai ba, sai dai ta fahimci komai ta ce, ."Na gane Ibrahim, .na zama .mai son' kai akan Sabeer. '
Ka san najima .ina‘addu'ar“ Allah ‘Ya kawo Yarinyarda zaka so‘, ban taBa zata abin zai zo a haka ba, na so kwarai kafin inbar duniya in ga ka samu yarinyar da ka ke 'so'ka aura";
.. Ya kankameta ' gami ~da cewa,'; "Ya isa Yayata Kin san inasonki, kuma ban taba yarda wai. don bakida lafiya‘, za kira‘su ki barba, ai-rayuwa' a hannun Allah ya ke ‘duk da kina _da kansa ban taBa'kawo miki mutuwa ba,‘ na san jinyar da ki ka tsaya ki kayi _a Canada kin samu 'lafiya,‘ na ‘san- ‘zamu rayu cikin farinciki, yayata ban taBa‘tunanin dan kin girmeni da shekaru‘uku zan sowata ,wai in .Aure ta don kin girmeni ba Farida, ina sonki amma abin‘ da ya faru ban s0 ya'faru 'ba, ban san‘ yaushe son Deeda ya shigeni ba, ban San 'yaUShe na fara sonta ba, ta zo cikin rayuwata-tamin baZata;
ba zan -iya Avoiding din ‘soyayyarta. ba, ‘ban san yaushe hakan ya faru ba, na san na fara Santa tun kafin'Sabeer' ya soma sonta,amm dana fahimci 'yana Sonta 'na. danne ‘zuciyata na Boye soyayyarta na yi kokarin .mantawa da ita da _soyayyarta; _na yi kokarin‘Boy m'iki da Boyewa kaina, amma yau na kasa
,da IdAnuwanta masu cike da‘ dimbin so da kauna, idanuwanta masu cike da tambaya da tsana a gareni suna bina sun hanani sakat
Yayata zuciyata .ta cika da nauyin sonta da nauyin laifin da nayi mata da nauyin rashin kunyar‘ son-Matar-kanina

Yayata ya .zan'yi in rayu da wannan'nauyin a kaina kayi kuka Ibrahim Ta fada cikin muryar kuka
"Kayi kuka Ibrahim ba zan hanaka ba. Ka yi kuka nima zan tayaka
' Nan suka rungume .juna suna wani 'irin kukan bakinciki da tashin hankali. ' ‘
tun yana jin motsin Farida har yaji shiru,ya dago kai da sauri. '
farida' Ya fada da karfi yana girgizata. Ya daga' hannunta gami da gwadawa yaji. Sakin hannun yayi hankalinsa ya yi mummunan _tashi; "Ya kira Sunanta da karfi faridaaaaaaaaa!!!" . ya rude ya fila hayyacinsa daga karshe ya fadi Sumamme deeda k0 data samu Sabccr ya yi Bacci a hankali ta zame jikinta ta' sulale ta~ bar 'Sabccr din, ta sauko falon kasa ta dauki'wata takarda ta masa guntuwar wasika ta ajiye masa a inda zai gani. ‘
_ ‘ A Daren ta sulale tabar'BIRNIN GAYU!
Ina ta tafi?yaya sabeer zaiyi idan ya tashi bai gantabA? shin meke faruwa DA Farida DA Ibrahim ne?yaya zasu kare DA wannan cakudaddiy kuma rudaddiyar DANGANTAKA?
mu hadu a BIRNIN GAYU BOO3
hared a profile .
birnin gayu
chapter15
sassanyar iskar asuba mai Kunshe da ni'ima tare da tarin
‘ ' albarka, shi ya doki fuskar Farida, hakan yasa ta ja dogon numfashi tare da motsawa, ta dinga kokarin bude idanunta a hankali. Ta yi tsawon .minti daya a haka kafin ta fara fahimtar inda take da ‘halin da suke ciki. -
A nutse ta juya ta mai da kallon ta kan Ibrahim da baisan inda yakeba, tuni abinda ya faru a daren jiya ya dawo mata. Nan ta yunkura cikin Karfin hali ta mike duk da ba ta jin karfin jikinta, haka ta yi kokarin takawa zuwa ga' 'window', iskar damina hade da yayyafi ya daki fuskar ta. Hakan ba qaramin dadi ya yi mata ba, nan ta yi Kokarin shakar iskar asubar gami da ware hannayenta yana ratsa ta. Hakan yasa ta ji ta

samu karfin jikinta da kuma lafiyar jikinta fiye da da.
Bimin Gayu-3________Sa'adatu Waziri Gombe '
Ruwan sama ne ya sauko da karfi, ta miKa hannayen ta duka ta tari ruwan, sannan ta juya ta nufl gun Ibrahim dake kwance, ta zura masa ido tana-kokarin tantance wanna hali yake? Suma ne k0 barci?
A take ta shafe mai fuska da ruwan da ke hannunta, .hakan yasa ya- motsa tare da yatsina fuska yana kokarin bude ido. Ganin haka ya sa Farida ta saki murmushi.
Lokacin da ya bude ido ya ganta gabansa, ya yi zumbur zai mike tare da kiran sunanta, ta yi saurin mai da shi, ta kalle shi ta fadada murmushinta gami da fadin
"(Welcome back)".
Shi dai kallonta kawai yake, ta ci gaba da magana. . . -
"Ashe dai da gaske .ne likitoci ba, sa iya ta'bukawa matan su, iyayen su, k0, wasu mutane mafi kusanci da su komai? Yau na gani akan mijina.
Lokacin da nayi dogon suma duk da ka san me zaka yi ka farfado da ni amma
Bimin Gayu-3 Sa'ad'atu Waziri Gombe _ ba ka iya kayi ba, sai tsabar rudewa Ashe kana ' sona' Sosai' haka?
Gashi dai' kaga. Allah Ya taimakeni 'na farfado' dai kaina har 'na farfado da kai.' ,
- to' dai ina'so ka fadamin da kai da ka ganni- cikin yanaYi- na ciwo ka' rude, ka tsorata, ka' rasa ~abinyi saboda' kana tunanin "wani "abu mUmmuna zai' faru dani. Da kuma'ni'da na ganka'a 'sume, na nutSu nayi'maka" abinda' ya f1 dacewa cikin nutSuwa, na- dake don kar wani abu mummuna ~ya faru . da kai. Wa ya fi wani son dan uwansa ni da kai?"
. Ta karasa'maganar 'da dariYa'. . '
Ibrahim ya yi. saurin rungumé ta sosai» a jikinsa, yace. ' ' _ '
A ,a Yayata, ' wannan lokaci da yanayi 'kina maganar Wasa? Kin san tashin hankalin 'da na'

tsinci, kaina jiya? Na zata,,,,,,
' "Ba abinda zai, faru Ibrahim,. Ta katSe ' shi
"Da' saura na Ibrahim, ina qoKarin
Bimin Gayu-3 ,,,,Sa'adatu Waziri Gombe 'shawo
kan lamarin nan. Duk' tsaWOn lokacin da na
sadaukar ina, rayuwa ba kai,;"saboda Kokarin
neman' magani da lafiya ta ba zai, tafi a banza
ba. Ina addu'a, kana min addU,a jama'a da nake
tare da su Wanda suka'san me nake ciki suna
min maddu'a. Ibrahim Allah; zai bani lafiya,' ina
'Kokari (I am fighting 1 saboda ina. son! in samu
lafiya; in rayu da' mijina, Kanina Ibrahim, kamar
'kowaccé mace _da ke da aure a gidanta. _ , . Ina
so in rayu da Sabeer dina, Daddy
sauran' 'yan' uwa. Ina. son kaWo gyara a
rayuwar mu da BIRNIN GAYU...''..
Ta Karashe maganarda kuka. " , _Tace, "Kanina,
ina son yin abuda' yawa.
"Za kiyi Yayata".
Ya fada-cikin sanyin murya tare da tausayaWa
halin da take ciki.
"In'sha . Allah Yayata, da yardar Ubangiji 'dukkan,
wani burinki zai cika. Ciwo ba shi ne mutuwa ba.
kuma wannan
Bimin Gayu—3___.______Sa"adatu Waziri Gombe
kanin naki zai kasance tare da. Yayarsa har
tsUfa, har mutuwa Insha Allah".
Nan ya" mikar da'ita' gami da kwantar da ita a
kan gado ya gyara mata kwanciya.
' "Kina-bukatar hutu".
Nan ya Wuce, ya. dauko magungunanta; ya bata.
(juice) ta sha, sannan ya; bata magani, ya 'sa ta
a gaba yana mata murmushi tare da shafa kanta
yana kara fada mata irin Kaunar da yake mata,
hade'da kalamai masu kwantar da hankali da
karfafa mata.- gwiwa har bacci'ya soma
daukanta. Ta bude ido' kadan' tana kallonsa-
dishi-dishi » saboda . magun'gunan' da tasha,
masu. Karfi ne, Cikin muryar bacCi ta ce
,"'Kanina,. a duk ' lokacin da. na ga wannan
fuskar taka da wannan murmushin naka,nakan
manta 'dukkan'Wani Bacin' ,-rai" da' KunCin
rayuwa. Murmushiin ka ka'dai, 'ya ishe ni~

dukkan tsawon‘ .rayuwa-(you are' the best
husband 'ever)"-
’ Haka ta. dinga-surutai shi kuma yana
Bimin Gayu-3/////Sa'adatu waziri gombe kallonta
yana mata murmushin da take so din har bacci
mai nauyin gaske ya dauke ta Ya lullube ta, ya
mike yana kaiwa da kawowa, damuwar sa da
kuncin sa suka dawo masa sabo, ya rasa me ke
masa dadi Kowanne motsi ita yake ji da gani, tare
da‘ Kaunar sonta mai zafin gaske ke kona masa
ilahirin jikinsa da zuciyarsa.. ,
"Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un! Deeda ta yi
aure, matar wani Ce amma na kasa cire ta a
zuciya ta, sai ma abinda ya karu
"Ibrahim, me ke damun ka? Deeda matar Sabeer
ce. kanin ka, dan karamin kanin ka da ka raina
kamar danka, cikin so da Kauna tare da'
shakuwa, kanin matar ka', wacce ta baka dukkan
wani Kauna da kulawa lokacin da ba ka da me
maka duk da Karancin shekarun ta. Tun kuna
yara ta koyi halin girma, saboda maraici. Duk
yarintarta ta kare a kula da kai, a lokacin da ita
kanta take bukatar a kula da ita. kafin mahaifiyar
Birnin Gayu-3 ’ Sa’adatu Waziri Gombe Sabeer
tazo ta'bamu-soyayyar uwa, tamkar ita ta haife
mu". . v ‘ ‘
"Yayata tayi. 'fada da 'yan uwanta, ta -- samu
saBani da:mahaifinta‘saboda ta ce zata aure ni,
duk da nima ina son Farida, don-ta girme ni
da'shekara uku, baitaBa damuna ko >‘rage min
soyayyar ta a zuciyata ba. Ina son ta, ina kaunar
ta, _'ina girmama ta da daraja ta.. Bani 'da niyyar
‘sOn wata ko hada ta da wata a rayuwa ta, '
Deeda ta shi'go rayuwa ta lokacin da ban zataba
balle tsammani, kafin in ankara ta yiwa zuciya ta
illah. Wani irin abu nake ji game da ita, wani abu
da ban 'taBa jin irinsa ba, wani abuda ke kokarin
fin karfina.
“ Ta zama mallakin Sabeer, amma ba abinda- ya
'canja, kunyar .kallon kaina nake balle Sabeer,
ballantana kuma Farida. Nauyin alkhairin su
agare ni, da kyautatawar sugare ni, ya'ci in
sadaukar da irin Deeda k0 fiye.

Ya ‘Allah Ka taimake .ni. Allah Ka
Bimin Gayu-3---sa’adatu Waziri Gombe bani ikon aiwatar da, abinda yake dai dai", - Nan kuma ciwon Farida ya- fado masa da kuma yadda rayuwar Sabeer da Deeda. zata kasance. Tuni' ya. ji: ya kuma rikicewa komai ya kwaBe‘masa ya, rasa . mafita: wannan halin
. ' ' Yaji‘ana sallah “a ‘masallaci, .hakan yasa‘ya shiga~bayi. yayi alWala yawuce masallaci. -' ‘ -_
' f
.Kwance yake .cikin ,jin «'dadi. _da kwanciyar hankali, da. alama‘ya‘ yi bacci mai dadin gaske‘wanda ya jima bai yi. irinsa ba, hankalin 'Sa a kWance', zuciyarsa" cike da tsantsar‘farin ciki da tsana’nin’ son Deeda‘ da ke ratsa‘ dukkan.ilahirin jikinSa, 'yana ratsa shi tare da saukar masa da. wanj irin ni'ima' da niShadi a tare dajin'dadi.-mara misaltuwa.
A hankali ya bude idanuwan sa'dake cike .da. bacci; .fuskar sa kunshe da murmushi, ya kai hannun. sa do Shafar
Bimin Gayu-3,,,,,, Sa’adatu Waziri Gombe Deeda tareda bude idanuwansa,don kallon ta, amma sai ya ji wayam Hakan yasa ‘ya mike da sauri tare: da, baza ido yana' neman' ta, Nan'ya tSai da idOn saf tare da tunanin sa cewa yayi qila tana bayi, saboda' jin“ da yayi ana sallah 'Ya mike da-sauri', 'Yayi'lattin zuwa sallah-har'an kusa idarWa; ya akai yi Deeda bata tashe ni ba?" ' . ' Ya' baWa' kansa 'amsa, _"qila itama lattin'tayi". ‘ ya Fita ya ya'nufi dakin da aka ware nasa,don a dakin-Deeda suka» kwana, Tunanin da ya yi tana (toilet) yasa shima ya' nufi’(toilet)) din dakinsa, 'ya yi alwala cikin hanzari, ammakafin ya foto ya ji har anyi~ sallama, don 'haka yayi'sallah; a dakinsa' kawai.‘ " ‘Bayan ya‘. idar ya fita zuCiyar sa cike‘ :da nishadi,; tare da "dokin son ganin Deeda, wanda ba. tare suka kwana ba.‘ Shi dai yafi Son ya yita ganin Deeda, kuma
Birnin GaYu'3,,,,, sa,adatu waziri gombe yana manne da ita a kowanne lokaci Wannan Shi ne abinda yafu masa kOmai dad1 a raYUWarsa Yana shiga ya tarar da dakin Yadda ya barshi,

hakan yasa yaji.hankalin sa ya soma tashi, ba Deeda a dakin ba alamar ta.
Bayin ya nufa kai. tsaye ya .bude, wayam, kuma ba‘wani alama na anyi amfani da (toilet) din, komai a bushe.
Zuciyar sa ya ji ta harba, ya fito dan ya gama duba sama kaf'ba ita babu alamar ta. Nan 'ya sauko qasa, nan. ma ya gama binci‘ken-sa,’duk wasu falo, kicin; dakuna‘da (toilet). na gidan zuwa harabar (area) dinsu, amma'batanan, hankalin sa yayi mummunan tashi.‘
"Deeda.Ya Shiga Kwala mata kira da karfinsa, kuma‘a rude.'
Ya sake komawa saman dakin ta;
Bimin Gayu-3 ,,,,Sa’adatu Waziri Gombe
"Deeda, ki fito, please in ma wasa 'ne bana so, ki‘fito in ganki. Na san kin Buya ne don ki ga ya zan yi? Na san dai yanzu kinga yadda na dawo, 'na birkice a cikin kankanin lokaci. Kin 'san. Sabeer bai da wata ’ farin ciki da kwanciyar hankali in ba ke, please Deeda ki fito,‘ na san wasa ki ke".
. Tuni idanun sa suka kada sukai jawur,‘ abinka da‘farin mutum, farin ma Kal, hakan ya sa fuskar ta rine tai ja sbd tashin‘hankali.
Ganin cewa da gaske Deeda ba ta dakin 'ya_ sa ya shiga neman Wayar sa, ya sake“ saukoWa falon kasa, ya shiga laluben waya‘ da bai san ma inda take ba. 'A nan ya ci'karo .da' Wata farar takarda' Wanda ta dau hankalin sa akan table. Nan yasa hannu ya dauka. ‘ ’
SABEER;
Ya ga an rubuta da manyan harufa, hakan yasa ya ji bugun zuciyar‘ ‘sa »ta tsananta; ya kasa budewa._
‘Ba k0 shakka ya gane rubutun Deeda
‘ "Me hakan yake nufin" ' Ya fada 'a tsorace. '"Ba dai Deeda..’." Sai kuma ya ‘yi shieu A'a; ba abinda nake tunani bane..;Nasan Deeda bata bar gidannan ba - Haka‘ ya sa wa takardar‘ido ya kasa bude ta, saboda tsabar tSananin fa'rgabar me ; zai tarar a_ ciki? Daga karShe dai ba shi DA zabi sai ya bude don' sanin abinda Deeda take

nufi. SABEER ' ' Dak da‘na san zaiyi wuya ka
fabimci" abinda zan fada maka‘, amma zan fada
maka ko’AIlah Zai-sa watarana ka fahimta.
Sabeez; -nabar BIRnin GAyu ba duniyata bace, ba
rayuwar' BIRNIN GA k0 daya a tsarina zanje na
nemi dai dai da, tsarin rayuwata.‘ "
Ina so ka zauna ka daure kayi dogon nazari da
tunani' akan Deeda, "Wato Shin son Deeda kake?
Shin Deeda abar sonka ce? Abar "faunar ka ce?
K0 dai Deeda Wata rigimarkace da fitinar ka,
wacce kuka saba a ko wane lokaci? ‘
In har Deeda fitinar kace. Wanda in kaso rigima
sai ka same ta kamar yadda ka saba samun duk
ibinda ka so 'a rayuwarka sai ka Samu, ‘kai ba
zaka yarda da‘cewa akwai abunda zaka nema ka
rasa a rayu warkaba, to wannan saidai kayi
haquri sannan inason idan ka rubuta takartar
sakina kakaima kakata ita tasan inda zata
sameni
wasiqar Nada yawa karmu bata lokaci ,Da kyar ya
iya‘ kai Rarshen wasikar, hankalin sa ya yi
tsana'nin tashi, rudani. tare . da tsoro da wani
irin firgita‘ ya. bayyana» a fuskar sa,; idanun sa-
Suka‘ kada. :Ya yi iya kokarin sa. ya
.zubda'haWaye ya gagara. Zuciyar tasa ~ta
dinga masa Zafl da Wani irin zogi. ' " '
Lokaci _ na_ farko. kenan da ya taBa tsintar
kansa a wannan yanayi na‘tsanani' da
tashin‘hankali a Wurin sa.
‘ 'Wani ' irin ‘ bikin ciki ya IulluBe‘ shi, wai duk
’irin tsananin' son 'da yake .yiwa‘ Deeda tace wai
ba so bane? - ' .
"Deeda ba ta San meye so ba, bata san me
nakeji.
'A~lokacin ya samu wasu hawaye masu zafin
gaske'suka' zubo masa.‘ '. "
"Deeda baki san abinda nake ’ji game
da ke me‘tsanan'i ‘da‘ ‘zurfiba bare, ki san-
abinda nake ji game da ke
da zafi bane. A halin' yanzu, ciwon abinda nake ji
na tafiyar'ki zai iya' kashe ni in naci gaba da jin
haka. Ba zan iya jurewa‘ ba".;
"ba dai Deeda ta tafI inda ba zan sake ganin ta

ba?" . d
Wannan tunanin' ya Kara furgita shi da tsorata shi, saboda shi' a- wannan _lokaCi ya riga da ya mayar da' Deeda fayuwar sa, komansa. 'Ji. yake shi ba zai iya yin komai ba in ba tare da Deeda .ba,' yana ganin duniyar Sa ta zo karshe. _' '
A rude ya fita yana rike da takardar,'- ya fito daga (area) dinsa ya' rasa ma ina-zai yi? Wurin. mahaifinsa ne k0 yayar sa da Uncle 1b,? Shin wa yafi biya masa buKatar sa cikin gaggawa a 'tsakanin' su? '
A take Kwakwalwar ,sa ta 'ba shi mahaifin sa, don haka ya nufi Bangaren sa yana kiran sa a'rude 'da Karfinsa. -
"Daddy! Daddy! Daddy! 1'"; ' '
A dai dai lokacin Ibrahim ya fito daga masallaci', don ya jima yana masallacin yana
karatu; tare da addu'o'i. Ganin' ruWan sama na shirin Sake Saukowa ya sa ya fito, lokacin ya hango Sabeer.' Tsananin mamaki-ne ya kama shi. Sabeer- a wannan lokaCin yana Kwalawa" Daddy kira, lafiya kuwa?" ' Binsa ya"yi da sauri, ya 'jawo'. Shi'. Ganin'sa a rude, kuma' a firgi'ce ya tsorata shi. Sabeer, lafiya? Ka ga wani abu da ya ,firgita ka ne?" "Uncle Ib Deeda', Deeda...'.'. .
."Me .ya saamu Deedan?" ' 'Kawai' sai ya fashe masa da kuka: kamar Wani" yaro, ya fada jikinsa.' "Uncle Ib ka taimakeni, Deeda..'.'". Tuni'. -_shima Ibrahim din; ya rude, a tunanin isa wani' abin ne ya samu'Deedan. Jan shi ya yi,' "zo mu je, meya samu Deedan?" " ' . Da kyar Sabeer din ya 'iya miKa masa takardar,' ya". .karBa 'da ,sauri ' 'ya fara
karantawa,
Hankalin ,sa 'shima ya tashi matuka, bai taBa zaton k0 tunanin'Deeda za ta iya guduwa ba. '
Shin rashin son da' take 'yiwa , Sabeer har yayi tsananihaka? Shin ta yaya zan' soma taron 'wannan sabuwar matsalar?. Tabbas komai zai rushe, tafiyar Deeda zai ruSa duk ginin da suka jima suna yi. '
"Ba zai yiwu ba
Ya fada a 'ransa. ,

. .. "Ya zama dole in nutsu in san 'hanyar' da zanbi da Sabeer, 'yanzu ,za'i iya ta da hankalin kowa a BIRNIN ‘ .GAYU, 'musamman Daddy da Farida. Zai daga hankalin: koWa, ba BIRNIN GAYU‘ kadai ba, ba mutanen gaei 'da hukuma kadai ba, har Deeda da mahaifinta da mutanen Kauyen su sai ya musu rashin mutunci, wanda hakan ba zai musu kyauba". .
Tashin hankalin da Ibrahim ya 'hango “ ya matukar firgita -shi,' ya .zama’ dole ya nutsar ‘da Sabeer kar ma mahaifinsa'ya kai ga jin abinda yafaru
Cikin dabara da wayo ya ja shi zuwa nasu 'Bangaren, ya ’ ja shi inda Farida ba za ta ji shi ba, ya rufe kofar yaddah, ya tabbatar da ba mai jinsu yayin da Sabeer' ya birkice masa. K0 su fita neman Deeda, k0 su je su fadawa Daddy ya sanar da :hukuma su fara neman ta.
Ba yadda Ibrahim bai' yi da shi ba ya nutsu‘ ya saurare shi ya Ki, yace sam shi kawai a fita a tafi. Ya dinga murda Kofar yana buga' ta, yana masa bori kamar wani yaeo dan yaye. Sai da Ibrahim din ya daka masa tsawa tare da jijjiga shi,,sannan ya yi shiru. Fuskanan tayi jawur, idanun sa sun kumbura. ' ' ' . ,
Ibrahim ya kalle shi ,da' kyau, kansa sunkuye,duk ya yi kalar tausayi da wahala, ga Kunci da wani irin shaukin‘ son Deeda a tattare da shi.
Tausayin sa ya ji sosai, ya ce
"Haba Sabeer, dubi yadda‘ ka ‘mai da ka-ka,"akan me? mace?_Akan Deed: wacce ba ta' sonka? Wacce bata damu da Santa ba?" ‘
., 'Hakan' ya sa'Sabeer ya dago kai'_ya kalle Shi da manyan idanunsa da suka' rine;
Ibrahim ya ce "Kwarai,‘kalle ni‘ da kyau,‘ Deeda ba ta ma san kana son ta ba.: Ka karanta wasiqar ta, 'amma da Alama ba ka fahimci‘me take nufi ba. Me ta ce maka? Ba son'Deeda kake ba,. Wannan- ba so bane, fahimtar kace, rigimarka ‘ce, kusancin ce; abotar kuce’ .yasa'kayi tunanin kana sonta., -
Sabeer,,in har wacce kake so, so na hauka, "na fltar hankali.bazaka ka iya tabbatar mata kana

son taba, in har son da kake matar-bai kai ‘
wanda .zai tabbatar mata kana Sonta’ba,“
maganar itama ta so 'ka har'kuyi' rayuwar aure
ai" bai taso ‘ba‘
‘ In har Deeda ba tasan kana son ta ba, ba ta
yarda ma sonta kake' ba, to’ ba. ka da
(right) akan‘ Deeda. Baka da Wata dama'akan ta
da har za 'ka 'zo-ka‘daga mana‘hankali,’ baka
da damar 'dagawa kowa hankali akan
(failure) :dinka._
Wannan‘ rashin nasarar naka ne don haka ka
dagawa kanka hankali ba Daddy ko ni; k0 Sister
ba. Idan ka ci gaba da haka ka zama mai son
kai, kuma mai son kai ba zai taBa nasara» ba a
duk inda yake. ‘ _.
Sabeer, ka_ fadi a matsayin 'ka- na namiji, da
'kuma matsayin ka na- miji- (you failed as a
man; you failed as a husband); don .haka
baka' .da damar dagawa k0wa hankali".
.Sabeer ransa yar yi masa zaf1, wani bakin iciki
yaji ya ‘tokare masa kirji akan Wanda da ya‘ke
Cikin zafin 'zuciya yace Unclle Ib, Kazafin da za
‘ka 'min kenan? Me kalamanka suke nufl?"
Ibrahim ‘yace, "Ba 'kalamai na bane,’ ina fassara
maka abin'da ke cikin wasikar Deeda
menene, wanda kai karantawa kawai ka yi, ba ka
fahimci wasikar karba". " Sabeer ya nuna shi da
yatsa, ya ce.’ "Ya ishe ka Uncle Ib, ‘Wannan
Kaskanci da wulakancin da ka min yanzu ba
zan“ .iya jura ba, in ka sake “zan, manta
dangantakar da ke tsakaninmu. Abinda nake ji
game da. Deeda a 'cikin 'zuciya ta, Kwakwalwa
ta da dukkan ilahirin jikina, idan ba. so bane,
to.wani_abu ne wanda ya‘ girmi ’so, ya kuma
fishi matsayi. Abinda nake ji game da Deeda wani
abu ne da kai k0. wani mahaluki bai taBa jin
irinsa game da wani' ko wata a duniyar nan ba,
don haka’ kar ka‘ Kara Karyata min (feelings)
dina, soyayyata ta gaskiya ce, kar ka sake
KoKarin (convincing) dina akan cewa soyayyata
.ba gaskiya bace". ' . Ibrahim ya yi murmushi‘, ya
ce. ‘ "Sabeer kenan, ni da kai mu ka San haka,
.muka'san cewa 'soyayyar ka ,gaskiya ce. Sai dai

wacce ka ke yiwa ba ta san kanayiba ba,
ah shared a profile .
birnin. gayu
chapter16
saboda bata taBa daukan ka (serious) ba, duk ‘wani abinda za ka 'yi ta dauke shi a matsayin yarinta, tana ganin ka yaro, ba ka san ciwon kan ka ba, balle ka san me kake so.
Sabeer, gaskiya daci gare ta, amma ya zama dole in fada maka. Duk da ka girma, amma sam kaki ka girma din. A tunani na yanzu matsayin ka ya wuce a nema maka abu k0 ai maka abu ka ci. Ka wuce Iokacin da Daddy, ni k0 Sister za mu maka abu, Iokaci ne da 'za kai wa kan ka abu, mu dai sai dai mu ba ka- shawara, in .kuma kayi ba dai dai ba mu gyara maka. '
Amma har yaushe Sabeer za mu dinga maka komai? K0 kana tunanin za , mu tabbata da kai? Rayuwar nan ba ta da tabbas, komai na iya faruwa.
Ka godewa Allah kana da gata, iyaye, 'yan uwa, wanda suke tare da kai, za su sa ka a hanya in ka karkace. Akwai dubbai irin ka a duniya da ba su kai ka shekaru ba, amma sun dauki nauyin iyayensu da' kannen, su.
Sabeer, Iokaci yayi da za ka'“san ciwon kanka in har" kana ,so ka Samu 'yadda kake 'so a rayuwa, in ba ka _so.abinda ya faru
da kai ya sake faruwa da kai me ka ke tsammani? Ba Deeda kadai ba, akwai-macen 'da 'ta san ciwon kanta,. ta San me take, ta‘
. yarda da'zama da kai?
. ' Ka taf1 gun Daddy,» in kana son abu'ba’: ka iya samawa kan .ka, ‘in .mats'ala k0 Wata ’damuwa ta ta‘so maka ba ,ka iya magance' ta,‘ ba kasan 'me’za ka‘ yiba, ,ba .ka da wata' dabara, ba tunani?‘
‘."Sabeer,-namijin musamman a gidansa' Shugaba ne, haka kowacce mace za .tai fatan danta ya gaji ubansa, ya yi' hali irin na mahaifinsa; ya ,zama gwani (rolemodel) na 'ya'yansa. Ka gaya min Sabeer wani ‘halaye ne daga cikin halayen ka; matar ka za ta so tayi

(Alfahari da shi,. 'har ta' soka zama uban yayanta?
. Sabeer, ya zama ,dole mu dinga yiwa kanmu -'tambaya, muta fadawa. kanmu
gaskiya"- ' ' Tuni jikin Sabeer ya yi sanyi, kansa sunkuye sai hawaye yake . Tabbas bai taBa jin kasaWar sa ba tunda yake a rayuwa sai yau.
Ibrahim ya tausaya masa matuka, haka nan ya ji dadin nasarar da yayi akan Sabeer.
- Ya matso' gabansa, ya. tallafi fuskar sa suka hada ido, sai ya fashe da kuka, ya fada jikinsa.
"(Uncle Ib, I am sorry) a 'shirye nake da na dau duk wani . gyara, ba zan sake fitinar Daddy k0 " Sister ba, ba zan sake dagawa kowa hankali ba.
Ka fada min Uncle Ib ya zanyi? Ina son zama irin mijin da Deeda ke so, ina son zama irin'ka, saboda Deeda na sonka. inason son zama irin mijin da Deeda za tai, alfahari da shi, haka ina' son 2ama (rolemodel) na 'ya'yana. '
Uncle Ib, ka yafe min, na fitine ku da yawa, yanzu ka fadamin ya zan yi? Duk abinda kace zan yi".
Ibrahim ya yi murmushi, yace
"Na'ji dadi da ka fahimce ni, zan baka shawara, in sa ka a hanya, amma sauran aikin naka'ne. '
- Kagana farko ya zama dole .ka kare mutuncin Deeda a matsayin ta na matarka. sannan mutuncin ta naka ne. A yanzukar ma ka bari Daddy ko Sister su ji ta gudu balle mutuncinta da kimar ta ya ragu a idonsu balle~har_ 'su dora mata wani' 'wahala' da damuWa Ka san~ Daddy 'zai~iya komai akan ka, wanda a garin haka zai Batawa Deeda,' ita kuma za ta dora lafin akan ka. Kaga'hakan zai sa ta' Kara'tsanarka, tare da niSanta' kanta da kai.Maimakon haka, kayi abinda zai kawo kusanci tsakanin ku".
.Lokacin Sabeer yadago kai ya kalleahi
Me zan'yi Uncle Ib?" ' - .Ibrahim din ya gyara zama, ya- kalleshi', ,yace' "Deeda matar ka ce,' don haka ka' bita inda ta ce duniyarta'ce 'ka je ka nuna mata
ba wani bambanci tsakanin duniyar ta da' naka, ka nuna mata duniyar ku daya, rayuwar ku daya, ka kuma tabbatar mata da cewa son deeda ba

rigima ba ce k0 fitinar Sabeer. Son ta so ne na hakika, so‘ na gaskiya, wanda za ka‘ iya yin 'komai kuma za 'ka jure komai muddin bai saBawa shari'a ba. Duk Wahala, duk Kunci, duk Bacin rai, KiShi, da yinwa ruwa da iska, zafl da' sanyi duk za ka jure. Ina fatan kana gane Hausa a dundule da nake maka?"
Sabeer ya girgiza kai, ya ce. - '
"Ina fahimta, kuma ina hango abinda ka ke hango min". ’
Ibrahim—ya shafa kansa, ya ce
"(Good my smart brother)". Yana murmushi.
Ya ce, "Na san za ka iya, za ka yi abinda ya f1 haka. Ni" kawai na nuna ‘maka abinda za 'ka yi ne, sauran dabara ya rage naka. ‘
Sannan abu na karshe Sabeer. kar ka taba roKon so_(nevcr beg for love). Idan ka tabbatar mata da soyayyar ka sai ka sa mata na ka soyayyar (make her fall for you); ka kasance ka karanci tunaninta yanayin ta da yadda take komai, zai zo maka da sauKi
‘ Sannan hakuri, juriya. Idan ka yi Wannan nasara tana tare da‘ kai da yardar Allah. Sauran ka yi addu'a ka barwa Allah".
"Nagode Uncle 1b, zan shiga ciki in cewa Daddy zamu yi taflya; ba zan -nuna-_ masa Deeda ta gudu 'ba, sai in xo in shirya‘in tafi
‘ Zan tafi neman Dceda, zan tafi Kauyen su, k0 a kango take zama zan bi ta mu zauna tare". ,
_ Yana gama fadi ya mike, Ibrahim ya bude masa kofa ya fita, ya bi shi da kallon tausayi. _
("Allah-Sarki Sabeer. dama, ta ya zaka iya rayuwa‘a Kauyen su Deeda? Yaron da zaman Nigeria kanta'. ke masa wahala yana cikin babban gida 'na ' jin dadin 'rayuwasa amma ya'na mitar zafi da wahala, ina ga , zaman kauye? Allah ba da sa'a Sabeer, zan yi ta maka addu'a". -
Ya mike kan doguwar kujera; tunanin Deedan da tsananin sonta ya dinga bijiro mishi. Sassanyar muryar ta da fuskar ta mai cike da kwarjini da annuri', tare da murmushin ta mai tafiya da dukkan wani damuwar sa, sannan da Sanyin hali

irin nata.
."Deeda, ya zama dole ki manta Ibrahim, saboda kina da masoyi wanda ya f1 Ibrahim son ki, haka Ibrahim ba shi da filin da zai iya ba ki a gidan sa da rayuwar sa. Filin da zan iya baki a zuciya ta ne, sai dai zuciya ta kadai bai isa ba, zuciya ta kadai (is not enough)"
Haka ya kwanta a wurin, idon sa rufe, tunani kala —kala aransa. '
A ' Kai tsaye Sabeer ya wuce Bangaren su, gaba daya jikin sa a mace, haka zuciyar
sa cike da kuncin rashin Deeda'. Haka- nan ya tsinci kansa cikin kadaici da tsananin kewa.
' A tsakiyar falon ya zauna ya 'hada kai. da gwiWa, duniyar tai masa - zafi, maganganun Ibrahim ke yawo"a kunnen sa.. Hakan ya sa ya-ji yana son yin kuka, sai dai bai bari hawayen sunzubo ba ya 'yi kokarin" tsai 'dasu, ya mike 'ya nufi bayi don-yin wanka, ya sakarwa kan sa shawa.' A lokacin' ya' samu damar sakin hawayen sa,'ya fashe' da wani irin kukan takaici da Karfinsa. Ya yi kukan samai isar sa,.Sannan ya fito'ya hau shirya kayan sa cikin wani dan madaidaicin jaka'; . '
Duk inda ya'motsa 'Deeda yake ji 'a ransa a ' zUciyar sa da Kwakwalwar sa,' tunaninn ta'ya hana shi sakat,_ ita kawai yake jida gani, haka nan'ita yake? son gani, da ita 'kadai yake son ya kasance Hakan ya bashi Karfin gwiwar taf1ya'nem0 ta duk inda ta ishiga, haka nan inbazata' ta iya biyo shi BIRNIN .GA'YU ba._. shi zai bita duk inda
take ya zauna da ita ya rayu da ita a k0wane irin hali,
'Da- .wannan tunani» ya 'gama shirya 'kayan 'sa, ya. .dauki duk Wani abu da-yasan zaii masa; amfani, ya nufi motar ya' zubasu, ya dawo ya shirya tsab, sannan' ya nufl Bangaren mahaifinsa. Kai tsaye ya wuce' dakin bacin sa, nan kuwa ya same'shi yana bacci. Nan ya 'tsaya yana kallon sa, ya' rasa .abin yi, Shin ya tashe 'shi k0 a'a? Anya'zai iya .tafia' bai yiwa mahaifin sa 'sallama ba .ya yi dai dai kuwa? Ba zai, iya' taflya bai

masa sallama ba, hakaba zai iya 'tashin saba, ya nemi kujera' ya ’zauna‘ yana jiran tashin sa. Zaman ida 'yayi‘ shiru yana tunanin Deéda da kewar ta na shigar' sa, nan da nan. idanun sa' .suka .ciko duk-lokacin da yake tunanin ta sonta » na matsa masa, sai ya ji' yana .sOn yin kuka. Nan. ya mike da sauri dOn ba ya Son yin-kuka’ a gaban mahaifinsa
Her ya juya zai tafl',"sai .kuma ya sake jUYOWa yayi ya tsaya yana kallon sa.A lokacin Daddy ya bude ido, ganin Sabeer .a tsayge ” ya bashi mamaki, amma sai ya y1 dariya Ya taShi gami da ‘sa glass dinsa, ya zauna tare da jingina a jikin gadon, ya ce
"Sabeer, kaine da safen nan?"
Ya fada yana ‘murmushi, fuskar‘ sa cike da faraa'a tare da jin dadin ganin dan nasa. .
Nan Sabeer din ya matsa gabansa ya zauna, haka kawai ya ji yana jin nauyin mahaifin nasa. Ya dan sunkuyar da kai tare da fadin.
"Daddy, ina kwana?"
' Daddyn. ya jawo hannun sa yana murmushi, ya ce
"Laflya Sabeer...". Tare da fad‘m.
"Lallai na yarda aure mai gyara mutum, mai kuma mai da yaro babba. Yau
na ga Sabecr dina ya girma, yau na ga wani nutsuwa da girma a tare da kai. ALHAMDU LILLAH da samun abokiyar rayuwa irin Deeda.Sabeer ,kayi dace kwarai, ka rike. yarinyar nan amana,'kuma hannu‘bibbiyu‘. kullum' 'ina‘ maka‘fata da addu'ar samun kyakkyawar rayuwar aure, ba .na fatan -_rayuwar ka ta Zama irin nawa, me. cik’ da ‘keWa, rudani da rashin ‘ nutsuwa da kwanciyar hankali.‘ Ina maka ‘_ addu'an rayuwar 'aurenka ta cika da farin ciki, ' ka rayu da iyalin ka cikin farin ciki da kaunar juna. Yau na ga alamar cikar burina a safiyar auren ka; yau Sabéer dina ya riga Daddyn sa tashi,‘ya.shirya‘tsab, ga wani sabon nutsuwa. a tare da kai. YarOna ya Zama (serious) ya girma, ba - sauran yarinta, ba fitina, ba rigima. .Zan ci ‘gaba da muku addu'a Allah ya barku- ,tare da

Deeda har iya qarshen rayuwarku " Ina ga Iokaci Yayi 'da-'2an bar“ ‘maka‘ komai 'kai da‘yan uWanka, inada‘ tabbacin kai da Ibrahim kun isa". Tunda'. Daddyn 'ya‘ soma magana kan Sabeer' na sunkuye', Wani' irin rudani, da
baqon yanayi ya dinga ji a'jikinsa'da- zuciyar sa, haka wani irin tsoro ya jii'Yana shigarsa. ‘ _Ya’ dinga jin wasu‘ 'irin bakin abUbuwa a jikin sa da zuciyar sa wanda bai taBa jin irin su ba. .Haka kawai‘ya ji‘ wani irin Kaunar mahaifin sa da tausayin sa tare da fargaban kar‘ mahaifin sa ya gane Deedan guduwa' tayi.' Nan ya yi qarfin hali ya dago kai, ya yi murmushi ya ce "Daddy na gode da addu'o'in ka,~ da kaunar ka gare ni, Allah Ya saka maka da gidan, Aljannah. Kafin yanzu ban taba gane muhimmancin ,ka da irin Kaunar da kake 'min ba ‘sai yanzu. Daddy,- (please) ka yafe min duk abinda na maka a rayuwa na Bacin rai, da fatan ‘za ka sa min albarka a rayuwa ta,‘ ba zan sake duk abinda ba ka so ba ina bukatar addu'ar ka fiye da komai".”
‘ ‘ Ya, kwanta a~jikin mahaifin nasa gami da fadin. _. - . " "Daddy ka yafe min".
Daddyn ya yi dariyar jin dadi ya ce
"Sabeer na yafe maka, kuma zan ci gaba da maka addu'a Allah ya baka sa'a da nasara a dukkan abinda ka sa a gaba, Allah Ya sa maka hakuri da juriyan mu'amala da mutane a duk inda ka ke
Sabeer ya dago kai ya yi dariya, ya ce.
"Na gode Daddy, dama ina so- in roKi. alfarma ne Kafi in koma aiki office ina so mu yi wata tafiya-ni da Deeda na dan tsawOn wani Iokaci, in mun dawo In-sha Allah zan koma aiki, haka nan ba za ka samu matsala da mi ba. Kafin in dawo aiki sai Uncle Ib da Sister su cigaba da aiki kafin mu dawo". ,
Daddy ya yi dariya ya ce, "Na fahimta, Iokacin ka ne yanzu, ba mai. hana ka taflya. Ka dau Deeda ku zaga duk inda za ku zaga a duniyar nan na‘tsawon Iokacin da ku ka ga dama, ku ka gama hutawar ku, sai ku dawo. Offlce da‘ aiki zai 'jira, amma wannan Iokacin na ku ba zai jira ba,

wucewa
zai yi. . Saidai duk inda kuke ka dinga waya muna jin labarin ku, ka kulada kan ka da Deeda; .ka tabbatar kuma ka, dauki .(Debit card) .dinka, duk' inda ka. keza ka ,iya,cire
kudi yace To Daddy, na gode, ba'zan manta ba; Allah Ya kaara lafiya, A'llah Ya kara girma
da daukaka'
'Ameen Sabeer'
Nan suka yi 'Sallama cikin farin ciki da son juna,mahaif1n sa na godewa Allah. ' ' Yayin da Sabeer ya fice, ya nufi jikin motar sa ya jingina, tunani kala kala a ransa. ;Yana godewa Allah da Ya. Sa Ibrahim ya tsai da shi bai je ya' fadawa' mahaifinsaba. "Tabbas da ya'je' da bai 'ga 'Wannan farin ciki da nutSuwa a ' tare da mahaifin. sa ba, Wanda ya'samu ta dalilin, sa. ' ' .- ' " ya wuce wurin yayarsa, a nan ya tarar da ita tare da Ibrahim. Kansa a sunkuye ya gaiShe ta, ta amsa tana' murmushin Karfin
hali, tana tausaya masa, saboda ta gama jin komai wurin Ibrahim. ". ' Sabeer yace, "Sister zan wuce". , "To Sabéer,.Allah ba 'da sa'a allah ya kiyaye hanya"; .' ' Ta fada cikin muryar rauni, ya amsa
.. ."Ameen in. Sannan ya kalli Ibrahim, ya Ce.
' ' "Uncle Ib, (Please za' ka kaini 'tasha
inda zan samu motar Kauyen su Dedda?"
' Farida ta kalle'. shi, "Haba Sabeer, ka
tafi da .motar ka mana, ba sai ka shiga
motar kasuwa ba". . '
. " Ya girgiza mata' kai, "A'a-Sister,
zan fuskanci Wata sabuwar rayuwa ne. Ina
so 'in ga iyakar'iyawa .ta, 'da juriya ta; Kafin
in tabbatairwa da kowa ina Son tabbatarWa
kaina, me zan iya? Meye ba zan iya.ba? _ Sister,
kar'ki damu, na san rayuwar da
zan fuskanta ba'mai' sauki ba ce, "amma zan
iya insha Allah". " '
' ' Yakalli Ibrahim, yace"Uncle Ib, zan jira'ka a mota". Nan ya juya ya fita, Farida ta'.bishi' tana Kwala _ masa 'kira hankalin ta a "tashe, Ibrahim yajawo ta. ' ' " '"Kar ki tsai dai shi Farida, in ki ka

hana shi tafiya yau‘ zaki yi dana sani a gaba, ki Kyale shi. Lokaci na farko kenan Sabeer zai. yi 'abinda yake dai dai, ya soma fuskantar gaskiya a rayuwa, ya soma gane' yadda ya dauki rayuwa ba haka take ba"; Farida ta fashedakuka,tace' ' ,"Haba Ibrahim, Sabeer ne fa? Ya 2a ka barshi ya tafi wani wurin da ba zai iya k0 da kai kansa ba balle har- ya iya gane wurin? Ya za a yi ya tafi shi daya,-yaron da bai taBa fita k0 nan nan shi daya ba? Yaron da. 'zaman Nigeria da Kano ma ke masa wahala, shi me‘ za ka tura shi wani Kauye? Ya zai ‘rayU, a w‘urin?‘Me. ,zaici? Me zaisha? A inazai kwanta?
‘- ’Ta fashe da kuka. "Gaskia Ibrahim
ba zan yarda da’wannan tsarin ba, Daddy ~ma in yaji_ ba zai ‘ yarda ba. Wai' ka manta Sabeer'da‘ Yanayin sa,‘ne.?" ~(Please) F arida". Ya'katse' ta. _ "Ki. Kyale‘shi, Sabeer mutum ne, kuma; namiji ne. Sannan kar ki manta matae 'sa zaibi,matar,sa'2ai nemo, yana da dukkan- dama, " (right) dinsa-ne ya je ya nemo matar sa, ya dawo da ita, ba wanda zai yi'masa wannan. Ya zama ' dole ya. dauki \dukkan wani (responsIbility). nasa,-ya dauki 'dukkan wani nauyi da ke kansa'; Shi zai wa kanSa_ wannan ba wani ne zaimasa ba " . “ ' . " ' ~ Kar ki manta. magana ne da bani na mutuncin sa; da kimar sa, da a. idon matar sa. Ya zama dole ya tsira': :da ~ mutuncin,'da‘darajar sa a idon matarsa Kar kimanta, a ‘halin yanzu Deéda‘ ita ce rayuwa da duniyar Sabeer gaba daya ya‘ zama doleta gane- haka, Ya zama "dole'ta fahimci' ceWa yadda take‘tunanin. Sabeer‘ ba
haka yake ba, .ya zama dole tasan Sabcer abin 'sone, abin ,alfahari ‘né ,ga ‘ kowacce- mace., Haka’ nan duk_ duniya ba zata .samu miji irin Sabeer ba, ba za ta samu mai son‘ta ' _ irin' Sabeer'ba; ,Ko ba za ta" so shi‘ ba, ya‘ zama dole ta San kimar sa da darajar“ sa, da muhimmancin sa.~ Kiyi Koqarin fahimta Farida ba abinda zai samu Sabeer". ‘
Nan ta zaUna ta fashe-da kuka, tace1 _ "Ibrahim, ina tausaya masa ne, shin Deeda‘ta cancanci- ya

sha wannannan wahalar
saboda ita?" ‘Yayi murmushi, ya ce, "Yayata, wannan IokaCi ne zai iyé nuna ta cancanta k0 a,a?
Nan ya juya, "'Ni na tafi kaishi‘ tasha, sai na dawo". . Nan- ya fice ya barta tana kUka tare da’ tausayawa Kaninta.
Tunda suka fara'tafiya ba. wanta ya' cewa kowa komai, har. Suka iso‘ tashar. (Bus)
da‘ zai je .Dawakin, ‘Tofa, daga nan in ‘ya sauka zai samu motar da zai kaishi qauyen su Deeda, 'hayin HAGO‘. —. ‘ ‘
Nan Ibrahim ya biya kudin motar tare ‘da‘yima' direban motar bayanin cewa in sun sauka a taSha ya néma masa motar‘da za ’ta kauyen Hayin hago ya sa ‘shi. Direban yace in. sun isa. Zai samumota, amma Sai .akori kura, don ba kowacce 'irin mota ke shiga ba, sai manyan manya irinsu ‘ akori kura-din ‘ Ibrahim '-yayi -dariya don ya san_ da,
wannan, sai dai ya. tambaya a gaban‘ Sabeer ne "saboda yaji da kunnen sa
Ibrahim ya- kalle' shi, yace
. "'Ka ji,'ko za ka iya?"~ -. .
Jikinsa a sanyaye ‘ ya girgiza. kai al'amar eh‘ zai iya. Sai dai da alama- tunda 'Sabeer ya zo tasha yaga ‘yadda yanayin’ yake hankalin sa' ya soma: taShi. '
~' Ibrahim ya ja hannunsa ya shigar. da shihar cikin‘ (bus) Ganin yanayin cikin' (bus) din, da irin kalar‘ mutanen “da‘ ke ‘ciki
ya shiga zuciyar sa ta dinga‘ harbawa, tsoro karara ya bayyana a fuskar sa.
Ibrahim ya kalle shi, ya ce
"Kar ka damu, ka kau da kai ga komai a nan, ba wani abin tashin hankali. Ba wani abu a nan, duk komai da kowa‘ a, nan (normal) mutane ne. Kayan ka na ‘bayan- (bus) din, inkun sauka ka kula,_ ka dauka kar ka manta".
Ya mika masa' Karamar wayar sa, ya ce
"Za tai maka amfani,‘ haka nan'a duk lokacin da ka ji Wani baKon yanayi ko tsoro', ko wani shakka, akwai' (application‘) na addu'o'i, ka bude

ka karanta. ' 'Akwai Alqur'ani a ciki, shi ma ka dinga karantawa (you will be fine). Na sa maka'sauran waSu tarkacen cikin 'jakar kar, wanda qila zasu yi maka amfani. Ni zan tafi, Allah Ya kiyaye hanya".

. Bai yarda ya kalle Shi ba, saboda bai son ya karaya, don haka ya juya zai tafi

Hakan ya sa Sabeer ya mike da sauriya kira shi, ya Kankame 'shi, zuciyarsa'na harbawa, tsoro Karara a fuskar sa. ' - Ya rungumeshi, ya ce. ~ '.'Un'cle Ib, inajin tsoro (I am seared) kar ka tafi ka barni, kazo mu tafi tare, (I am scared of being alone)". ' Ibrahim ya, tausaya masa sosai, ya ji " tamkar' ya hana shi tafiya, ya ji kamar ya ja . shi su koma. Sai dai hakan ba'zai yiwu ba, inya tafi'da shi Wurin,Deeda shirinsu zai warware. ' . Ibrahim ya dago shi 'daga jikin sa, ya masa murmushi cikin karfin hali, don ba shi Karfin gwiwa, yace. _ ' ' "Sabeer, wannan yaKin naka ne (and you must-do it alone). Kark'a' ji ,tsoro, ba komai, ba abinda zai faru da kai. Matar' kaza ka je ka' dauko, ka tuna'Deedan ka, Wacce _ta ke rayuwar. ka da farin' cikin ka a yanzu tana can, bai kamata ka ji dar ba, ba kai" kadai bane; Allah .na tare ~da kai, saboda

niyyar ka mai kyau ce, haka nan da lokaci kadan za ~ka kasance tare da Deed, kar ka damu. '

. Kar ka manta duk abinda ya shige ma duhu ka yi tambaya cikin kwantar da kai, in manya ne 'ka musu cikin ladabi, in. yara ne ko sa'annin ka kai musu cikin tausasa lafazi.. Ka zauna lafiyada kowa ka ji?"' .,

.Sabir din'ya girgiza masa kai alamar ya ji. Ibrahim: din ya~ zaunar da 'shi, sannan ya' fita. Sabeer ya-bi shi da kallo yana jin tamkar ya' bi shi, 'har ya shiga mota yana kallon sa ta window. Haka Ibrahim" din ya dinga kallon sa shima hankalin sa a tashe,.ya rasa 'me .ke masa dadi? Har motar ta tashi yana zaune a mota ya kasa tuKin, kewa da rashin Sabeer ya shige shi., . Tunda aka haifi Sabeer ba su' taba rabuwa ba, duk inda zasu je suna tare, kafar sa Kafar Sabeer, k0 Farida ba ta' kai shi kusanci'da .Sabecr ba.

Haka Sabeer shi ne mutumin da ya fi kusanci da shi a dUnia
duniya fiye da kowa; kullum suna tare, .su yi fada su ‘shirya. Ya zama tamkar uwa kuma uba ga Sabeer; haka Sabeer ya‘ zama tamkar dansa, abokinsa, kanin sa.
‘ Ya tuna Sabeer ba ya iya yiwa kansa 'komai a 'rayuwa, kula da kansa ma bai iyashi. balle kula da kayayyakin sa. Zuciyar sa. tai; masa Kunci, ya runtse ido‘ yana .addu'a a ransa, tare da yiwa Sabeer addu'ar samun nasara, da fatan Allah _.Ya kare shi. Ya jima a wurin kaifin'ya tafi ' ‘
Hakan ce ta kasance ga Sabeer, shi ma tunda suka‘ ‘fara tafiya a (bus) din hankalin sa a tashe yake, kallo daya in an masa za a ga'rudani da tsananin tsoro da firgita Karara a fuskar sa. '
Rufe idonsa ya yi' gam ya Ki budewa tare: da rungume jakar sa ta hannu Karama da ya goya a baya ya ciro ya jefa wayar a ciki, ya rungume‘ta tare da' damke idanun sa ‘yana addu'a; yana kuma tunanin Deeda, ya‘ hango fuskar ta. .Wani lokaci‘ yakan yi murmushi.
in ya tino zai je; ya ganta, zai ‘kasance tare da ita., ,Da wadannan tunanen ya mance damuWar sa,. har suka .iso karamar hukumar Dawakin Tofa. A. nan‘ ya ga mutane na ‘ta sauka, shi dai 'ya rasa abinyi, ya tsaya yana kallon su har' suka sauka duka. Ya lura kowa na ta harkar gabansa. ~- Direban ne ya shigo ya ce, "Malam, ‘ba‘ za ka sauka ba' ne? Ba kaine mai taflya Kauyen Hayin Hago ba?" Sabcer 'ya girgiza masa kai ' tare da cewa."Eh zan je, motar ka ba 2a ta iya kani ba?" Ya fad‘a‘kamar zai yi kuka, - ' Direbah' ya Ce, "Wa'? Ai mota- ta ba zata iya shiga wannan Kauyen."ba, musamman yan ’zu'a. damina; Akori kura ce ko babbar mota'masu manyan tayu za su' iya ga wata can” akori kura' kayi sa'a sun yi lodi za’su tafi kai" nono, sai ka je' ka biya .su ku tafi. Amma' fa ba za ka samu gaba‘ ba, don ka yi. latti ya cika, kayi' sa'a ma ba za kayi
jira ba, tun safe suke'lodi". ‘ ' ‘
: Nan (Sabir ya taso ,ya fito yana bin mutumin.

yadda~ zai 'biya‘ kudin motar ma bai. iya' ba,
sai da direban ya taimaka masa ya ciro kudi a
aljihun sa, k0 Kirgawa bai yi baya miqa musu.
Nan ,suka tsaya suna kallon sa, Naira dari biyar.
zai ba su, amma ya Ciro kudi‘da yawa.
.. ' Nan mummin ya ja shi gefe ya' ce ’
' "Kai malam, shatar motar‘za ka yi ne
duka?""A'a kudin motar nake biya".
"Naira dari biyar ne ai‘ na fada maka". ' Nan ya
miKa masa dubu daya ya je ya biya masa,.da‘ya
kawo masa canji ya ce ya bar masa, nan ya
washe baki'yana ta godiy‘a.' Yanunawa Sabeer
bayan akori kurar ya ce, ya hau.‘ Nan. ya ‘ tsaya
yana zare ‘ido, buhunhuna ne a cike da
kayayyaki,’ sai wasu. Fulani guda biyu, bai san
ma a ina zai zauna ba-.- '
Ya juya ya kalli mutumin kamar zai. yi
kuka,_yace’A inaza‘n'zauna?" Mutumin‘ yayi
dariya, albarkacin alkhairin da kamin "Bari
in‘nema maka Wuri". - ' Nan ya~ matsar da
wasu kaya, 'ya gyra wani lungu inda zai iya
zama. “Sabeer' ya. .kalli mutumin, ya kalli
~Wurin,_yace. ‘ ' "A'nan zan zauna?Kwarai
kuwa";DA a Ina kake tunaninzaka zaunan
Hmmm
jama,a shin wai ita wannan Son DA ake magana
batasan ya kamata bane ya za,ai ta dau dan
babban mutum Mai naira kaman saber ta kaishi
wannan kauyen? ‘ ‘ lol
c y'll
hared a profile .
birnin gayu
chapter17
_ Ya ce, "Ai na maka gata ma, da sai dai ka
zauna a saman buhunhunannan' Ba yadda ya‘
iya, ‘hakaya yi ta Kokari‘n' haWa, da- kyar.
direban' ya taimaka masa’ ya‘ hau, bayan ya sha
kasa sau, biyu, a ukun ya dace ya samu‘ ya
shige, ya makure~-guri guda’ yana 'runtse ido
yana ji bayan sa na" amsawae.
; Direban ya tsaya yana kallon ‘sa, yana
mamak’i, don . ya lura , kamar " haWaye . ke
shirin f1ta masa Nan"ya"'shiga laluben jakar

sa. zai sha ruwa, ya kuma dauki wayar sa, Gaban sa ya fadi da ya tuna ya bar babbar . jakar sa a mota, ga direban ya'juya. -
' " ‘ Nan ya mike da sauri ya dirgo ya nufi (bus) din da sauri, ya tsai da mutumin, ya ce masa ya manta jakar: sa. Nan ya duba ya dauko masa ya mika masa yana janta da Ryar. Ya isa ya samu motar. za ta tashi, ya ji . kamar ya fashe da kuka da ya tuno wahalar
- '- hawa motar.
' Nan ya daga akwatin ya wurga, da kyar ya samu ya hau. Tuni bayan sa ya fara amsawa,._ haka ya 'zauna a maqure cikin buhunhuna,‘ yana rungume da jaka babba da Karama lokaci guda.Wahala ta sa ya fara fita hayyacin sa, ga iskar bayan mota, ga kura ya cika masa ido, gashi ba shi da hali ko' sukunin bude jaka balle. ya dauko glass ya' saka, saboda a takure yake. Nan fa Fulanin nan suka sa shi a gaba da kallo tamkar‘sun ga wani sabon halitta.Da alama‘dai yanayin sa da yadda yake su ke kallo, suna ganinsa
tamkar wani Bature'ko Balarabe. Shigar. sa kadai zai ba da tabbacin ya fito daga gidan Alfarma, to k0 me'zai kaishi kauye? Sabecr bai ga komai ba sai da suka bar
hanyar titi, suka hau' na kasa, suna shiga rami, suna fadawa, suna hawa tudu. da ’gangare, tsoro da fargaba suka cika masa zuciya. ’ "Wayyo Sister, Daddy, _Uncle Ib. Wayyo Allah na...".
‘ Bai rufe bakiba'kuwa ruwan sama ya sauko, ya yi. masa dukan tsiya a bayan motar. ~ya galabaita, ya‘ fitta hayyacin sa, ya shiga rawar sanyi yana karkarwa, ga ruwa, ga ’iSka mai sanyi na hura shi. A cikin wannan tsananin Sabeer ya iso Kauyen su Deeda, .da kyar ya samu ‘ya Sauko duk jikinsa ya yi tsami, k0 ina ciwo yake masa.
Ya sauko yana jan jakar sa, ya rasa ma ta ina\ zai fara shiga Kauyen wacce hanya zai bi? ’ - ' Nan dabara‘ ta fado masa. ya tambayi
"ya tambayi yan Fulanin nan wacce hanya za a bi a Shiga cikin kauyen, da. ya lura da inda suke

tasha ce k0 kasuWa. , . ' Tsayawa Sukai. suna .kallon 'sa‘ da. alamar ma ba su san yana yi ba,don‘.kuwa ‘ ba Hausa suke ji ba. . ‘ _, Haishi ya kama shi, ga in sun tsaya ‘ suna kallon sa.tamkar ba magana yake musu .. ba. - Nan.ya hau jan jakar sa yana kutsawa 'tare da addu'ar, Allah Ya sa akan hanya dai '
dai yake.‘ In ya ‘gaji ya kan zauna ya huta ya - yi ta tunanin gida da Deeda. Shi dai ya san inya hadu da ita dukkan damuWar sa' ta
‘ kare. .
Allah Ya amshi- addu'ar Sabeer, yana ‘ cikin tafiya ya soma cin karo da mutane da kuma bukkoki, wasu' kuma» ginin qasa ne, ‘ a watA ; Nan ya hau tambaya ko' ina zai samu-gidan Inna mai Fura?
~ "Kasan'cewar garin' Hausa Fulani ne, don 'haka ya dace da HausaWan garin, sukai .. masa kwatance’ kan kWatance, har ya' dace,
ya samu yaron da ya ce zai kaishi har gidan ~ su Deeda.,. _ " " ' Nan 'ya' sauke wata- irin ajiyar zuciya, ‘ tuni' ya manta da duk Wani wahala'ko tsoro ' ' da fargaba‘ da ke tattare da shi, .ya shiga 'murna da ,dokin ganin.Deeda,‘yayin da duk inda ya' wulga, sai, an bi shi da kallo, wasuma mu'samman suka. taso suna binsa, ; suna ’mamakin me ya kawo Balarabe kauyennan"Abink a .da mutancn kauye, abin‘ kallo‘ bai
mush kadan. ,
' Inna ce zaune ta hada tagumi, hankalin ta a tashe, abin duniya'ya ishe ta. ‘Deeda ‘ce kwance'a cinyarta .tana kuka, wacCe ta iso; kauyen tunda'sassafe. ._ . - " ' ,Kuka 'take'tana" rokon Inna kar ta .mai _ data birni, ta barta ta zauna da ita a Kauye.:. ‘ Deeda ke yarinya-ce shi yasa' kiké- . aikaté'wannan "babbar kwaBar,‘ki_ ka tafka‘ kuskuren da ban san yaya zan soma gyara
shi ba; An fada miki- aure wasa ne? wanna irin rashin hankali ne _ ya Sa -ki ‘tunanin guduwa— daga gidan mijin? Kin ‘zata’baza' su_ iya ZuWa Kauye su 'nemo. ki- bane? Kin San: za ki gamu da fushin mahaifin 'ki? ‘Kin san Sabeer ba zai

kyale mu .ba.
Bayan' wannan, Deeda me kike so? Me kike nema a rayuwa? Allah Ya baki miji mai son ki, me kaunar ki. ‘Ki tuna duk jama'ar kauyen. nan mazan su da matan su sun guje ki, mahaifin ki kansa‘ sai‘ da yaguje ki, A wannan lokacin Sabeer ya ce, ya ji ya gani yana son ki, Deeda meye damuwarki? Meye matsalar ki?"
Deeda ta fashe da kuka, ta ce.
_"Inna' kiyi Kokarinn 'fahimta‘ ta, 'Sabeer‘ fltinar sace kawai" ba wani so, 'Sannan’Inna ' ya za’a yi na cutar da Sabeer in zauna da. shi bayan ba na son sa? Ya 2a a yi na ,ci amanar sabeer da amanar aure? Ina auren sa da son wani a'zuciya ta? ' '
'Inna,_kin San irin son da nake yiwa.
Ibrahim, ta ya zan-iya. rayauwa‘ da shi gida daya, wuri daya da Sabaer, ina ganinsa kullum? "
'
Inna, ba na son ‘cutar da ko dayan mu, in na ci gaba da rayuwa a BIRNIN GAYU‘ bakin ciki zai’ kashe ni,’ rayuwa ta za ta nakasa, zan cutar da kaina da Sabeer. Inna,
.na rasa ;ya zan yi, na rasa inda Zan shiga;
’Sanin kanki'ne‘bani da kowa; bani da Wanda ya' wuce ki. Kin san Baba kansa.‘ ya tsaneni Inna bani da inda'ya wuce ki da Kauyen nan, haka duk rintsi- duk abinda mahaifin Sabeer zai yi sai dai ya yi, amma ba zan bar Rauyen nan dakeba.
. Haka nan na san Saber, na san eigimaesa da yanayin rayauwar sa, zai yi fitinar sa na lokaci kadan ya manta dani, inda nake’ ko ba zai” iya zuwa ba,;‘ba abinda zai sa Sabeer ya 20 nan.
'Shi yasa na-‘taho nan, saboda Sabeer mutum ne Wanda ,ya ‘saba da dadi wahala k0 ba ya 'iya jure ta ko na Kankanin lokaci. "
Mutumin dake Kyamar Wasu unguwannin 'ma a cikin'gari, balle kuma kauye, qauyen ma irin' namu, me kama 'da jeji? Ba abinda ’ zai kawo_ shi‘, dOn haka Kauyen nan" shi ne kadai ‘hanyar da zan bi. in gujewa 'Sabeer da'fitinarsa
Inna dai tayi shiru tana ta, saboda wannan tunnin na Deeda ne ita' kadai,‘ ta‘san: ' rigima da tashin

hankalin da, take hango musu.‘ In har Sabeer ba' zai iya zuwa kauyen ba,~ tafi kowa sanin mahaifin Sabeer 'da nata. ’mahaifin' sai sun mai da._ta gidan Sabeer. Ya _‘-zama dole ta ganar da Deeda. cewa, gidan
Sabeer da Sabeer kaddarar ta ne da‘ ba za ta iya 'gujewaba Nan ta mike ta shigar‘ da kayanta cikita yi murmushi ta ce;
~"Shigo‘mu'kintsa gidan,kin san nima ba 'wai na jima da dawowa ~ bane, tashi- ,biyo ni
Sunkuyar da kai tayi ba' ta~' Ce mata komai ba,
‘. nan suka "hau gyare-gyare 'da
kimtsa gidan tsab. Yayin da ta kaiwa Deeda kayan ta daya dakin, ta ce
"Yanzu- Deeda . na‘ ta girma, tana buqatar sirri, don haka na gyara wancan dakin
Deeda ta kwantar da kai a jikin Inna, cikin shagwaBa ta ce. '
"Ni dai Inna gaskiya ban girma ba, da ke zan dinga, kwana. Banso, ni zan mai da kayana dakin Inna. na, za mu“ ci- gaba da zama kamar yadda muke rayuwa da".
Nan ta “mike, "Zan je in dauko kayana".
Inna ta bi ta da kallo, ta ce
"Deeda, rayuwar_ da ta wuce ba ta dawowa, komai ya canja. Duk yadda zaki yi ba za ki iya karBar rayuwar da ki kayi da a. yanzu ba". . '
Deeda na shiga dakin ta. ga yadda Inna ta gyara mata shi tsaf ya sa ta ji sha'awar zama a.ciki, don haka ta ‘fasa daukan kayan, ' sai ma ta zauna ta bude akwatinta ta ciro
wata 'yar Karamar laptop da' ta zo Ta ‘- tuno wannan ita ce kyautar Sabeer da ya fara mata, “haka lookaci' na farko da aka taba mata kyautar da take matukar; so, kyautar da tai mata dadi, ~
" " ‘ '
Bata. Bata lokaCi ba ta'bude‘" shi, hoton tane da na sabeer din ya soma bayyana.‘ . - Gaban ta ne‘ta ji ya harba da Karfi, da ta ,hango kyakkyawar fuskar -sa yana ’mata murmushi, yana mata kallon da bata San ya" 2ata fassara shi ba‘ . '
Ta runfe ido tana tuno Wasu alamura~ da suka,

Wuce. Wannan hoton shi yaSa'mata ' shi "a gaban (screen) din (laptop) dinta da nashi',~ ran da 'ya siyo su. .Wannan hoton. sun. 'dauka ne_ ranar da'suka dita da shi a office" ranar' 'da ya fara nuna mata alamar; yana sonta, ranar da yasa mahaifins'a ya ;yi mata karin girma a kamfanin su.
. Nan tatsinci kantat ,da ,bincika sauran hotunan ciki, a' duk'lokacin da ta ci- karo' da fuskar sa Sai ta ji gabanta ya fadi,' hankalinta ya' tashi.; Ta tsinci kanta cikin wani' yanayo, ba ta ankara ba taji an tsuge da ruwan sama.
~Motsin Inna ta ji tana rufe rufe,. harta ja mata. kofar _dakin ta hakan ya sa ta mike akan gadon, ta lulluBa da mayafin da Inna ta ajiye mata'a gadon, ta kashe (p.-c) din 'ta kwanta. Har yanzu tana jinsa a mata, daga ta rufe ido fuskar sa take hangowa. . Zumbur 'ta'miKe ta sake dauko ' Wani littafi 'tana karantawa, amma' sai karatun ya gagara, tunanin _sa ya zuciyar ta; yanayin sa, halayyar sa, taflyar sa,.maganar' sa su ne 'abinda ke yawo a , zuciyar _ta da kwakwalwar ta; Take ta ji ta tsinci kanta cikin kewar sa da rashin sa. -
Ta 'yi murmushi, "Allah Sarki' Sabeer, ban, so na yi wannan sabon. mai tsanani da' kai haka _ba, ban taba tsammanin akwai ran da zan yi (missing) hallayar ka ba,- ban taBa zata» zan' zauna haka ina (missing) duk .wani' (moment) yanayi' da na yi da kaiba". - ' '
Lokaci guda kuma tunanin Ibrahim ya fado mata, idonta ya ciko- da' hawaye; ta runtse ido. Tunani kala-kala k0 ta ina ta juya. su' take ji a ranta, ko- wanne motsi ta yi Sabeer ta ke'ji a jikinta, yadda yake wuni, kwala mata kira, Deeda, 'Deeda kamar 'Shi ya. sa mata sunan. ' .
Zu'ciyarta'ta ji 'tai mata Kunci, hakan yasa ta. mike da' sauri ta fito ta nufi dakin- Inna, da gudu, ta je 'ta kwanta a bayanta, ' Zuciyar ta na' 'bugawa da qarfi kamar wacce ta ga abin tsoro. Inna na jin ta sai dai ba ta Ce- mata komai ba,_ da hakan ta samu baCci . ya'.sace ta, 'yayin'd'a Innan ta zuramata ido tana jiran ta ga ikon Allah,

Wato, me‘ zai faru a GAYU bayan BacewarDeeda.
'Deeda bata farka ba haf Sai~ bayan azahar Inna ta tashe ta; don ,ta ‘yi sallah, yayin da" ita ta 'nufi kicin don nema musu ' 'abinda zaSuci.
Deeda Zaune kan- sallaya bayan. ta idar da. sallah,‘ tana,karanta addu'o'in ta, ta ji’?‘ muryar yaro yayi sallama, nan ta amsa' tare
da daga kai don taga me sallama
Dam Dam!! . Zuciyarta ta, -'buga da karti, don ganin wan‘da 'ba ta zaci gani ba, a. wani yanayi da ba ta taBa zata ko tsammani ba. '
Sabeer ne tsaye' tare da yaron, hannun sa riKe da jakarsa. . ' _
Ya zura mata manya-manyan idanunsa masu nagarta da kwarjini yana, kallonta, tsananin mamaki‘ya kama ta. " '
Bude baki tayi za ta yi magana amma ta kasa, sai bakinta ke ’motsi alamar sunan sa take kira Kasa kasa motsi tayi
Jakar ya saki, ya nufi wurinta cikin doki da tsananin murna, ba ta ankara ba sai
jinsa -tayi a, jikinta ya makalkale ta yana sauke numfashi gami da kiran sunanta cikin tsananin shaukin so da murya mai kama da rada. '
1"Deeda (I missed you so much) me yasa ki ka tafi ki. ka barni?" ' Kallon sa kawai ,take, tana mamaki.
Shin mafarki- take k0 «ido biyu? Wai‘ Sabeer din ne. a, Kauyen‘ su? '
Inna ma da ke kicin ta fito baki' sake tana kallon "su tana‘ mamaki, duk yadda take zaton 'Sabeer na son Deeda ya wuce ‘ haka Dariyar jin ydadi tayi tana .godewa Allah' a ‘ ranta. ‘ .Deedan-ko tana zauné ta rasa. abin Yi, tana ;.. jin .Sabeér na dada cusowa cikin jikin'ta, ya~ . Kankame ta tamkar wacce yake tsoron kar 'ta
Sake guduwa .ta barshi. .Haka‘kawai‘taji- tausayin sa 'na shigarta, ta sa hannu 'tana Shafar sa gami'da “kwantar da kanta a jikinsa; Cikin murya Kasa-kasa ta ce ' sabeer (please) nanba wurin zUwan’ ‘ka bane,’ wannan' dajin, qauyen ba inda‘ 'za ka taka bane. ‘KWannannan bai dace. da kai ba .Sabeer (please) ka koma".

Ya girgiza mata kai, -.."Ba' zani koma BA Deeda, ba dai zaman' GAYU ne ba kya so 'ba? To, ni zan.-Iya zama ,a ,kauyen ku
"Me yasa ka cika rigima ne?' Wannan fitinar taka shi ne'Wahalar mu"... ' Nan tayi Kokarin janye shi, amma ina Gam ya manne mata tamkar wanda aka lika shi a jikinta. ' . "Sabeer (please) mana". Ta fada cikin 'damuwa -"ni dai ki Kyale' ni, ba zan tashi ba. Kin san wahalar 'da " na _ sha kafin in 20 Kauyen nan ni daya' a (bus)? (I was scared) haka na shiga bayan' akori' kura, kinga duk ruwan sama ya min duka, dubi jikina "fa; kinga yadda na dawo (vry dirty)" Ta zarO-'ido, "Kai kadai ka zo? Daddy da Ibrahim suka kyale ka?" Nan ya dago kai ya kalle ta, sannan ya girgiza mata kai, ya ce. ' ' "Deeda na ne ta Bace' .ba tasu-ba". » Kau da kai ta. 'yi; 'ta ce', 'Tashi - kayi alwala. ka yi sallah,' -zan raka ka ka koma; don koruwan garinnan- baza ka iya Wanka da shi ba balle ka sha".
' Ya Bata fuska gami. da bata rai, ya Ce; "Bazan tafi ba Itama'~ ta bata, rai'Sai ka tafi; in ba ka tafi don dadi ba 2a ka tafi'don Wuya";Cikin daga ,murya da zaeo ido, zuciyya . ta kulershiwa yace 'Ba zan tafi ba, Wai me-ki ka maidani ' ne?,Kuma me ki ka dau kanki? In nan gidan ai 'Kauyen aiba naki bane da za ki matsa 'min in tafi
' Nan fa'_'suka kaure da' fada, Inna ta _' ' shiga :tsakani da 'kyar, ba' su, ankara ba sai jama'a' suka gani cike a kofar gidan suna .kallon ' su, -taron' mutanen, Kauyen tamkar Wanda suka samu ''talabijin. Hakan ya sa
'Deeda tayi; saurin jan Sabeer' cikin daki, sannah ta fito ta Bata fuska tace~. ,"Meye ku ka taru kuna kallo' 'ko baku taBa ganin mu bane?" wani daga cikin 'samarin ya ce.
v"Ke dai mun ,sanki, amma'shi 'bamu 'taBaganin saba, k0 irin saba ba'
Inna ce ta'Sa baki, ta ce, "Mijinta ne, sai 'yaya? Ba dai ku kun canfa taba? To Allah Ya bata-miji wanda 'ya fiku,' kuma za su . zauna na dan' 'wani "lokaci' a gidan nan kafinsu tafi Ko da mai magana?" - '

Suka yi tsit' duka, Inna tace maza su watse
mata- daga gida Kowa ya san halin Inna sarai da
fada a garin, bata kyale kOWa. Don. haka .ba su‘
Bata lokac‘i ba ‘suka fara watsewa mazan su -da
matan su, wasu ma ceWa_ suka dinga wai hala.
dan aljanu neba danmutum ba. Tunani da camfi
irin na mutanen Kauye sai dai Allah Ya kyauta.
A daki Deeda na Kokarin yiwa Sabeer magana
amma bai saurare ta ba, sai ma ya juya mata
baya.- Ta sake shangabansa, a nan~ ta ga Bacin
ranSa da bata taBa gani ba. - -
Tsawa ya daka mata tare da daga’mata hannu,
ya ce
"Ya ishe ki, kinyi . na __farko kinyi na karshe,
karki sake kuskuren ce min ‘in' bar kauyen nan,
‘na ga wulakancin naki da rainin naku gaba yake
In . gidan kune ba ‘ kya so in zauna' zan ‘bar
muku' 'gidan ku, .. amma'ba ruwanki dani da
zama na a garin , nan,
Za tai magana bai_saurare tataba ya fIta. cikin
Bacin rai,Inna mai fura na jinSu, ‘ta kalli-Deeda’
itama nata ran‘a Bace; ta ce‘
' "Me' yasa ki- ka yi~ haka? Gashi' kin
Bata masa rai,‘ kin sa ya bar gidan". "Inna to ya
zanyi ne? Sanin kanki ne
Sabéer ba zai iya jure rayuwar kaUyen nan
ba
' - Inna tace "In haka ne ai sai ki bi shi a
hankali". '
Deeda, tace, "'Inna', kin fasan halin. Sabeer da
rigimaesa, da kaflya, ya zan yi- da shi? Ya fita
kayan sa duk a jike suke ga sanyi', yanzu sai
wani ciwo yakama shi"; Ta fada kamar za tai
kuka'. _ ’
‘ Inna ta ce, "Ai Iaifinki in bar kin .damu
da'shi- .ba' kya .so ya sha wahala k0 Wani ciwo
ya kama. shi, .ai sai' ki
bishi ko kuma. 'Duk abinda ya same shi Iaifin ki
'ne ba na kowa ba". , ‘ ‘
Fashewa tayi” da kuka, Inan ta zari mayafinta
tafi_ta don dubo Sabeer din. A gindin wata'
bishiya ta hango shi zaune ya hada kai da
gwiwa, ya rasa me ke masa _ 'dadi, yara na

kewaye da shi suna kallon sa.
Inna ta isa 'wurin ta kore su, sannan ta matsa dab da shi ta kalle shi, ya kau da kai, ta ce.
"Haba Sabeer, ga cikin gida me yasa za ka' zauna a waje? Kar ka damu da ‘ maganar Deeda".
."Dole' in damu Inna'
Ya bata amsa cikin muryar damuwa, ya ce.
' "Inna, Deeda ba ta sona, rashin Kaunarta ya kai wanda har'ba ta son ganina, tana’ kora ta. Ni kuma na kasa rabuwa da ita, na' kasa jure rashin Deeda. Inna, in ma Deeda ba ta sona ta bani damar tabbatar mata da cewa ni ina sonta, ina kaunar ta", mana
Ya kwantar da kai, "Inna, da gaske nake". _ ‘ .
"Na sani Sabeer". Inna ta fada cikin tausaya masa. '
' Ta ce, "Na sani Sabeer, sai dai Deeda ba kin ka take ba k0 korar ka ba, ta damu da kai ne, ta san yanayi irin .naka da yadda kake rayuwa in ka zauna a Kauyen nan komai zai iya faruwa da kai. Deeda ba za ta iya jure ganinka cikin tsanani ba".
"To in hakane Inna Deeda. ta barni in zauna-kusa da ita, saboda 'lokaci mafi tsanani da Kunci a rayuwa ta shi ne lokacin da na wayi gari ban ga Deeda ba. Innagara kowane irin tsanani da wahala akan rashin zama kusa da Deeda. Inna, kar kice in koma, ki barni, ina son zama kusa da Deeda, ina son kula da ita da dukkan‘ matsalolin ta, da damuwar ta. Ban damu in zauna ko a ina ne
ba in dai zan kasance tare da ita".
Inna ta kalle shi cikin hali na damuwa, ta ce. Sabeer, mahaifin ka..."'.
"Kar ki damu Inna, Daddy _bai san ma Deéda‘ ta gudu'ba', Daddy ya zata mun fita. yawo ne da 'Deeda. Inna, 'mahaifina ya samin albarka, ya yi min addu'a' kafin in taho, ba abinda Zai far dani a kauyennan. Abin - da ku ke tunani ba zai faru ba
Inna ta ce‘, "To shikenan Sabeer, ba zan raba 'ka da matar’ ka ko' hana ka 'zama kusa‘da' ita ba,“kana da' hakki‘ da dukkan wani dama akan matar ka"~. "

Ya yi. murmushi; "Na gOde Inna". Itama dariyar tai masa, ta ja hannunsa; “ "Tashi muje". ' ' " Ya ce,‘;"Inna, ba wani wurin inda ‘zan' '
iya zama‘ a garin nan?" Don me .yasa‘ za ka zauna a- Wani wuri? gidana, :zaka zauna .Deeda ka, rabu- da" ita 20 mu tafi
Nan ta ja 'hannun _sa suka tafi har' ciki. ta ja‘ shi, 'Deeda na kallon su, ta je ta. fito da " kayayyakin Deeda a‘daya dakin da
mata, ta sa na Sabeer, ta Kara gyara masa, ta" sake sharewa. , - '
Ta kalli Sabéer, ta ce.
- "Daga _ yau nan. dakinka ne halak malak, ka zauna har iya tsawon yadda kake so, ba mai' takura maka da matsa maka. Duk abinda” kake so Zan maka a gidan nan in. har bai fi karfina ba. Ka sake kayi ,yadda kake so, gidanku ne'".
Deeda ta saki baki tana kallon ta.
. ."Inna meye..
"Ba ruwan ki". ' '
Inna ta katse ta, ta- qara da cewa.
"Ina da baKO' a gidan nan, Sabeer baKona ne in na ji ko na ga kin kuskura kin Batamasa, k0 kin masa ba dai dai ba, koda: ' kallon da bai gamsar dashiba kika masa ni da ke né.‘ Zaman ki daban', nashi daban".
' .Deeda ta Bata fuska, ".Haba- Inna, me ' yasa kike haka?" . ’ - ‘Sabeer ya yi dariyar tsokana, ya ce." ’Inna, a fada mata kar ta kuskura ta matsokusa dani balle ta ce in tafi, don ~ba - gidanta bane, kuma wurin ki na zo ,ba warin ta ba". _ ~ ’ Inna ta' ce, "Ai ba ta isa tace’ka tafi ba". ‘ Nan ta shige kicin ta ce, "Bari in sa ma ruwan zafl kayi wanka, in hada maka abinci irin na kauye". ‘ . » Nan ta shiga kicin, shi ma ya shiga. dakin, suka bar Dceda baki bude. Sam ba ta so Inna ta daurewa» Sabeer gindi ya zauna 'ba, yanzu ina‘. mafita a gare ta? A nan ta zauna kan tabarma, Inna ta KWala mata kira ta je; ta ce‘_ "maza ki je ki gyarawa bakona‘ bayi zai yi wanka yadda ba zai takura ba, ki hada ' masa ruwan zafl ki kai masa, ki.‘ masa magana ya jeyayi wanka". . ‘

Nan ta turo baki, "Gaskiya ni Inna...".
"Aiki na saki, za kiyi k0 ba za kiyi
ba?" . Inna ta bata rai,‘hakan yasa Deedan ta '
yin abinda aka sa .ta ba don ta so ba. Bayan ta
gama ’gyara masa‘bayin; ta _ kai‘ruwan,
ta'nufi'dakin; ta same shi zaune kan tabarma
a’takure, alamar sanyi yaké ji, . har yanzu
wannan kayan ne a jikinsa. ‘ . Ba .ta kulashi ba,
ta jawo jakartsa' ta bude, :ta ciro masa (towel)
tare da wasu kayan, da 'abubuwan da ta san" zai
buqata. Sannan ta rufe, ta kalle shi. "Ka tashi‘ka
~je~ kayi wanka, ka cire" - wannankayan' masu
sanyin. Ga (towel) nan ' mu je in nuna maka inda
za kai wanka". . , .Kau da kai yayi bai kalleta ba
tamkar bada'shitakeba.’_ ' '- "Sabeer, da kai fa
nake"
. ' Wannan karon baya‘ ya juya .mata, ta harare
shi,arantatace. ' "Yau kuma miskilancin' ne ya
tashi, amma nima aina iy shi
Nan ta sha gabansa, ta‘ sa hannu ta ’soma
ciremasa'rigar sama.Meye haka?"
ya fada Itama ba ta‘ kula shi ba, yaCe. , - . "Ina
da hannu, zan‘ .iya bana son alfarmar ki"
. . ~ Ba ta saurare'shi ba',Taci gaba’har ya ‘
zamana saura‘best, a nan‘ ta tsaya. '
' ‘ Ya yi dariya, ya ce"'Shima ki cire “mana, in ki
gama Wandon shima ki cire".ta
‘ 'Harareshi ta yi kWafa, ta' wurga masa (towel)
din ta fita..Ya fashe da dariya, Deedan ta'fita
tana- mita.
' . . "In kaga dama kar kayi wankan, ka zauna
haka; ina ruwana‘Inna tace"keda Waye?'-" ‘ ' Ta
amsa da, "Ni da dan gatan bakon ki ‘ne, ina jin
ruwan wankan ‘ma daki ~za'a kai masa". Inna
tayi dariYar zolaya‘, ._','Toce toba sai ki. ‘kai
masa ba",im .Kafin ,tace wani' abu Sabecr '_.ya.
fito. Ihu’deeda ta'kwala gami' da zairc ido,
ganinSa daga shi sai daure da . gajeren taWul,
tace a haka zakaje wankan?????
birnin gayu
chapter18
saurayi da shi, duk jiki amurde. '
Ta mike da sauri, "Kai Sabeer...".

Jin ihunta yasa Inna mikewa za ta‘ fito ganin
haka ya sa ,ta mike da sauri ta je ta tsaya a
gaban sa tana kokarin kare shi, sai dai duk da
haka bai sa ta'iya kare shi ba, don kuwa ya f1 ta
nesa ba kusa ba, namijin gaske ‘ne, tsawon sa
ma kadai ya isa. Jiki ne da shi irin na jarumai.
Ganin su a haka yasa Inna ta fahimci manufar’
Deedan, .ta kada kai tayi ciki tana dariya. ’ , ’
Bayan Inna ta shige Deeda ta harare shi garni da
jan hannunsa, tayi bayi da shi tana masa mita,
"Nan ba (bathroom) din gidan ku bane; ba a
tsakar dakin ka_ kake ba, nan gidan mata ne ka ji
k0? Ko kunya ba kaji kana bude mana jikin ka?
Nan kauye ne ba Birni ba...". ' '
Zura mata ido yayi tana ta surutu, nan ya yi
saurin kai hannun sa bakinta, ya ce.
"Bakin ki ba ya gajiya da magana? Gidan mata
nake," su waye matan? Mata ta ce da'kakata,
don haka kar ki yarda kice za ki koya min'yadda
zan yi rayuwa ta".
'- Wani kallo' tai masa, ya ce.
"K0 Karya nake? Deeda mata tace dubban jama'a
Sun shaida, kuma ba laifi bane don mata ta ga
jikin mijinta".
'Juyawa tayi za --ta tafl, ya jawo hannunta da
Karfi. ' ' ‘
"Ina zaki?. Ai tunda kika- rakoni wankan ma'sai
kin min".
"Sabeer, ba ka'da hankali, ka sake ni".
Meye rashin hankali a ciki? ~Ni fa ba zan sake ki
ba". _ _ " Nan ta hau kokawar kwaCe hannun,
amma wane .ita. Sai da ya gama zolayar ta
sannan ya sake 'ta, ta gama kula,‘ ta tsaya tana'
mishi masifa. Nan ya yi maganinta ya soma
kokarin kwance (towel) din, tuni ta fito aguje,
zuciyar tana bugawa, tana sauké ajiyar zuciya. " .
Dariya ya‘dinga mata,ya ce, "Ai 'da kin tsaya";
‘"Zan yi maganin ki ne". ‘Nan ta fice Waje, can.
ta‘dawo da‘ wasu yan matan' 'kauyen
ta'Shimfida ‘musu tabarma. atsakar gida, suka
hau hira, tana -baSu 'labarin Birni, su kuma
sunata mata tambayoy'i. Sabeer k0 da kyar Ya
,iy‘a yin wankan, saboda wani irin iska mai

sanyi_~da ke kada shi,-gashi bayin fili ne 'ba ko
rufi Tuni ya hau rawar sanyi, yana Allah-Allah ya
fito. Yana zuwa dab da qofar fitowar kuwa ya ji
surutun 'yan mata, da sauri ya koma, ya rasa
ya'Zai yi yafita. Deeda na lekensa, da ,suka'
hada'ido ta fashe da dariya tana masa gwalo. ‘
' .. Ya langwaBé kai yana ma ta al;.amar
‘ (please)‘ta 'zo. Ba‘ta musa ba taje ta same shi,
ta juya masa baya. ' "Meye?"> . Ya ce, "Deeda
sanyi', ina son wucewa
ga 'yan’matan nan, 'ya zanyi in wuce?"
Ta yi dairyar‘mugunta, "Ba kana Son yawo .a
tsakar' gida da tawul__ ba? Kar ka damu, 'yan
mata 'ne, hala su ma matan kane?"
Nan ya sa hanuu ya finciko ta da Kardi
yace Ni kam ba mata, na bane, Deeda ce kadai
mata ta, k0 dai ki sallamesu 'su tafi 'ko kuwa
muyi ta, tsayuwa inyi bargo da' ke a nan, da ki
min maganin sanyi na".
Nan ta' hau kokawar kwace jikinta, amma ta
kaSa. Ganin 'ba yadda ta iya yasata fara roKon‘
sa. .
, "Haba Sabeer dina, nice fa Deedan ka, (please)
ka sake ni, so kake sanyi ya kama ni
inyi_'zazzabi?
. -. Ganin yadda ta' marairaice ,masa tana mai '
shagwaBa yasa ‘ sa shi mutuwar jiki Wani iirin
sonta ya ji-yanaratsa masa jiki da jijiya, ya
lumshe ido yana kallonta, bai ki su tabbata a
haka ba. Ganin haka yasa Deeda ta
ture.‘ shi; ta kwace jikinta ta- gudu ‘tana masa
dariya da kwalo, yayin da ya' harde hanan a kieji
yana kallOnta, Iskar dake ratsa shi ya ji
yana'masa dadi, saboda- hade yake da sanyin
son Deeda. -tsiyar da Deeda ke ma Sabeer' yasa
tafito ta sallami 'yan matan, sannan ’ya‘
‘samu'ya wuce, yana kallonta tana kallonsa, tana
masa dariyar' tsokana, yayin .da shi bai gajiya da
ka‘llon ta,”bai',Ki suyi ta zama‘a. haka ba bai iya
gajiya _da kallon ta, bai iya 'gajiya‘ da Kaunar ta.
- 'Ya, shiga ciki, kwanciya ya yi a hakan har
sai'da Dceda tashigo kawo masa abinci .ta same
shi a- hakan. Bata kulashi ba, 'ta jaWo jakar ta

bude ta duba masa kaya tare da- ciro ‘masa
(body oil) da yéke shafawa, da dan kayayyakin sa
na amfani ta ajiye masa,»tace. ‘ . - "Idan' sanyi
ya- “kama mutum nan "Kauyen ba' mu'da ko'da
‘(Nurse‘)ne balle likita, haka ko teburin sai da
magani. bamu
da shi balle kantin sai da magani.. Ka rufawa
kanka asiri ka sa kaya".
‘Yana jinta ya share ta, .sai ma gyara kwanciya
da yayi ya juya mata baya.
“ Magana nake malam"
" Ta fada a qule, ya ce. '
‘ "in har ba za ki' iya min magana ta harce mai
dadi ba nima ba Zan kula ki, kuma ina ruwan ki
da ni? Ko sanyi ya kama ni k0 kar ya kama ni
jikin ki k0 naWa?"
"Oh Allah
Ta .fada gami da» kama kai,_ wato rigimar
Sabeer tafi ta Karamin yaro.
Hannu ta sa ta-jUyo da kansa, ta yi murmushin
yake.
"Ranka ya dade, Yallabai Sabeer, tashi ka‘shafa
mai, ka Sa kaya, (please)". ‘ .
‘ Nan ~ya mike yana dairyar tsokana, ya ‘ce. - '
ai."Tunda ‘har kin: roke ni. ai ba zan' Ki ba"
nan ya fara shafa man, ta‘ harare shi
gami da girgiza kai, ta fice ya 'bita da kallo yana
dariya. ' '
Bayan‘ ya sa kaya ya fito 'ya yi alwala ya yi
sallah a inda ya ga Deeda ta shimfida .. masa
sallayar, "
Yana' zauna kan sallayar, bai jima ba ya ji 'an‘
kira la'asar. Bayan ya ,idar' ya jima‘ ' yana zaune
akan sallayar yana kallon tsakar dakin da yake
zaune. Wuri 'ne da _bai taBa tunzini ko zaton 'zai
iya. koda minti daya a ciki ba, balle ya iya zama
a ciki. Amma yau 'wannan wurinya fi masa k0
wan wuri'kyau da dadin zama. , _ ‘ Nan ya mai
da hankalin sa ~kan abincin da Deda ta kawo
masa; ya sa hannu ya>bude langar, shi
dai_'wani. abu'ne da bai gane mene ne ba, don
bai taBa gani‘ba. Nan ya zurawa langar ido yana
Kokarin ' gane mane ne' Lokacin 'Deeda ta daga

labulen dakin ta‘ .shigo, ta zauna a gabansatana kallon sa, ta Ce, .
"Na san baka' san mene ne ba; ba ka
taba ganin irin wannan abincin ba a rayuwar ka. Ga wannan, fara sha, na san dai shi ka taBa gani. Madarar shanu ce Inna ta sa na dafa maka, a damunar nan da kyar na samu itacen ya kama, don haka ya zama dole ka sha. Sannan wannan abincin kuma dambun shinkafa ne da zogale, a garin nan 'masu gata ne kadai suke , samun sa. Don haka Bisimillah, in ba haka ba yau kayi kwanan yunwa".
Ya harare ta, ya ce, "Wai ke ba za a iya magana mai dadi da ke ba? Ba za ki iya tausasan kalamai ba wurin magana?"
"Ba zan 'iya ba, Saboda zuciya ta bata cikin dadi da taushi, ganin ka- a Rauyen nan a gabana yana'kona min zuciya, kana sa ni ganin laifin kaina, ina jin kunyar kaina. Saboda gani nake ni na sa ka a halin da kake ciki. '
Sabeer, na rokeka ka sauke min nauyin auren ka da ke kaina, ka' bar wannan rigimar taka, ka koma. Ba yadda za'ayi mu
rayu tare ni da‘ kai, duniyar mu ba daya bace. Sabeér, ba na sonka, ba ka Sona, ,an tava rayuwar aure ba soyayya?"
Tuni kalaman Deeda suka fusata shi, suka tunzura 'shi, ransa yai mugun- Baci, wani‘ irin takaici- da 'bakin ciki Suka lullube shi; ' Ya rasa- me zai ce mata? Wai duk wannan abu da yake ji game da- ita'Deeda tace ba ya sonta? ~ ‘
Mikewa ya yi a fusace ya fita, ya bar dakin. Ta bishi ta na kira
"Sabeer!". .
Waje. ya‘fita, Inna“ tana kallonsa; ba ta ce komai ba har suka bar gidan tana kiransa bai kulata ba har sai da-ta’sha gaban sa, ta tsai da shi, hakan ya ‘bashi damar 'damko‘ta yayi mata riko mai tsauri. gami da zare mata jajayen idon sa, cikin fushi ya ce. .
"Ya ishe ki, ba kya ,sona na ji na yarda, kar ki so ni, amma ba ki isa ki hana ni son ki ba.- wannan abin da nake ji a zUciya ta game da keba ke

kikasamin ba 'Allah Ne
ya sa min, don haka ke ba ki isa ki cire' min abinda Allah Ya Sa min ba, ba ki isa ki hana ni abinda. zUciya ta ke so ba. yau ya zama na karshe da' za ki karyata son da nake miki. "
-. ‘ 'Idan'har kina tunamin zuwa na KauYen nan in zaune da matatace da' ‘fltina ta Ce, na ji. Idan .kina tunanin barin Daddy, Sister da Uncle 1b, na‘gaba ‘daya da aikina,’ da rayuwa ta gaba daya - inzo kauyen nan rigima tace toki sani aurenki da zama da. ke shi- ma rigima ta ce, kuma ba wanda ya isa ya "hana ni zama kusa da ke a duk inda' ki. ke' sai Allah,’ sai mutuwa, k0 ke kanki .ba ki isa ba. 1' In ba kya sona kar ki kalle ni, kar kije 'inda-nake, kar ki ‘komai, amma ni zanje inda ki ke, kuma zan kalle ki, zan so ki iya son’ raina. 'Idankika sake kokarin Karyata? soyayyar da nake miki, k0 kuma ‘fassara shi 'da Wani abinda ba mé'anarsa .ba kenan, za ki yi dana sani. Kar ki sake kula ni ko'shiga harkarta, kinaji'na- k0?” " Yana gama fadi’ ya-cillar .da ita'gefé guda," sai da ta kusa faduwa, ta ji kanta’ na‘ *sarawa.; Ta, tsuguna a ‘ wajen, shi kuwa 'ya‘ wuce ya barta, k0 juyowa bai sake ba ‘ balle ya kalle ta. ‘ ‘Yayin da ta bude baki za ta kira shi, amma sai ta'kasa. 'Tuni, hawaye suka' zubo 'mata; hankalin ta ya tashi, komai ya shige . _mata duhu. Wannan sabon‘halayya'da sabon.» yanayi ' na Sabeer da ta gani ya firgita ta. Addu'a ta- dinga yi a cikin zuciyar .ta don samun. sauki daga . tsananin da ta tsinci kanta, Yayin da ta mike daga ba’ya‘ ta bishi Ya zama dole .ta kasance tare da‘shi k0 tana ' ' so k0 bata So, muddinyana kauyen ba za ta . iya kyale shi ba. , . " '
Al'amarin Sabeer kuwa haka ya yi ta za'gaye cikin kauyen‘, ‘duk' inda ya_ wuce jama'a sai ‘ya. ga sun taru suna kallon- sa, har ya soma sabawa da kallon 'da suke masa;
’ " Wasu "yan yara .ya"samu suna zaune,’ ya zaune cikin su yana ta Kokarin hira' da su da irin ta su ’Hausar. -" .Wayar sa ya dauko ya kunna yana nuna musu hotunan- Birni, . da yadda

gidajen Su suke', da video irin na yara dai. Nan kuWa Suka taru akansa har da layi tamkar wanda suke karBar‘ wani abin. Haka. ya - dinga‘ daukar su; hoto yana nuna musu" suna ta‘ mamaki,.;yayin da suke ta salle da murna tamkar Wanda ya yi musu kyautar wani abu. _ Ya jima a cikin 'su' yana mamakin rayuwa irin tasu, bai taBa tunanin akwai mutane 'irin' haka a wani wuri da suke rayuwa haka ba. . Haka kawai sai ya ji tausayin yaran da'sune manyan gobe sam ba su san ma meye wani rayuwar jin dadi ba, ammé duk da hakan hankalin su kwance, suna murna a tasu "duniyar, duk da ko duniya ta manta da su gaba daya, suna gefe. ‘ Tuni zuciyar sa ya ji yana son yi musu wani abu, yana son kyautata musu rayuwar su,‘ to amma me zai iya'musu? Shi ne abinda
yake tambayar kansa, bayan shi kansa bai taba yiwa kansa komai ba balle ya yiwa wasu. ' Take ya ji zuciyar sa ta masa nauyi, hakan ya sai’ ya'yiwa yaran dabara yace zai 'dawo gobé su' sake hira, 'su kaishi yawa‘a Kauyen. ‘ ’ ~ ‘ ‘ "Mijin Deeda sai gobe". Hakan ya sa ya jUyo ya'tsaya yana kallon yaron, take k0 yaran ‘suka duka suka " dau soWa, "Mijin Deeda!". Sunan da suka sa masa kenan. Murmushi ya yi duk da zuciyar sa ba dadi, ya shafakan yaran ya wuce. ' , Deedan tana ‘ tsaye daga nesa tana kallon su, lokaci na farko tun haduwar ta da Sabcer data ji ya birge‘ ta.. ~ ‘.Tabbas' Sabeer bai, iya mu‘amala da mutane .ba, amma yadda ta ganshi yana yi da yaran nan ayau sai ta ji ya burgeta .. Ta bi shi da kallo tare da tunanin ina kuma zai yi? Kar .ya bace mata. Hakan yasa
ta bishi.
Ga mamakin ta sai ta ga ya nufi gindin gadan nan da take zuwa tayi kuka a duk lokécin da‘take cikin damuwa ko kadaici.
- Wuri ya nema ya zauna yana kallon _ruwan da ke gudu a Karkashin gadar, yayin da tunanin gida. ya fado masa. Haka nan ya tsinci kansa cikin kewa da kadaici.
Nan ya hada kai da gwiwa, tsananin son Deeda

ya_ ji yana shigar sa, yana ratsa jiki da zuciyar sa.
Hawaye ya gangaro masa, "Wayyo ‘Allah! Wannan so da ciwo yake, Ya Allah Ka dandanawa wannan baiWa taka ko da rabin abinda nake ji game da itane, hala za ta gane cewa sonta nake ba rigimata bane
. Deeda da ke gefensa ta ji zuciyarta ta mata kunci, tsananin tausayin sa ya kama ta. Ba tasan lokacin da‘ ta isa gare shi ba, ta sa hannun ta bisa kafadar sa tare da kiran sunansa cikin sanyin murya., ‘
' "Sabeer", ,_ , _. Ya dago kansa da sauri suka hada‘ ido, ya mike ba tare da ya kula'ta ba, ya juya ya'. ,_ .tafi Ta'bi shi tana kira, amma bai saurare‘ta ' ‘ba balleya tanka mata,’ har suka isa gida. ya samu Inna 'zaune' ' a' - rumfa, . hankalinta tashe ta ce. ’ 'Sabeer, ina ka shiga duk na damu?" "Inna, ba zan Bata ba; ni ba yaro bane. Na zaga inga Kauyenne kar ki damu na san me nake, ki yarda dani-". . _ . ‘ ,, _ "Na yarda da kai Sabeér, sai dai duk da haka dole in damu, bana son- ganin ka — Cikin damUWa" Ya yi. murmushi‘tare ‘da .durKusawa ‘ gaban Inna, ya ce Inna tana tare da,.ni ai bani- da .. ‘ sauran damu‘wa, Na‘san hanya, duk inda na" .je zan dawo, sannan ki .cewa Deeda ta ‘daina 'bina' duk inda na . Shiga, .bana bukatar. maigadi .ko — kulawar. ta, zan ' ‘iya 'kula da 'kaina ‘ ' ‘ '
Inna ta ce,‘ "Na san kana cikin fushi, kayi hakuri, dole sai’ an dinga samun' irin saBanin. da‘ Bacin rai wani lokaci‘, kafin mu kai ga'cimma‘ burin mu, k0 sanin matSayin mu da muhimmancin mu a" rayuwar‘ ‘wasu. Ina fatan 'ka fahimce ni? Sannan ga madarar nan na sake dafa'maka ita, ka daure ka sha Sabeer, ka ga akWai’sanyi.‘Ab incin ma kaCi k0 kadanne don ka samu Karfin jikin‘ ka".. '
‘ Ya yi murmushi, ya karBa ya ce, "bari ‘na shanye yanzu ma kuwa a gabanki"'. ' Nan" 'ya rufe ido ya kafa kofin a bakinsa, sai da ya Kare‘ ya dire, yace "Alhamdu lillah"._,, , .ta' abincin yace, "Kinga shima ‘a gaban- ki zan. ci..

Kullum‘daga yau tare da' Inna ta zan dinga cin abinci, duk lokacin da‘ naji kewar Sister da su Daddy zan zo wajen Inna.mu sha hira. In ina tare da ke zan'ji kamar ina gida ne"., ~ " Ta yi dariYa, ."Dakyau Sabeer. Allah
Ya maka albarka"yace Amen
' ‘Kiran sallar magarib ya'katse musu hirar, .ya tashi‘ ya yi' alwala, Inna -ta masa kwatancen masalla‘ci ya -taf1, itama tayi alwalar. '
._ , _~Deeda tana tsaye tana jin su,‘ ta‘rasa me ke .mata dadi, musamman ma da ta .ga. Inna "ta‘ kau' da 'kai gare ta, ko kallontar bata‘ yiba Alwalar tayi’ itama ta shiga’ daki kusada‘ Innan ta yi sallah.
' _ Bayan duk. sun idar da. ’salllar ma Inna‘ ba ta kulata ba, hakan ya sa ta fashe da kuka, ta fada cinyar ta.
'Wai Inna me na muku ku ka tsane ni?"
-‘ Inna ta’ ce, ~"Mu ba mu tsane Ki ba, mu masu Son ki ne Deeda, sai dai hala ke kika tsani kanki. Deeda, k0 ba‘ ki ‘da. zuCiya a cikin kirjin; ki, yakamata ki duba; kokarin yaron nan duk abinda yayi saboda kawai ya -zauna da ke rayuwa baki gani.
Deeda, ba a duba fuskar mutum ace ba a son sa,‘ duk mutumin da ki 'ka cewa ba kya sonshi ba zai taBa mantawa, da shi ba. Sannan a rayuwar yanZu ina mutum yake samun mai sonsa haka? Duba da kyau ki 'gani, Sabeer in yana so ba irin kalar macen da ba zai samu ba, saboda Allah Ya azurta shi. da komai, abinda bai da shi ta hanyar halayyar sa' yana KoKarin gyara kansa da halayyar sa yayi iri daya da ’naki, da yadda ki ke so, amma ba kya gani, Abinda na lura,’ na fahimta shi ne kece me fitina da rigimar ba Sabeer ba, kece mekafiya, ba kyaso~ ki amince ki yarda mahaifin Sabeer Ya .yi nasara akan ki, ya miki dole kin auri dansa, kin auri wanda ba kya so. '
-Ibrahim ki ke so?‘ Deeda Ibrahim ya miki nisa, yana da. ‘mata da' rayuwar_ sa wacce‘ ba ke a ciki. Kina tsammanin in Sabecr ya sake ki Ibrahim zai' aure ki?‘ Kina tunanin za ki iya rayuwa nan

gaba matsayin matar Ibrahim: ki rayu tare da yayar. Sabeer ne
da Sabeer gida daya?
Deeda,' tunda' aka .haifeki- nake fata da addu'ar Samun miji nagari; ma1 sonki, wanda 'zai 'mutunta ki, ya darajaki Idan' yau Allah Ya baki miji irin Sabeer, da soyayyar miji irin na Sabeer, saboda tsananin addu'a ta 'ce Allah Ya dube ki da idon Rahma Ya baki miji amman kina wulakanta 'shi? '
Ni dai ina' gargadin ki .da ki bi a hankali, ,kar 'soyayyar Ibrahim ya makanr dake, ki manta da sanin'ki da addinin ki. Ki,sani Sabeer mijinki ne, ki san haKIkin mijin ki da ke kanki,kin san'illar mijin ka yayi fushi da kai', kin san illar Batawa mijin ki rai da kuntata masa. Idan ki 'ka mutu a wannan halin bai yafe ba kin gama yawo, gara ki tuba,~ ki tuba, ki 'rokeshi gafara kafin dare yayi more ki 'Idan' kin san za ki' masa' magana' ta Sacin rai ,gara ki ,yi shiru ki kyale shi, kar ki kula shi. Kuma na maimaita Sabeer bakona ne, karki sake
kuSkuren Batamasa",
; Tana gama fadi ta mike don yin Sallar nafila.
- ,. Deeda' ta fa'she da' kuka ta rasa-me ke ma'ta dadi,- tsoro ya shige ta --'Fadan Inna ya shige'ta sosai, 'ya yi tasiri _a zuciyar ta,.har ta yi dana sanin guduwar datayi.
Shin yanzu ya zatayi? Gashi Sabeer na fushi da ita, 'ko magana ba ya son' mata balle ya saurare ta. ' .
" , Haka .ta;.kasance cikin .'rashin' 'dadin zuciyahar sukai. isha; ta zauna kan sallaya tana addu'o'ii ta ji 'shigo'war Sabeer. Da sauri ta shafa ta mike ta fita, amma sai ya dauke kai kamar bai ganta ba,'ya shige daki, '
' Haka'. t'a dinga kaiwa. da 'kawowa a tsakanin 'dakin' Inna da inda_ Sabecr din yake,maa bai fito ba.' ' -
Can ya'leKo dakin Innan yayi'mata sai. da~ safe; 'yacé zai 'kwanta don duk a gajiye yake; 'Deeda; ,na kokarin' yi masa magana amma baibata dama ba. Inna ma

dai shafa mantaleta »tayi a kafafunta dake. mata ciwo‘, ta kwanta. ta "Kyle Deeda .a wurin. :
Abin duniya ya ishe ta, haka ta dinga juye-juye, ta kasa bacci. ' .
" 'Abinka da damuna, basu rankara’ ba sai ruwan sama ya sauko .da iska mai Karfl, Sabeer na kwance a daki yana ta ,juye-juye. ya kasa bacci, saboda Wani irin ciwo-da jikin sa kemasa, ko ina ya yai masa tsami . Ga gadon bunu, bai saba kwanciya akai ba.’ .
Nan fa ya sauko kasa, nan kuwa sanyi da danshi saka masa sallama, ga feshin ruWan sama. ‘ ’ Wani‘ irin sanyi ya ji na ratsa shi, ya mike da-sauri, nan kuwa‘ guje-gujen Beraye suka yi masa sallama. ‘Yayi saurin hayewa ’saman gadon ya zauna ya takure waje daya, tuni ya fara rawardari. , . ' .. , ZazzaBi mai tsanani ya lulluBe shi,’ tsoro da fargaba ' tare ' da kewa, da, tsananin kadaici
suka dinga shigar sa, son Deeda da tunaninta ’suka cika' masa ‘zuciya. Tuni hakoran sa‘ suka fara hadewa, bakin sa ‘na Bari saboda tsabar sanyi. ‘ . '
.Deeda ’hankalinta ya kasa kwanciya.
"Ya 2ama dole in leKa Sabeer inga a wane hali yake? In naga'idon’ sa biyu, sai na ,ce" 'masa ‘na ‘ zo rufe ~'window' ne saboda ruwan sama. In kuma? ya yi bacci inga a Wanne hali- ya kwanta? Kila ma bai yi addu'a, ba bai sa kayan bacci ba, bai lullubeba. Na San halin Sabeer komai sai an masa".
. Da wannan tunani nata ta nufi dakin.
A hankali ta tura Kofar dakin, hannunta rike da (torch light) tana haskawa. KaSa-kasa saukar numfashi ta ji da karfi, da karar hakoran sa dake haduwa.
'Zuciyar ta ce-ta tsinker, ta yi saurin haska shi. Halin da ta ganshi ya mugun ta da mata hankali, da sauri‘ta nufe shi, ganinta ya sa ya' yi saurin fadawa’ jikinta. Tsananin zafin jikin sa ya 'ruda ta, ta rasa abin yi, sai
sunan sa da take kira;'Sabeer, me ya same ka?"
_.: ‘ Ta'yi saurin ,taBa kansa, ba shakka zazzaBi

ne da‘ mura sukai ‘ masa mugun kamu;
"Sanyi Deeda,’ IulluBeni". '
Abinda yake fadi mata kenan, amma 'ita kanta ta San ba zai masa maganin sanYi ba. Gashi ba su da wani babban bargo.
"Inna . Iillahi wa inna ilaih‘i rajiun'! Sabeer ya zan yi' da kai ne? Dama abinda nake gudu kenan". ‘ -
‘ Ta mike da sauri ta ja window ta rufe, haka. Kofar. ta'cire hijabin da ke jikinta ta yafa masa, amma duk da haka bai bar rawar ‘sanyin ba. Nan .ta dauko tafin hannunsa ta dinga gogawa da karfi, Gaba daya ta rude ta rasa abin yi. _ .
"Deeda‘ sanyi". Abinda kawai yake fadi kenan. ’
. Ta fashe‘ da kuka, "Ya zan maka ne Sabeer, dama abinda nake gudu' kenan.
Ruwan sama ya buge ka, ga iska, ga sanyi irin na kauyen nan, gashi bani da maganin da zan iya baka. Sabeer, ina tsoron kar wani abu ya same ka". '
Addu'o'i ta shiga tofa masa, gaba daya kwakwalwarta a juye take, ba ta da sauran nutsuwa balle ta san abin yi. .
"'Bari inje: in ta da. Inna k0 za ta‘ taimaka". ‘
MiKewa tayi zatai Waje, ya jawo ta ya rungumeta sosai tare da kokarin shigewa jikinta, murya Kasa —Kasa ya ce; -
"Deeda kar _ki‘tafi ki barni, (please) ina buqatar‘dumin jikin ki". ‘ _
Ba ta da zafi a 'wannan Iokaci da ya wuce tayi yadda za ta taimaka masa ya dawo hayyacin sa. A hankali ta dinga goga jikinta a” cikin nasa, sun yi gOgayyar jiki sosai, wato (body‘contact), duk ilahirin jikinsu sai da ya hade tun daga fuska har kan kafafuwan su.
Dumin jikinta ya ' matukar taimaka masa ya dawo hayyacin sa, ganin ya daina
aima admin uzuri jiya baiyi post ba
baiji dadi bane
luv y'll
shared a profile .
birnin gayu
chapter19
rawar darin yasa ta zare jikinta daga na sa. Da

Kyar‘ ta iya zare hannunta‘ daga cikin nasa, ta mike ta duba cikin kayan sa, a nan ta samu'safa, hula da rigar sanyi, ta koma dakin'Inna ta dauko mantaleta ta zo ta shafa masa a _taf1n kafa, sannan ta sa masa safa tare da hular. -
Wurin sa rigar sanyin ne»_ ya farka, ya yi saurin kwanciya ‘akan cinyar. ta, ya' dunkulé guri guda ya kamakai, 'hakan'yasa ta gyara masa rufara, ta' cire hular tana' matsa masa kai (massage) 'da kuma gefe da gefen kansa har bacci ya. dauke_ shi yana kankame da ita. Haka ta dinga kula da shi da kowane motsi nasa, ta dinga daddanna masa- jiki har itama bacci‘ mai nauyi ya dauketa; - . Tabbas Deeda , tayi laushi daren, kula da miji irin Sabeer ba wasa bane, saboda Sabecr irin mazan' nan ne da Bature ke kiran su da' (giant) sai-dai bata yi wahalar banza ba, don kuwa Sabeeer ya samu sauki‘
Dukkan. Su basu farka ba Sai da gari ya yi baske, Sabeer ne ya fara bude'ido ya ganshi kWanCe jikin Deéda, ta rungume shi da kyau. ‘
. ’Ido ya Zuba mata yana kallonta,‘ ya yi murmushi ta're da. karé shigéwa jikinta.
"Deeda, me yasa ba‘ za ki bari' mu rayu tare'a haka ba? In kasance tare da ke har abada? Ya' zama kownane motsi zanyi inji ki a jikina?" . ~ .»
‘ -
Haka ya‘ - sa mata ido, baya ' ‘ko KWaKkwaran motsi don kar'ta tashi , Bai tashe ta ba har Sai da ta ,tashi don kanta, ta ci karo da fuskar Sabeer‘ya sa mata ido, haka’ kawai ta" tsinci kanta da 'masa murmushi; Sai kuina ta yi saurin‘ janye shi a jikinta, ta mike da sauri, sannan tai masa ya jiki? Bai bata amsa ba sai kallon ta da yake, yasamata ido
‘ Ya'miKe ya nufe'ta tare da kai hannu yana "shafa fuskar ta 'tare': da saman qirjinta, ya ce ~ "Tsarki ya tabbata ‘ga Wanda ya ‘Yi wannan halittar". ‘
Sai lokacin ta lura: daga ita sai dan shimi ‘da tsayin sa bai wuce cinyarta ba.‘ Nan ta yi saurin kankame jikinta tare da zare zaninta da-ke yashe a Kasa, 'ta yi saurin daUrawa‘, sannan ta Zari

hijab dinta ta saka, ta fita da_sauri. Ya bita da kallo, sannan ya zauna ya lumshe ido yana jin wani sabon sonta da sha'awarta na shigar sa. Gaba daya .ta gama'ruda shi,' a kullum shi Deeda yake so; halayyarta da yanayinta, da fuskar ta, amma yau ya ji yana mugun kaunar Deeda'da sha'awar ta. Hakan ya sa ya Kara tabbatarwa' da kansa zai iya jure'komai don ya rayu tare da Deeda. _ '
' Gaba daya jikinsa ya mutu, ya ji ba ya son yin komai sai' dai ya kWanta ya yi ta tunanin ta.'
A hankali abinda ya faru a daren jiya ya dinga dawo masa. 'Murmushi ya dinga. yi yana sauke ajiyar 'zuciya da numfashi mai
hade da zafin so da kauna, tare da tsananin sha'awa. " _ '
Hakan ya faru da Dceda, ta_f1ta ta tsuguna a rumfar gidan zuciyarta na harbawa .da Karfl tamkar wacce tayi tsere. In ta rufe ido gogayyar ta da Sabccr ta ke tunowa, yayin da take jin shafar da ya mata a yanzu.har cikin ranta. Wannan ya saukar da rudani tare da bakon yanayi a zuciyar ta. '
"Deeda?" Inna ta kira sunanta. ' '
Ta mike a firgice
"Lafiya ki ke zaune a nan da sassafen nan? Ga ruwan zafi can na hada ko'kuna da bukata". '
Deeda kanta sunkuye ta ce, "To".
Innan ma- wucewa tayi ba tare da ta tsaya mata dogon bincike da tambaya ba.
Da sauri ta mike ta hadawa Sabcer ruwan wanka da alwala, 'ta'nufi dakin.- Ba ta yarda sun hada ido ba, ta ce
"Ga ruwa can inza ka iya waka, don na ga da sanyi'. In wankan zai maka wuya
yanzu Sai kayi alwala 'kawai', sai 'ka hanzarta 'don mun makara sallah.". Kafin ma yace wani "abu ta" fice da sauri'murmushi ya yi. ya mike, ya fito.' Ya: lura da wani Sabon salon jin kun'yar Sa data fara. . ' " ' " "Duk da dankaren, sanyin da ake bai hana . shi' yin wankan ba,' wannan ya' bawa Deeda "damar dawoWa ta shiga ta tattara dakin, ta gyara tas, ta ciro; masa kayan 'da zai

sa, ta tattara. masa kayansa da ya ‘watsar, . Ta girgi‘za kai, "' "san yaushe Sabecr.zai.
koyi’tattara kayan sa da kula Nan ta ‘fita da su don wanke'wa. _. ‘ _ ’ Bayanya fitone-‘ta-samu .damar shiga tayi ‘nata -wankan hade da alwala. A daki kuWa .Sabeer ya, lura da yadda Deeda ta kintsa’dakin hatta salla‘ya da kaya tare da’man da ‘zai shafa .duk ta ciro masa.
sauri.
Kaunarta Ya Kara ji ta ratsav shi, yace "Deéda daban kikeda sauran, kin can can ci ‘a jure kOwane irin wahala da matsi, da'kowane irin yanayin rayuwa_akan.ki'.'.' ‘ ‘ ‘ _. . _Bayan ya kintsa ya _._”fito don 'gaida Inna,~ a'kicin ya Same ta tana; 'kokarin hUra wuta. Nan ko ya sa hannu yana taya ta, Inna, tace. ' . ’ .‘a.a sabeer wannan 'ai ba aikinka bane, fita- ka jirano yanzu zanfito", Ya yi dariya, ya 'ce, "Inji waya ce ba aiki na. bane? Kece ma‘ za'a‘ ce. ba aikin ki ba, kina gani na sabon jini,‘ idona lafiyayye, ke kuwa’ 'idon irin na tsofaffl, duk ya 'zama. maneji".
Ya‘fada cikin zolaya. . “ Ta yi dariya ta ce, "Wato abin naka ma harsa.zolaya ,ce, ko? To idanun'nan nawa' ,da kake ' gani. sun nake garau suke sunfi naka karko.ku yaran ‘yanzu meye-naku. me karko da kwari? Nifa’ I'nna ban 'yarda ba. idon Deeda
kuwa kin san ba mai irinsu a duk duniya, ita kadai Allah .Ya. yiwa baiwa da ‘irin Wannan idanun. Ki tashi kawai' ni zan hura". . ' Nan ya: dage‘mata sai da, ta tashi, Inna tace. _ "Yaur naga dan baqon yaro, ka zata hura wutar'wasa ne?" ' .. , - ‘ Ya jata waje, ya fito da, ita, ya kaita. rumfa, yace. ' - . zauna ki huta". ' ‘ A ' 'DOlenta ,ta, zauna, "ya dawo yana ta' fama agindin murhu da hayaKi, idanun nan kuwa sukawyi jawur, ga hayaki‘ da ya tuenike kicin- din.a wannan halin= Deeda ta zo ta same. shi, ta zura masa idotana dariya. Tace, "Hura wuta‘ba‘cin tuwo bane malam'Sabeer". , Ta matso kusa da' shi, ta sunkuya tana kokarin hura wutar, 'ya ture‘ ta Me kika maida ni?" 5 ‘- ' Ban mai ,da kai komai-ba, yanayin ka ne ya nuna

Ta kalle‘ shi, "Ka ga idanun ka kuwa
_ Dago idanun nasa yayi ya zuba-'mata
a cikin nata ‘idanun. Gabanta ne ta: ji ya
tsinke, tayi saurin kau da kai, ta fltagaba
daya ‘ta rikiCe. Ta rasa me yasa idanun' Sabeer
ke fadar'mata' da gaba:
_ Murmushi yayi, ya ci gaba da flflta wutar, sai da
ya hura ta kuwa' sannan ya flto yana tari,
~idanun'sun kada suna hawaye. ‘ -.
Inna ta mike? cikin rashin jin dadin halin da yake,
ta ce. ‘
"Kaga yadda ka mai da“ ’kanka k0 Sabeer? Ba ka
bukatar kayi wannan abin". Ya ce, AuMe yasa‘ba
zanyi ba? Akwai’ bukatar, in taimaki Inna ta,
yanzu lokaci» ne da za-ki ‘huta; Fada min‘wanne
aikin ‘kuma zan sake ‘miki?" "
. .Ta yi~ dairya, "Sabeerba ka da dama".
_ Kicin dinya' sake binta; ‘duk, abinda zatayi sai
ya karba ya taya ta, ko suyi tare suna 'hira' suna
dariya tare, Deeda' ta .sa musu .ido‘tanakallon
su tana murmushi, ta, kasa
daga idonta akan su, musamman Sabeer din dake
kokari‘n yin abubuWan da’bai iyaba. Yadda yake
ma Inna; da 'irin_ kulawa" da dariya da yake. sa
‘ta yasa ta tsinci kanta da jin Kaunar. sa a Inna
itace komai nata a ‘rayuwa; don haka duk me_
kaunar Inna. masoyin‘ta ne? ‘
Idonta na kansu harta‘ shiga daki, ta dauki jakar
ta tare; da hijabi, ta cewa Inna‘zani wani wurita
Zan dawo yanxu
Inna ta kalle ta, "Bani za ki tambaya ba, mijin ki
ne zai iya baki izinin fita".
»Hakan yaSa' Sabeer ya fara murmushin tsokana,
'yana‘ 'kallonta' tana' kau‘ da 'kai,‘ amma sai‘ da
yayi .nasarar hada ido da‘ ita’ gami da daga
mata gira,‘ yace
' “(i will do Anything .for“ my Decda) _na baki
damar zuwa duk .inda.-kike so (I .truSt you) na
yarda dake Murya'KaSa-kasa tace
Na'gode":Ta'fita ‘yayin da ya ‘ci gaba da hira da
Inna, tana bashi labarin Kauyen su,~ da
~yanayin rayuwar su. Duk wani aiki kuwa da
'zatayi tare.‘suke yi, k0 ya mata. Hatta aikin

furar ta .tare. Suka. yi,-" yayin .da ya dauko
(camera) dinsa yana ta daukan ta hoto. _tare da
zagaye cikin Kauyen yana daukan duk abinda ya
burgee shi; - . ' ' ' _ Bayan ya dawo ne ya-samu
Inna ta dama kunu tare da masa"yar tsame, nan
ya zauna ya' soma cin nafarantin nata, yana
santi.‘ Ya .sha’ kunun ma yakoshi sosai; Innan'
ta masa- ‘dariya, yayini da-take masa‘ addu'ar
fatan alkhairi, a zuciyar taAshi- da Deedan. Ita ta
San. duk duniya ba za a samu me son Deedanta.
kamar Sabeer ba. Haka nan ta lura Sabeer na ,
da 'wasu Boyayyun halayen kirki wanda sai ka
zaunada shi neza ka fahimta. , ' '~ . -Deeda
kuWa tafiya' tayi sOsai‘ da ~kafa ta' ' jé kaSuwar
dake: gaba' da kauyen 'su .kadan, Wanda a
nan;-"akan',samu-abubuwa' ’ sosai fiye da,
kasuwarkauyen tasa. A nan ta ’. dauko yan:
sau‘ran kudaden‘ta ‘da'take- ‘da su. ‘ «.ta yiwa
saber; siyayyar'irin abinda ta san zai?"
bukata, sannan ta kama hanyar‘dawowa. " _ A
gajiye ta iso da kaya ta same su~ a» filin gidan,’
Sabeer ya sa'Inna tayi'. gaye yana ta daukan ’ta
hoto tare; da yaran anguwan sai .hayani'ya
Sukeyi Innan‘ " ta kalle’ta daga inake na
ganki 'da kaya haka‘?" ; Daki ta ja Innan‘ta‘na
nunamata, inna na yiwa Sabeer cefanene, tunda"
na san' --Wahala cimar, abincin Kauye,‘ zai masa
kafin ya 'tadi, sai a ‘ dinga masa amfani da Su".
Gidan .sauro _. ne tare. da wani madaidaicin
bargo sai -kayan (tea); ruwan, sha na tuba, wato
SWan "da Abincin ,kwali kamar .su (c0rnfleakés)
da makémantan Su” tare da'flask, Hate din‘cin
abinCi'da kula,’ ' tare'da cokula. sabulu Dettol,
sai dankali da ~ - - sauran tarkac'e dai.. - Inna
ta yi murmushi, ".Gaskiya kin kyauta Deeda,-
kiny'i tunani mai kyau". Saber da'ke ,tsaye daga
nesa yana
ya‘ ’kalli Inna, Ya kalli Deedan' yace
"Inna, , bana ’_bukatar _ wannan abubuwan. ba
sai kin min wadannan. abubuwan ba...f'. 1 ' = , ‘
1g"? pe, *"Nasan- dadin maganarka Sabccr,
tunda na saya ba’ za'a ‘yi aSarar‘su Ba,— sai dai
a kori gaba".

' Yace, "haka ne Inna,‘ sai dai tare da ,ku za mu hadu mu cinye _su ‘ba ni daya ba. Sannan da ‘sharadi: ‘zan maidawa ‘Deeda
~ kudinta da ta kashe, saboda hakKin cinta da Shanta da’ nawa duka a kaina yake. Wannan nauyina nane bana Deeda ba,_ tunda ina da halin yi ba sai tayi ba".
. " Inna tayi dariya, "Allah Ya maka, albarka", , ._._ '
‘ Nan ta; tattara' kayan ta fita da su, lokacin Sabeer ya mai' da kallon .sa kan Deeda, ta yi godia ta kau da kai.
. Muemushi yayi, ya matsa dab dai; ita tare da dafa haunta ', ya ce
"Deeda‘,‘na gode‘ da kulawarki 'gare ni, na ji dadi kwarai, saboda 'hakan ya~ tabbatar min da ceWa, kin bani .damar ‘zama. kusa da ke, kin bani damar "zama. kusa da abinda'nake so, zama kusa da abarkaunata, farin ,cikina, nutsuwa' ta‘ da .kwan'ciyar hankalina (Thanks) Deeda, ina So ki 'yarda dani, ~zan iya (managing) zan iya rayuwa a Kauyen nan kamar yadda ku ke- yi. (I swear to Allah) Deeda zan'iya‘cin duk abindaza ki ci, zan iya shanduk abinda za ki sha ~ko‘mai 'dadin sa komai rashin sa.- Haka zan iya ray'uwa a duk indaki ke'rayuwa". " ‘ A hankali‘ ya. jawo ta jikinsa _ya rungume ta'sosai. ' "Indai kina tare. dani, kina "kusa dani, tObani da sauran matsala"
_ _ Lumshe ido taYi tana. Shakar KamShin jikinSa; ta» ‘tsinci 'kanta da kwnaciya akan faffadan Kirjinsa tana sauke ajiyarzuciya, ba ta ankara ba sai bakinsa ta ji'anata.- : .
«Ras Kirjinta ya buga, ta yi saurin bude ido tare da janye ~jikinta daga nasa, ta fita daga dakin dasauri,’ ta bar gidan ta nemi _ wani 'gindin bishiya‘ ta Zauna tana sauke numfashi ‘ ‘
' - ' ' Haka rayuwar Sabeer, ta kasance a . Kauyen su Deeda, har ya saba .da mutanen Kauyen, da‘kuma rayuwar garin;Inna koya. mai da ta koman“ sa, dUkkan hirar’ sa ‘da damuwar sa ita' yake‘ fadaWa. ,Deeda kuwa kwana' take. kula da .. Sabeer, dukkan tsawon dare haka za ta

dinga .kaiwa-da kawowa, wani lokacin ma bacci ke_ sace ta . a dakin, hakan yake 'bashi damar kuladaita._ , ~ ' . _ A duk lokacin'da 'Deeda ta tuna da (body contaCt) dinta da ,Sabeer sai gabanta ' ya fadi, ta ji hankalin ta ya tashi. _ Haka nan duk rintsi ba ta bari 'su hada 'ido saboda' a duk lokacin da'suka hada' ido ,_ irikicewa take',wannan idanun nasa suna bata tsoro - tare da wannan shu'umin mumushin. ' nasa mai; dasa mata' tunani, a cikin zuciyar ta.' Bayan wannan dare abubuwa da dama 'sun canja a rayuwar ta, zuciyar.' ta da kuma' jikinta. ' Abinda' 'ta lura ya kuma daga mata hankali shi ne,~ yadda fatar'jikintaja soma canjawa kamar da abinda ta rabu da_ ' shi 'tun jimawa, ciwon da ta manta ma da shi taga ya far'a daWowa kadan-kadan, sai dai bai yi yawa ba, amma ta ga alamar sa. Wannan ba- karamin daga, Hankalin Deeda ya yi ba, sai, dai ta Boye ba ta fadawa' Inna ba, saboda tana iya matsa mata su koma Kano ' asibiti, Karshen, ta" kuma BIRNIN GAYU za su koma, ' don ita.'bata buqatar hakan ' Sabeer 'yakanyi tafiya mai nisa ' da Kauyen kafin ya-samu (Network)? ya kira mahaifinsa a waya'. A nan ya fada masa cewa suna nan cikin Nigeria, ba su bar qasar ba, suna zagayawa Ya tabbatar, masa-da shi ,da Deeda duk suna lafiya, sannan in lokaci ya
yi za su dawo. Yakan yi dariya ya sa masa albarka. ' .
Haka yana waya da Ibrahim tare da Farida. Ibrahim din ya sha tambayar sa me ake ciki? Yaushe za su dawo? Ya kuma) yake fuskantar rayuwar Rauye?
Amsar dai guda daya ce shi ne ba ya fuskantar .wata' matsala', kuma insha Allah zai dawo tare .da Deeda. Bayan shi ba wani abu da yake fada musu. ' '
Farida ce tasa Ibrahim a gaba cewa dole suzo su duba Sabeer, sai dai ya kan lallashe ta da cewa su kara masa lokaci, ya tabbattar in Sabeer. na bukatar su zai neme su, amma lokaci zai yi Wanda za su je ko bai neme .su ba.'Haka nan

tana bukatar nutsuwa don .ci gaba da'(treatment) dinta. ‘
Haka Ibrahim da Faridan sukai ta. kokarin kula da BIRNIN GAYU, tare da Aslbitii, .da kuma; (Business) na Daddy, yayin da, Sabeer yai bude sabuwar rayuwa a kauyen su Deeda.
Al'amarin’ Deeda kuwa ganin ba ta da wani abuda-take yi sai zama, haka' yasa. ta soma tara 'yan ‘ yaran kauyen‘ a karkashin Wata katuwar bishiya tana ‘ koya musu karatun_boko da safe', .da yamma kuma tana koya musu-na .Islamiyya. da’ dan‘ ilimi' da fasahar da Allah Ya‘hore mata.
' Sabeer kuwa har da shi‘ a zaman ajin,‘ musamman na Arabic da take koya musu addu'o'i, Azkar din nan na‘Safe, da yamma. Don kuwa akwai addu'o'i da .yaWa ‘da- ya karu da‘su, Wanda bai san da su ba. Wanda suna da matukar humimmanci ga. rayuwar dan Adam, ya kamata ce sun ' zama daya daga cikin al'amuran rayuwar na kullum.: Deeda tun tana hana .shi zuwa, ajin har'ta‘gaji ta Kyale shi, don kamar. Kara zugashima take DA yaxo
Wani lokaci- shi yake‘ ‘taimaka mata wurin koya musu rubutu da sauran su. kuma
tana jin dadin hakan. Wani“ lokaci takan zauna ta sa’. masa ido tana kallon sa cikin yaran kauyen ya mai da su tamkar ‘abokan \sa, ya ja ,su a jiki.
Wai' 'Sabeer din da take ganin a da bashi da tarbiyya shine yau yake koyawa yaran nan dabi‘u (manners) yadda» 2a, su’ yi mu'amala‘da mutane cikin "nutsuwa, da *tarbiyya. Wannan, halaye naSa ya‘r-sa ~ta fara girmama shi, tana (respecting) dinsa‘ sosai, har ta. soma jin zuciyarta ta aminta da shi,‘ta yarda da shi.- _ Ya taimakar mata ta Ban'gare da dama, ta hanyar shawarwarin yadda za; ta bunkasa makarantar ‘da ta Kirkira a“ gindin bishiya ya koma aji.’ Shi ya‘ bata‘ shawarar su je su roki dagacin kauyen ya baSu wani guri da ,zasu' mai da shi ‘koda ‘aji dayane Su tara yaran, ciki Su'zauna‘ko da akan tabarma ne, .saboda' lokacin sanyi k0 'damu'na in ruwa ya sauka kar ya katse-musukaratu, ' ‘ '

-' Da farko dagacinya Kiyarda, amma daga baya ya amince da sharadin in ta samu
yara masu yawa iyayensu sun yarda zai basu Wani wuri'wanda dama 'can asalinsa anyi "shi da ’sunan makarantar ne‘, ‘amma yanzu ya *koma'wurin' ajiyar buhunhunan abincin sa in ‘ ya‘_'noma, saboda' makarantar ta jima da mutuwa ba‘ aiki take ba. ..
” A- nan Sabeer. ya .taya ta yakin fahimtar -da “iyayen. 'yaran- muhimmancin karatu; da:ilimi, musamman a Zamanin ‘illar‘ zarria _cikin duhun kai, musamman ilimin Addini da‘ ake ‘yinsa’ ko‘ oh’o. 'Ya tabbatar musu 'da‘ idan har. suka nuna suna son karatu to dole jama'ér da Suka manta, dasu, su waiwa-ye ~su_. In har suka ja hankalin gwamnati da ta manta da su a'gefe, haka in suka nuna» sunason ilimi 'suka ja'hankalin malaman addini, to duk za Suwa wayesu, su’ taimaka‘ musu da samun ingantaccen ilmi don kyautatarayUWar su na duniya da: Iahira." Amma in suka yi ta zama'a haka, to “a' hakan rayuwar .su za'ta kare, :anzo haka za a koma haka. ' ‘ ' ‘
Da wannan shawarwarin suka yi ta bawa iyayen Kwarin gwiwa~ har suka yi nasara, don‘ .haka - dagacin ‘ ya cika alkawarin sa‘ aka ‘gyara wurin suka’ fara karatu; . '
‘Duk da ita da Sabeer din ne kawai, haka koyar da yara ba abu ne mai‘ sauqi ba, musanman yaran kauye. Amma ba. su' gaza ba'saboda abu ne da ‘suke yinsa cikin ’kishi har Zuci da .son' kyautata. rayuwar yaran. . ,
' Nan dagacin Kauyen. ' ya‘ musu alkawarin shiga (Local government); wato 'karamar hukumart'da kauyen. yake, don‘ a‘ ankarar da. su buKatar su wanda sun tabbatar suna a cikin (budget) na gwamnati,‘ sai dai. sun bata ne a rubIbi- da ba su koka ba kuma aka mance da su.
Deeda kam ba‘wanda. ya kaita murna da faruwar - hakan a; kullum tana ‘fatan ci gaban kauyen su,'_ tana kishin ilimin su sosai. Wannan abu 'da Sabee‘r'ya‘ mata ba Karamin
daukaka 'ya samu‘a' wurintaba harta- soma tunanin‘ tafiyar 'da rayuwarta‘ tare da ‘ shi.

Tabbas Sabcer' shi ne .irin abokin rayuwar da ake nema, Wanda zai mata'jagora, ya' taimaka mata a dukkan matsalar rayuwar ta. .Haka a zahiri- Wannan' shine' 'burinta, daukakar' Kauyen su da ci gabanSu, su har' rayuwa cikin duhun kai.~
Yau ma kamar kullum bayan . sun gama hira da Inna tare da duba takardun 'yan' makaranta da torch da fitila, wani' lokaci da' .hasken waya duk da garin ba (service) akwai inda suke zuwa cajin waya na kudi da' 'janareto. Wannan wurin wani lokaci' akan samu (service) na MTN, a nan 'Suke zuwa 'suyi, cajin' waya, Batir, din kamara,laptop 'dinsu da 'makamantan su. Deeda ta 'shiga' ta bar; Sabeer da Inna suna' hira, tana jinsu yana bata labarin yadda Kauyen- nan wataran zai yi suna, yayi fice. , '
_ Innan ta fashe da dariya, ',tace,_"'Allah Ya sa".DA zanfi Kowa murnA
ah shared a profile .
birnin gayu
chapter20
Sabeer yace, "Kwarai Inna; wata ran sai an samu manyan 'yan boko, manyan yan kasuwan da za su kawo cigaba kafinTa-ankara sai gari Kauye ya zama Birni. Kinga wadannan 'yan yar'an, wataran su ne manyan gobe. ' Kinga abinda muke koya musu. suna' fahimta cikin sauri fiye da tunani Wannan ya'nuna alamar yara ~ne masu kWaZo, idan har gWamnati da iyayen 'su suka basu dama da hakkin su, da ~irin su Daddy masu kudi suka taimaka musu, to za.' kiga wataran sune za su taso su rike- mana yaranmu, su kare mana hakkin mu da addinin mu".
' Inna ta ce, "Ga mai- tsawon rai, Allah Ya tabbatar, Allah, Yasa maganar ka' ya zama gaskiya"! ' . '
"Amin Inna". Ya ce
'Wani lokacin mutum yana 'buKatar shiga irin wuraren nan kafin 'ya fahimci haka, ada kafin in 20 nan ban taba tunanin k0 sanin. akwai ,mutane masu rayuwa irin haka ba,_ don haka' ina godiya ga Deda da ta

san1 zuwa har na fahimci haka, 'naga abinda '
ban 'sani ba. Hakika Karin ilimi da haske na
samu a Bangaren da ban ‘sani, ba"Inna ta ce,-
"Haka ne, Allah Yasa mu dace".
. ."Sabeer‘ya amsa'da, "Ameen".
: Da wannan‘ hirar Suka yi sallama, Deeda na
jinsu, tana.jin Inna ta shiga ta kwanta‘ tayi‘
bacci,‘ ta mike-'a hankal'i ‘ta fita hannuntarike
da torch, ta nufi .dakin'Sabecr ‘Ta same ’Shi
kWance yayi ‘dai daya alamar ya gaji, bacci mai
nauyi ya dauke shi. yadda ta ga ya kwanta baki
bude, bacci mai’nauyi ya "dauke shi ya bata
dariya.
Ta Kara ‘haska shi tare dazura‘ masa 'i’do tana
kallon sa, a hankali tana jin Kaunar Sa na
shigarta. . ' Rufe ido 'tayi tana tuno rayuwar su a
BIRNIN GAYU, lokacin da take masa aiki kullUm
suna fada. Ta yi murmushi- tare da gyara ‘masa
kwanciya, ta lulluBe shi,-»tasa' shi gaba tana
kallo, don kuWa da tana ba ta
iya‘kallon sa, ko’ da wasa‘ba ta‘yarda ya dora
idon'sa cikin nata, *yanzu‘Sai-..ta*-?rikice,ta
rude. Sai in ya yi bacCi take ,zama’ta yi ta
kallOnsa kamar talabijim .‘ , ’ " :Wannan__
‘lokacin da ‘yanayin ‘ ya fl.‘ kowane lokaci dadi
da nishadi a tare da kwantair da’hankali gareta
tana kallon sa, tana‘shaffa ‘kanSa,'cikinmurya-
kaSa Kasa ta ce.‘
. "Saboer, ban. San Cewa daya" Bangaren' 'cikin
ka ya f1 Wajen ka kyau ba yadda ‘nake tunaninka
sam ba haka’ kake ba" (you: are such a nice and
good humanbeing) Wannan side dinnaka’: ya.
burge, ni, wannan‘ (personality) din naka
ya;;danawa‘ zuciya ta tarko, ban "San yaushe
(respect) din da nake baka ‘ ya‘ ‘koma so ba ban
San; yaushe burgenin da_lWannan‘halayyar naka‘
ya. bani komai, ka mai‘ da burina naka, ka mai
da 'rayuwa ta rayuwar ka, mutane na, da kauyena
ka mai da su naka, Ka ruyu damu Sabeer; ban
.tabbatar da kana so naba
lallai nima zan tabbatar maka da ina sonka:
Sabeer,‘ zan run-gume ka hanhu bibbiyu,.zan so
ka, Zan ~tsare maka amanar' 'kaina zan zame

maka uwar 'ya'yanka, zan kasace da kai ‘a kowane irin halin Kayi 'hakuri Sabeer da "abinda ‘ nayi ‘ maka a baya, ‘yanzu” ba komai a zuciyar ’Deeda sai tsabar tsantsar sonka Sabeer". ‘ " - A hankali "ta' kwanar da kanta bisa kirjinsa, 'ta rungume'sa tare da shafar kansa,” ta lumshe ido tana. shakar sonsa tare da jin kaunar sa na bin jikinta, yana fatsa ta.

‘ Kamar kullum yauma ta riga shi tashi, sai'dai kusan tare suka shirya. Suna shirin ma zuwa makaranta 'wata makociyar,.su' ta shigo a rude tana KwalaWa Inna, kira; cewa ta zo ta taimaka musu

Inna'ta kalle ta a rude; ta ce.

"Talle, laflya dai k0?

"Ina lafiya' kuwa, Ta sallah ke Ciwon ciki, duk 'wani jiKe—jike mun bata ammah banga‘ alamar sauki ba, kin San. juna biyu gare ta, amma bana' jin ta kai' lokacin haihuwa, mun rasa me ya faru? Shi ne na' ce ki zo 'ki duba ta‘tundakin fimu shekaru k0 za’ki‘gane meye matsalar'

’ Tuni Inna ta zari gyale; 'ta bi tana jimamin al'amarin, yayin da Saber da Deeda suka‘bita; “ Sun samu’ Ta'sallah ' nata juye ‘-juye kamar za ta mutu, Inna ta kama ta tana? ~la‘tsa cikin tare da tambayar ta ina ke mata'ciwo? A mma k0. magana bata iya yi, sai numfashi .take sama-sama.

. “Deeda ce 'ta' tsuguna tana tofa ‘mata addu'a, dukkan su sun rasa abin yi. A nan Sabeer ya kalleta duk ta galabaita, bata da wani Sauran karfi, za a iya: rasa ta da“~ abin cikin nata. Ya lura yarinyacé ma karama.

“Nan. ya shiga ‘dUbata, ya kalle su, ya ce.,

"Haihuwa zata Yi; tana'bukatar asIbiti‘ cikin gaggawa

Talle .tace, "Na yi- zaton'haihuwar da saura‘? To mu‘ .ina‘ muka ga wani a’sIbi’ti? A'i wannan sai Birni,‘ '.Inna ta. .ce,' "Bamu‘ da k0 'unguwarzoma ‘balle likita,haka“ dai 'muke haihuwar ‘ mu a- " KauyE, in abin yayi sanani in da halli: “mu Shiga cikin gari, in babu 'hali kuma sai .yadda Allah Ya.yi.".

' Sabeer ya bude'baki cikin' mamaki, k0 aSIbiti_ babu balle 'ayi‘maganar likita;
-‘ . Ya. » kalli Tasalla da ’kyau,"Tana bukatatae asIbiti" cikin ,gaggaWa,‘ gashi ba~ lokaci; kuma karfinta ya gama Karewa". ., . . -
~A nan ya .mata duk'dabarun da yasan zai mata-‘a matsayin sai na- likita,sannan ba abinda zai iya‘ yi saboda- ‘ba 'kayan aiki b‘a magani; ; ' Ya mike hankalinsa a tashe,yace.
..",Deeda,".ba ta da ‘sauran karfi, tana bukataf (drip) da ruwan naquda' su taimaka mata, in har ba haka ba zata iya‘rasa su duka', ga ta yarinya ce, Karama, ba za ta iya ci gaba‘da’ jurewa ba, Ina zan‘ samu (chemist)?"
,- Deeda hankalinta- a‘ tashe ta ce, ";Sai dai mu - shiga gari, shima ba‘_ kowanne irin magani 2a. mu samu ba";
. Saber' yace, "Bamu da lokaci', zan je in nemo ' magungunan, kafin nan Inna ku kula da ita,in ta bata ruWan zaf1 kafin in dawo, zan yi KoRari in dawo da wuri . Deeda ta ce, "Saber; zan bika, don ba ka San gari‘sosai ba
_ Bai mata musu' ba suka' wuce, Deeda ta lura hankalin sa ya tashi sosai, ta ce
"Sabeer, abin ya yi' tsanani ne
.Sosai ma Deeda, ina tsoron kar wani abu. ya Sameta(She is in 3rd stage of labour) 'Karfinta ya‘ kare duka, ina‘ga‘ mun yi amfani da (forceps) don ya taimaka
mata, amma na san zai yi wuya mu samu".
Deeda ta kalle shi, "Me zai hana in mun samu (Network) ka yiwa Ibrahim waya sai ya aiko mana da kayan aiki kafin mu isa kayan sun iso, sai mu taho da shi". . .
Dariya yayi gami da sauke ajiyar- zuciya, ya ce , "Gaskiya kin kawo shawara mai . kyauu . Yanayinta da kyanta asIbiti ya .kamata' a shiga da ita, amma ba zai yiwu _a daukota . ba, don ta galabaita. Sannan yadda Kauyen yake ba wuta ba wani kayan aiki, ban " ' , tsammanin za mu iya bata taimakon da ya kamata, sai dai kawai muyi iya abinda zamu » iya mu barwa Allah sauran; , Gaskiya “ban ji dadi ba, matar- nan (is in pain

and) ba zan iya mata komai ba. (I can't do anything for her As a Doctor)".
Deeda ta kalle shi,' ta yi 'mUrmushi, ta ce "Sabeer, kayi mata abinda za ka. iya, a haka ma ka mata Kokari' 'sosai ma wanda; ba'ai taBa mana irinsa a qauyen mu ba".
Haka ta'_dinga jinjina Kokarinsa tare da' bashi Karfin gwiWa, tana' tausar' sa - da kalamai' masu dadi; Da hakan 'suka isa" inda Suka' samu (service) 'ya kira Ibrahim ya masa *' 'bayanin ciwon matar, bai Bata lokaci 'ba kuwa ya je (store). din maganin su da ke asibiti ya hada' masa . maganin da yake bukata, harda ma karin;magunguna , kamar maganin zazzabi, malaria, ciwon ciki, *ciwon kai na 'yara da na manya,_ duk magungunan da yasan 'ana yawan bukatar su ya hada su' wuri' guda : cikin 'manyan kwalayem Da kansa yasa a bayan mota ya nufi garin su,. ' ' ' Sun iso cikin garin karamar hukumar .suna jira .'sa,' inda suke" ,yawan waya .yana ' 'fada'musu ga inda, yake,. yayin da ' Saber 'yake" 'kaiwa' da. kawowa. tare da tunanin 'wanne hali matar nan take ci-ki?
Sun yi awa guda . suna jiransa kafin ya iso, tare suka shiga motar don ya' kaisu 'iya inda za- su sauka Su Sami motar da'za'ta' Karasa da su'qauyen. , 'Tunda suka shiga motar Deeda kanta na sunkuye, ' ~ 'Ina kwana?" Shi ne' ka'dai ya hada ta da Ibrahim, ' ta kau dakai gare shi, shima ya yi' karfin'- halin daga kansa daga kallonta,' yayin da , ya mai da kallonsa kan Sabeer. Ya lura'ya dan rame,~ yayi duhu; Sai dai ya ga alamar "nutsuwa da -' girma a. tare da shi, sani wannan yarintar da ke tattare da' shi yanzu. babu. ' . - Ya' lura Sabecr k0 maganar. gida bayamasa; sai labarin' yadda haihuwar matarya zo mata, yake ba shi. Haka sukai , ta tattaunawa yadda haihuwar. za ta 'kasance,' har suka isa, suka nemi' shatar ' Wata mota da-za-ta iya shiga, da 'su' kauyen, sukai ,sallama da Ibrahim. '

Sai lokacin ya samu damar kallon Deeda, suna

tafoya yayin da ta kau da‘kanta gare shi, tautsayi
k0 ya juyo da Sabeer, nan ya ga irin kallon da
yake- yiwa Deeda. Wani irin kishi ya turnike shi,
ya ji tamkar ya juya ya shake shi. Haushin sa ya
kama shi, ransa ya yi mummunan' Baci, zuciyar
na tafasa. Cikin fushi. ya shiga motar ba tare da
ya sake waiwayawa ya kalle shi ba. Haka ya
dinga huci a mota, idanunsa sukai Ja. ~ .
. Deeda ta lura da halin da yake, "Sabeer,laf1ya?"
‘
Kau da kai yayi bai kulata ba, duk da hakan- ba
ta fasa tausar sa ba, a tunaninta ganin Ibrahim
.ya sa shi tunanin gida, taflyar Ibrahim din ne ya
daga masa hankali. '
Ta kallé shi a zuciyarta tace yanzu in za ta ce ya
koma gida sai ya hau fushi da ita, amma har
yaushe Sabeer zai cigaba da
rayuwa da ita a kauye? Da irin wadannan tunane-
tunane suka isa Kauyen, kowa da abinda ke
zuciyar sa.
Sun samu Tasallah ta 'galabaita gaba daya, k0
Kwakkwaran motsi ba ta‘iya yi, ga mijinta da
sauran jama'ar Kauyen ‘a‘ cike
a gidan, daga mai jiqo sai mai rubutu. ,, ~
Haka akai ta dirka mata. _ Inna na ganinsu ta yi
godiya ga , . Allah, ‘ a nan kuma akai ta dirama
da- mijinta, don ya Ki Sabee'r, ya duba ta, duk da
k0 ya nuna masa shairdar sa na likita, amma ya
ce shi ba mai taba masa mata. Da 'Kyarda kyar
aka shawKo kansa .ya yarda. Sabeer ya~ kalle
shi Dattijo da shi, ita kuwa yarinya Karama. - . , '
"Allah Ya kyauta". Ya fada a ransa. A nan ya
shiga yi‘ mata taimakon da ‘ duk ya san zai iya,.
tare da dabarun su ‘na likitoci. Deeda dai ta
zama, (Nurse) din dole, duk da bata san komai a
aikin aslbiti
ba, ita ta dinga ‘kawo miKO, yi kaza, yi kaza,
*har Allah :Ya taimaka Tasalla ta‘
haihu; yaro namiji '-lafiyayye; Sai dai kam'ta
wahala.“
Nan kuwa Talle ta buga guxa, Wuri ya dau sowa,
Inna ta harare ta. ‘ "Ni fa ban 'son jahilci, ki-
gOdewa ’Allah ba guda zaki yi ba in kin gode

maSa kya yi duk abinda zaki yi"..' .Talle ta ce,
"Alada 'ce,' bari inyi . kayana". ' ' ' ' .Inna ta
girgiza kai, ta mike Ita'yiwa Tasallah barka, ta
nufi' gida, bayan Sabeer ya ,tabbatar kOmai
lafiya; suka- tafl 'Tasalla tai' ta masa 'godiya,
Haka 'ya kom'a gida ransa-ba' dadi;~ don har
yanzu yana: tare da .' -fushin Ibrahim, , '- Deeda
ta kalle --shi ta yi murmushi, ta ce. - ' "(W el
done my Hero)". Daga- kai yayi yana wani, sha
mata
Kamshi; _ _ Sallamar'jama'a suka ji,~' hakan
yasa suka fito a tare; "Yan'uwan Tasalla ne: da"
mijinta suka.ta masa, godiya, da .sauran Dattijan
Kauyen.~ ' -- ,Shi dai 'nauyin su ya dinga'ji, 'ya
'nuna ' musu ,shi baison' godiya, aikinsa' ya.yi.
' . _ Haka.mata sukaita shigowa suna yiwa Inna
godiya. A wannan ,rana. da ' wannan 'lokaci
kwatanta farin cikin Inna-da ;- 'Deeda ba'mai
yiwuWa bane. ' ' " . Deeda ganin' sabeer 'na
"wani'" sha' - matar Kamshi yasa 'ta" fita d0n
tafiya makaranta, ta barshi; a zaton ta Zai biyota
ga mamakinta'har'.'suka tashii'bai
zoba- Yanaf gida tare da..-Inna har
yamma_,"sannan: :ya fice' yaje "ya duba', ' " mai
jego da danta, ' ya",fito~_ya 'nemi :wurinda
ba ,kowai ya Zauna, zuciyarsa . na cikin ' Kunci
da BaCin-rai;
'

bayan deeda ta dawo ta fito yawon neman sa,
har tayi sa'ar samun shi. Nan ta nufi gurinsa ta
zauna a gabansa suna kallon juna, ta lura ya
daure fuskarsa
"Sabeer, mene ne?"
Ta fada murya Kasa-Kasa.
"(Please)- ka fada min, ba ka san yadda
hankalina ya tashi ba ganinka cikin wannan hali.
Na san dai ka tuna gida ne halan, Sabeer me zai
'hana ka koma...". '
"Ya ishe ki".
Ya fada cikin fada. '
"Na fada miki cewa karki sake min wannan
maganar, kin manta? Ba zan koma ba sai lokacin
da na so kuma na ga dama, kuma na fada miki

a cikin kwanakin nan saboda juya masa baya da kika yi
., Hawaye ya zubo mata; murya na rawa ta ce.. '
-"Deeda ba don halina ba, na roKi Alfarma ki zauna da Kanina
Deeda hankalin ta ya kai 'qololuwar tashi, tSananin tausayin Farida ya kama ga, Kaunar Sabeer ya yi mata yawa a .zuciya. Ta fashe kuka cikin tashin hankali, ta rasa wanna irin amsa za ta bawa farida, tausayin .kanta; ya kama. ta, Wani 'yanayi .ta" tsinci kanta a ciki na halin Kakani. kayi. Itama
gani take 'mutuwar zata yi, ga ciwo a jikinta, ga ciwon son Sabeer data "Boye 'a Zuciyarta
Nan ta‘ juya. tana tsahanin‘ kuka, 'ta wuce ba tare da ta ce komai ba, saboda ba ta da abin fadi, » yayin da Farida ta fashe ‘da' kuka; Ibrahim dake tsaye‘nesa da su kadan‘ ya taho ya rungumeta da’bata baki. ' 'Ya isa haka Farida, kin yi iya kokarin ki; Sabeer ma ya yi, saura sai mu barwa Allah". '
kasssss akace laifin dadi qarewa mu
hadu a book4 donjin cigaban wannan qayataccen Ibrn naso mu Fara book4 din yau but I can't make it SBD an Ari book dinne amman idan an dawo dashi koda zuwa gobene sai muci gaba
naku har kullum
a zallah shared a profile .
birnin. gayu(★^4^★)
chapter23⇩
BIRNIN GAYU-4
deeda ta wuce Sabeer a kofar ’ gida',' ‘ta lura"”yana cikin, ' - tsananin damuwa .da- tunani.
' Shi ma ya lura da irin kukan da take yi, hakan ba karan ba karamin daga hankalin .sa yayi ba,_ya bitayana kira. ‘ Deeda‘, Deeda". .
. Amma bata tsaya‘ ta saurareshiba daki ta nufa ta rufe, kofa, ta 'wuce Inna a "tsakar gida,’ ta mike tana' kallonsu.
,"Lafiya kuwa'Sabbér
A , rude "yace "Inna‘ lafiyé“Ba lauba
.‘.Deeda na gani ta- shigo tana’ kuka, ban San

,meyasame'taba". '
Bai rufe baki ba kuwa suka jiyo muryarta ta sake; fashewa da *kuka da Karfinta. Tuni
Sabeer'yasake hawa
"Inna; kice mata" tayi'_ Shiru, 'ki tambaye ta me ya same Waya taba ta? Inna kukan Deeda yana daga min hankali
fiye da komai a rayuwata ina son gani'nta cikin farinciki da kWanciyar hankali
Jin_ kalaman sa ya sake: sata wani
sabon kukan ta yi saurin'toshe -' bakinta'tana don kar Inna? abin' .ya dame"ta, " Deeda 'ya Wuce Iya saninta ta ga alamun son -Sabeer 'a tare da. ' ita' kwanaki, to; me ya faru kwanan nan ta kasa gane: kanta? K0 Ibrahim din ne? .ta shiga rudani ' da al'amarin ,Deeda,' _, haka ta ~yanke hukuncin tambayarta kuma dole: ta bata 'amsa don abinda
takewa sabeer'Ya soma isar ta
,. Decda ba; ta fito ba sai magarib' nan ma .sai da' tabbatar Sabeer ya tafi ' masallaci, ta fito tayi Alwala, kafin Inna ta mata wani tambaya tayi sauri ta koma daki -; ta rufe, don ita a har yanxu bata DA amsar tambayoyin dasuke mata
Tana idar- da sallar isha'i ta bude kofar ta yi .saurin saka mayafi ta kulluBa har kanta tamkar mai ,bacci ta San sabeer zai shigo kwanciya, kuma ba ta so ya same . 1 ' Ba ta jima da; kWanciyaba ta ji motsin shigowar Sabeer tare da Ibrahim da kuma Farida,>tana' jin duk hirar da suke yi da Inna a tsakar' gida wanda duk kan shirye shiryen bude makaranta da asibiti ,ne, yayin da Sabeér 'kowanne bayan minti daya: sai ya. leKo ya ga tana. bacci. "dukkan su sun lura da hakan.
Inna ta'soma musu', sai- da safe, ta wuce Farida sai -ta_ :shigo, Ibrahim kuma dama a rumfa' akai' masa wUrin kwanciya da aka zagaye DA gidan sauro
Kauyen nan har da kai?"
Gaban Sa ya ji ya fadi, ya- kalleta.
"Ai dama ba tare muka'zo ba"; "
"Na sani, ba fadi na'bane, Daddy ne ya fadi in an

gama bikin nan zamu" bar qauyen nan, kamfani na 'can'yana jiran mu. Aiki‘muka bari muka"‘taho nan; tunda'an dauki Kwararrun likitoci ma'aikata banga me zaka *Zauna'kayi ba Ai mun jima "a kauyen,’lokaci ya yi da’zamu tafi. .Ka tuna alkawarin daka ‘yi'wa Daddy, ’ba Sauran fitina' ko dOle. ka bimu mu 'koma
ya kalleta; "Na‘jij‘Allah ‘Ya kaimu".
Ya‘mike ya shi‘ge ‘ciki, ya tura kofar
"' Ta bishi “da kallo cikin tausayawa halin da ya shiga. ‘Tashi tayi itama ta shiga‘ ‘daki cikin damuwa, yayin "daya kwanta, tunani kala-kala a ransa
A daki" Sabeer Ya nufi" gun Deeda wanda a tunanin 'sa bacci take, a hankali ya janye mayafin tana dukunkune cikin (body
suit) idonta A rufe, korjinta 'sai bugawa :yake,‘ tana Addu'ar Allah Sa sabeer kar ya wuce- iyakar sa ya gajikinta, ‘ ‘
. . Zura mata ido 'yayi yana kallon ta,- yana jin wani sabon sonta. hawaye ya ji ya. fara zubo masa. yace Deeda bakisan yadda 1...;nake tsananin fargabar rabuwa da keba (why) Deeda, ta yaya Zan iya tafiya in barki? Na zo» garin. nan ne don in tabbatar; miki da soyayya ta, in; tafi dake. Amma ga. dukkan alamu .hakan‘ mafarki nake, burina; ne wanda‘zai tsaya a buri kawai. Na kasa,_ na gaza, ,ba 'zan iya yin komai ba. Sai son ki, ba zan iya sawa ki soni dole ba, ba zan iya sawa ki zauna dani dole ba". ' _ . .‘Dago ta yayi ya rungumeta a jikinsa sosai tare da kwantar da kansa‘ a jikinta yana Shakar sonta yana sauke numfashi‘ a- hankali.;.'~. , ‘ , ; Wani kuka mai Karfi ta ji ya 20; mata tare da sonsa mai radadin gaskeé
‘ wanda da kyar ta samu ta tare hawayen. Da haka bacci ma‘i Karfi ya" dauke shi, wanda hakan ya ba‘ ta damar kwantar' da' shi tayi'kuka sosai kuka mai isar ta,_'tana' rungumedashi. "
‘ ' "Ina sonka sabeer so 'mai tsanani, son da ban taBa yiwa wani ' mahaluki ba, son da ban taBa jin irin sa akan kowa ba sai- . kai. Sabeer, naf1 ka tsoron‘ rayuwa da kai, ‘rayuwa ta za ta

quntata inbaka. Sai dai ba yadda Zamuyi, ciwo na ya shiga- tsakanin mu In har’za ka ganI ' tsana ta zaka‘yi. Sabeer, sannan ba zan jure tsana a idon ka ba, ba zan jure inga ka kyamace niba"; Da hakan itama bacci ya ‘ dauke ta suna manne da jUna. ; ’ _

’kullum yau' ma ta riga kowa
tashi a. gidan ’tana yin" sallah.'ta.tashi ta fice daga gidan, k0 Wanka bata yi a gidan ba tsabar gudun kar ta ci karo da k0 'mutum daya a cikin su. Ita'a nata tunanin ma ba zata sake s haduwa dasu ba har su tashi
su bar kauyen
_ Sabeer tunda ya tashi 'yake neman ta amma ba ita ba labarin ta,‘ duk inda yake zaton zai, same ta bai ganta ‘ba, nan ya fahimta kansa salon gudun , sa" take. Haka ya haqura‘ ya'zo ya‘ shirya ya wuce asibitin tareda‘su Farida. Tunda gari ya. waye ake‘ ta‘ gyare kauYen, ko ina fes, haka garin ya cikada (security) jami'an tsaro saboda an gayyaci manyan mutané; tun ,daga kan Minsitan lafiya da na ilmi,‘ har kan kwamishinoni, har da gwamna. maiCi na .wannanlokaci
, : Karfe sha daya baki suka fara zuwa,‘ kafin 'aCe kobo » Kauyen ya Cika da baqi na. Musamman aka' shimfida titi. don baqii "‘da za su bi hanyar'
Ranar mutanen"Kauyen 'aun sha
kallo; sun ga jama'ar da ‘tunda ‘suke ba Su itaba. gani Ganiba'yan masu . ’ dauka .na talabijin' da radio, sai aiki suke
kala-kala. ,Lokacin da "baKi' 'Suka gama isowa tare da Dr. Sulaiman aka 'soma' taro, bayan fara bude shi da addu'a tare ’da gabatar da manyan baKi, da 'shugabannin makaranta da asibitin,‘ Wanda akabudesa sunan Sabeer. Nan dai_: kowa " ‘ya tashi "yayi jawabin 'sa da godiya ga Dr. sulaiman da kyaikkyawan‘~ "qarshe‘ ‘da misali. _‘kauyen sukai kWamba guda suka je don nuna godiyar su ga‘zuriyar-su Sabeer gaba daya.‘ _ ~ Deeda tana ‘tsaye daga baya-ba'ya, ta yi kuka, ta yi' dariya, ta yi godiya ga Allah, ta kuma

godewa Sabeer. Haka ta dinga ganin abin kamar a mafarki; Zuwa” azahar taro ya Watse, anci"an sha, kuma daga‘ makarantar 'har ‘asibitin za su fara aiki washegari; ‘ Dr. Sulaiman” yakira Sabeer Bayan taro ya watse,’ "ya kalle shi da kyau; ya lura ba ya farin ciki k0 kadan “Tsaye yake a. gabansa, kansa sunkuye . yayin da" shi kuma ke bayan motar sa, ya ce Sabeer, dago kaika kalle ni". Nan ya dago kai ya kalle shi, ya yi saurin kau da kai saboda dab yake da ya fashe da kuka; don ya San me Daddyn keson fada masa, su koma, kuma ba shi da‘ sauran wani (excuse) da: zai hana shi komawa Daddyn ya kalle shi .da‘kyau, ya ce, 'Sabeer (you re not happy) me yasa? Na zata yau za kafi kowa murnA ' _Nan ya Kakalo dariyar. dole, ya ce.Daddy,' ina murna Sosai‘,'Allah Ya Kara kirma da arziki, Allah Ya saka": ' ~ Daddy yace "Meye matsalar ka
"Ba komai Daddy". "'
"Tun da ka ce ba komai shi kenan, ga mota nabar maka‘ da direba, taho dakai da Deeda, aiki yana can yana jiran ku,‘ Ibrahim zai taho da Farida. (Enough
of) ‘zaman Kauye, lokaci ya yi da za ku koma ku fara rayuwarku. Sunkuyar ‘kai yayi,‘ ya ce "To‘ Daddy". . Kar 'ka manta Sabeera zan jira bana son jin wani labari daban, ka tabbatar kun 'taho". Daddyn ya fada yana Kokarin rufe. motar. _ Sabeer din ya amsa da"To Daddy, insha Allah za mu taho". Da wannan su kai.sallama, Daddyn ya taf1.Yabi= motar da kallo yana tunanin ta ya‘ zai soma tankwara Deeda su koma' BIRNIN GAYU da wannan sabon Kiyayya da take masa masa? , v .:
. _ Yana cikin wannan halin ya 'ji an dafa shi, ya juya da sauri. Ibrahim ne ya gani' a tsaye tare da Farida, nan ya Bata rai ya kau da kai. Ibrahim din ya yi murmushi, Sabeer kenan, tsayuwar me kake yi?
Lokaci yayi da zamu wuce, kar ka manta Deeda matar kace, kar' ka» tsaya wani tunani. .Tunanin me zaka yi? Umarni kawai ; za ka bata, kuma Ya zama dole ta bi Lokaci yayi da za; ka dau' matarka matsayin ka na mijin ta, lokacin

lallashi ya wuce; (You most take a step)". . i "
Farida ta‘ ce, ."Kwarai ’ Sabcer,“ Ibrahim gaskiya
ya‘ fadi, muje". ‘ ‘ Wani‘mugun kallo ya ‘yiwa
Ibrahim, ’ yace.Ba kai za ka fada min yadda‘zan
tafiyar da mata ta ba, ba ruwanka. Na san ‘ dai
dadi kake ji saboda Deeda ta canja
‘ mani, to bari, in fada maka, duk tsiyar ka, , duk
abinda za kayi ba zan bar maka Deeda ‘
ba Nan ya wuce cikin fushi, Ibrahim yace
sabeer, kai “min rashin fahimta"Ka yi hakuri akan
Wanda kake.yi". __ Farida ta fada tana kallon sa
Yana zafi ne yanzu, da kuma
cikin hali na rashin sanin ya'zai yi". "Na fahimta
Yaya ta, muje: mu’yiwa Inna sallama; Nan
suka=wuce. A cikin gidan su Deeda""Sabéer ya
wuce dakin su 'kai -tsaye ’ya ‘ soma‘ tattara
musu kaya. Wannan lokacin ‘Deeda na
dakin Inna tana mata fada, ta' inda take.
shiga ba ta nan ta‘ke'fita ba; don ranta'. ya
mugun Baci ganin yadda ta kafe ita sam ba ‘ za
ta koma da 'Sabeer ba. -
‘ Lokacin :- Sabeer,‘ ya ' yi ‘ sallama hannunsa-
rikeda’ jakunkunan su duka biyu, .ya yi' sallama a
dakin Inna‘tare da daga
labule, yace Inna
"Za‘ mu Wuce Kano, lokaci ‘yayi' da za mu
koma".
. Dam! Damn Deeda‘taji"Kirjinta ya buga, wani
gumi ya soma zubo‘ mata, tsoron rashin Sabeer,
ya shige- ta, hankalin taya tashi. Inna ta mike
tana
gOdiya-
"Sabeer, Allah ' ‘Yai maka Albarka, ' Allah Ya
saka maka, «Ya sakawa iyayen ka da Alkhairi,
‘Allah Ya baka; Yara masu yi maka biyayya. Allah
Ya *sanya Albark Ya baka zuri’a ta gari, masu
jin~tausayin ka da jin qanka. "Yaro dan ‘Albarka";
* ._ Sai kuwa ta fashe da “ ' kuka"Yau zan yi
kewar ka
Tuni Sabeer ya ji hawaye sun. ciko masa, don
kuwa ba qaramini sabo sukai da Inna’ba. Hirar da
yake da Inna koda Deeda bai taBa ba, ya saba da
ita, ya shaqu da ita tamkar mahaifiyar sa.

Yace "Inna, kinga kin sani kuka k0? So-kike ace mata ta sa mijinta kuka? Ni da na' saba kullum Inna mai fura tana, sani dariya har in manta; Sacin rai na, a yau Inna ta sani kuka, hawaye na zuba". '
Ta yi dariya,‘ ta ce, "Ka San ba kullum ake kwana a gado ba".‘ ‘
, Nan suka sa dariya duka, yayin da ya koma kuka,tana.
'Kayi‘ haquri da halin Deeda, ka. yafe mata. Na yi iya Kokarina ta Ki jin' ba yadda na iya da ita"; . . _ . .. Nan Deeda ta' fashe da kuka tana.
"Inna ki Yafe min, ba bana jin maganar ki bane“. ;
, '~Inna ba ta kula ta ba saboda haushin abinda tayi take ji. ~ . “Sabeer ya kalle ta fuskar nan ta rine tayi ja,‘abinka ~da farin mutum, ya ce., 'Ba komai Inna, na yi iya Kokarina, ;na yi kuma‘ iya abinda na ga zan iya, bana‘ . jin-zan kuma iya daukar abinda zuciyata ba zata iya'daukaba a matsayina na dan Adam, ba abinda kuma zan iya yi gaba.Wanda yanzu zan iya:
na tabbatar wa'da Deeda son da nake ma
‘ ta dan haka yanzu yadda take so haka zata Lokaci-yayi da zan koma in taimaki Daddy, mahaifina na bukata ta, ba. na 'son bashi wani matsala". '
ya mai da kallon sa kan Deeda suka hada ido,- wani sabon sonta ya ji ' yana tsuma shi, wani shauKi ya dinga ‘ ji game Kallon ta yama manta abinda ya ,yi niyyar'fada mata; Tuni itama ta :rikice; saboda. ganin‘ wannan mayataccen son nata a idon sa,“ haka son shi ta ji yana shirin fasa mata zuciya. Ya 'birkita- ta, ’ya rikita mata‘ Kwakwalwa, dakyar ta iya kau da kanta, ta sunkuyar da kai. '
jikinta na rawa, yaCe;
.Deeda, ga kayan ki na hada zakizo mu koma k0 kumabazaki tafi ba?
; ,Har yanzu idanunsa a kanta suke, ‘tambayar ta yi. mata qunci. "Wayyo ni Deeda" - , '
- "Karki yaudari kanki; Sabeer bazai iya rayuwa da ke da wannan _jikin naki ba, duk ran da ya ga jikin ki son da yake miki zai koma KiYayya, za ki

jawo masa
CiWOn rashin kWanciyar hankali, wanda daya yake da hauka";
Nan .ta daure ta ce, "Ba zan bika'ba, ka koma kai; kadai, Allah Ya kiyaye". =
' Kanta Sunkuye _ take . maganar, " saboda ya kafa mata 'idanu.. '
Haka yaji maganar kamar ta cake shi da kibiya', cikin zafin zuciya da Kunar rai ya juya, ya dauki jakar 'sa ya bar nata, k0 Inna bai iya sake ce mata wani abu ba, ya tafi. . ~
Deeda, ta fashe-'da wani irin kuka da karfinta kuwa, Inna ba ta 'kula ta ba, ta ji kamarta rufetada duka- '
Tuni deeda taji zuciyarta ta gaza, tabbas yau in Sabeer ya bar Kauyen nan za~ ta mutu' ' rashin sa, da 'kewar sa, da sonsa Sunyi irinsabo da shaquwarda k0 da fada! suke _ yi tana son kasancewa tare da shi.
. ~ ;Ta fada jikin Inna tana kuka sosai da karinta, tana. ' ' "Inna Sabeer, Inna Sabeer... Inna ba zan iya rayuwa ba Sabeer ba, Inna Sabeer ya zama rayuwa ta, kowanne iska nake Shaka da 'tsananin son shi a tattare da ni, kaunar sa ya gama huda dukkan jikina" kukan da take har yasa jikinta ya yi sanyi ta 'fara tausaya mata; " ~
"Shin Deeda na 'yiwa . Sabeer ' wannan Son, to me 'ya hana ta binsa?" '
' Ta tambayi kanta, 'ba ta ankara ba 'sai gani tayi Deeda,' .ta' bishi tana kwala masa kira*Farida da Ibrahim da ke tsaye '_tsakar gidan suka bi su, Inna ma binsu .tayi, jama'ar Kauye suka tsaya suna kallon su, . ' ' -. 'Jin yadda Deeda "ke kwala. masa kira ya sa ya tsaya cak ya juyo Hango ta da' yayi yasa zuCiyar sa' tai maSa 'fari, dadi- ya lulluBe 'shi, ya sa dariya. '-
'"Deeda... Deeda na tana Sona dama zuciya ta ya bani Deeda na tana sona
» Dariya ya tsaya'yana yi yana kallon ta harta iso, ta tsaya-a gabansa tana haki, yayin da yake' kallon ta .yana, dariya. Farida da Ibrahim suka tsaya suna kallon . su.
'Deeda, zaki bini mu tafi? Deeda, kina sona? Kin

amince ’dani ' a: matsayin mijin, ki, - abokin rayuwa 'na har abada?" ; Hawaye ya gangaro mata, idanun ta sukai jawur, ta sunkuyar da kai, ta ce "Bawannan ne ya kawoni ba, so nake ka'sauwaka min‘kafin ka tafi, kar ka barni da igiyar aurenka. (Free-me from this marriage)".zaro- i‘do yayi yana kallonta cike .da Kunari ' zuci‘ya, yaji zuciyar kamar‘ WutaWani irin bakin‘ ciki‘ yaji yana Shigarsa marar misaltuwa. Farida ce ta matso dab da ita. ta ta wanke ta da mari, sai da ta rike kunci.) "Ashe ke dama ba ki. da mutunci, ba ki da tauSayi?"."Sister, (please) ya isa, ki Kyale" ta,‘ zo mu tafi Sister. Ba saki‘ take soba? Zan ba ta, ama a rubuce, don bakina ba zai- iya fadi ba. Ki min addu'a Allah Yasa‘ hannuna ya iya: rubutawa", Sabeer- ya fada yana hawayen takaici , ‘ , Nan Farida ta 'nufi inda yake ta rike. hannunsa Suka nufi mota, ‘ “ ; . "Kayi hakuri qanina, Sister tana ' ganin ka :cikin bakin ciki‘ kuma ba zan iya komai ba dan rage maka zafi da qunci' da kake jibi}. sabeer, kai ta addu'a Allah Ya kawo maka sauki". . ‘

‘ Deeeda na tsaye 'a wurin ta kasa motsi, Ibrahim ya nufo ta da masifa da, fada_, cikin bacin rai ya ce, ,

'Burin ki ya' Cika, kin hana Sabeer‘. . abinda yéke So, k0 Zaki iya fada

meke faruwa? Wane irin kiyayya ki ke 'yiwa Sabeer? ba ki da 'tausayi'ne?‘ Baki ganin yanda Sabeer ke wahala saboda ke? ' Kar ki manta, duk abinda; kai ma wani sai an maka, ' guji ran da- Allah zai kamaki ~' da hakkin sabeer; ,, Deeda, "(for God sake), kalle’ shi ’ ki ganshi (luck at him)wacce irin, zuciya garéki K0 zuciyar ce‘gaba daya babu‘a kirjin ki?" yana fada da daga murya" yake maganar.

. Deedan ta fashe da kuka, tace ."Ya kakeso inyi' ne Ibrahim? Inma

inason Sa bani da ikon zama da shi: ' ’ Ina son Sabeer sonda ban taba yiwa wani' mahaluki ba, na san akan ka na soma sanin so,’ na .San dadin'so. Amma akan Sabeer na soma dandanar

zafin so, dacin so da kunar so', Wanda inka‘
dandana zafin so da ciwon .so,“to ananne Zaka
san meye asalin so, .anan ne ‘za‘ ka "fahimci
kaunar asali mara gushewa‘ na har abada. A
lokacin zakaji ba'zaka iya rayuwa ba wanda‘ kake
soba' lokacinda " zaka gwamma'ci gara mutuwa
da‘ rayuwa 'ba ' tare da~wanda kake ' so ba-
Wannan lokacin zakaSan meye so; ’ 'a halin’
““yanzu‘~ kwakwalwata°a bargitse “take, zuciya -
ta na" cikin“ qunci da tashin hankali. Ina jin
kamar- Zan haukace, saboda tsananin “Son
Sabeer. Amma duk da haka na nemi Sabeer ya~ '
sauwake min, saboda‘ ni da Sabeer ba_
Kaddararjuna bane". ' ‘ "Me yasa? . Ibrahim ' "ya‘
"tambayeta ' "cike da mamaki’ nan 'taja rigarta‘;
ta'cire saafar da ke' "hannunta, ta nuna masa"
tare da fadin "Saboda wannan".
.; ciwon idon Ibrahim ya'yo waje
ganin hannunta a tsorace, mamaki da fargaba
suka bayyana a fuskar sa, lokaci guda kuma'
tausayin ta ya kama shi Abinka dama da wanda
ya binne: qaunar ta a 'ransa, hankalin sa
yai'mummunan: tace Ta ce, "Ibrahim, inhar
Sabeer zai . ga hannun 'nan dan kadan ya
'firgita, ya kusa haukacewa, inaga yaga dukkan
jikina’Deeda! " ' Yakira sunanta arude;‘ 'Kina
nufin duk jikinki haka yake? ' K0 wancan karon da
ki ka zo asibiti baikai .haka ba na zata ciwon ya
Tafi ta fashe ,da kuka, ta ce Ibrahim, ban san me
ya faru ba, ..,ban san me yasa ya daWo har yaf1
na da ,ba. Shin Ibrahim me kake ganin, zai faru in
Sabeer'ya ga jikina? K0 ya tsaneni k0 ya yi
“Karamin hauka‘ ban “san a wanne hali‘
kwakwalwar, sa za ta kasan ce ba.
Wannan tsoro“ da fargaba-dashi nake kwana
nake tashi". ~
Ibrahim ya' kalle ta', “"Kiyi ‘hakuri, komai yayi
.tsanani maganin sa Allah; ' kuma Allah Bai
saukar da cuta ba sai da' ya saukar da
maganinta Sannan Deeda, Sabeer ya kira kan‘sa
ME SONKI; lokaCi" yayi da zai tabbatar da hakan,
.lokaci ne na gWajin‘soyayyar Sa a- gare ji". ~
~» , A'a Ibrahim, ‘zuwan .Sabeer‘garin nan kadai

k0 da bai kwana ba ya Shaida son da yake min, balle ya dawo kauyen da zama gaba 'daya, :cin Eauye, shan kauye, wahala: qauye, taimakon mutanen kauyen
Ibrahim“ Sabeer ya fiye da ‘abinda ya kamata, k0 ka manta Sabeer da yadda .yake rayuwar sa? Mutum ne da ba- ya jure wahala ka. wani talauci k0 kunci, mutum ne da bai damu da rayuwar wani ba kO ya mutu k0 ya rayu, bai. san; ‘ciwon mutaneba
da kima da darajar su ba. Sabeer- mutum neda ko a' office mai A-.C da .
kayan, alatu ,yaqi zama yayi aiki Sabeer mutum da ne bai san meyake‘soba,.bai; san mezayi'arayuwaba. “ amman
_ , Akan Deeda daKauyen mu ya ‘soma sanin me‘yake so? Me yake so yayi? Ya san' .ciwon _wasu, ya damu da~damuwar wasu, ya gane gata, da ni'ima‘da Allah Ya,yi masa, ya zama mutun ta da daraja ni'ima da baiwarda Allah Yayi masa.
; , Sabeer ba ya buKatar sake tabbatar. ' da- soyayyarsa ko yanzu Sabeer ya guje ni ba zan taBa ganin laifin sa ba, kuma ba'_ zan‘daina gode masa da yi masa addu'a ba, ba zan taBa manta Alkhairin gareniba Ibrahitn, inasOn Sabcer, »ina son rayuwa da, shi, ina son. ' kyautata ‘masa, - ina son- nuna masa. soyayyar da wata mace ba ta taBa nuna-
‘ mijinta ba. Ina son :zama da Sabeer dina, ina shagwaBa shi, in yi wasa dashi; in yi dariya da shi, in fada masadamuwa 'ta, ya fada nasa; «mu zama juna in kwanta in nuna masa
‘ tsananin‘ison da nake masa
Ta fashe da kuka. _ "(PleaSe) Ibrahim; ka taimaka min,
ina so in warke, ina so. in rayu, ya zanyi
. Na kasa"fadaWa Inna don kar hankalin ta ya tashi, yau na fada maka ka taimake .ni Zan taimaké ki""Deeda’. Jikin ki ne ba‘ yason‘ qauyen'nan; 'na taba fad‘a miki’ .. kina -da (allergy)- da «wasu '-abubuwa- kamar iskar da kike shaka' na

yankin nan, ruwan'da kike sha, abincin da kike ci?
Ya zama~dole kiyi sallama da
qauyen nan, dama 'na *fada kO da ‘
’ kaya ki ke sawa daga; kinga' canji ki guji
kayan, ko abinci’ ne" daga ci kinga
canji kadan ki guje shi. Ya akayi ba ki Iura ba?
Deeda, kinyi sake; kinyi wasa har ya riké ajikin
ki"; a, . Tana ‘kuka ta ce, "Lokaci daya, rana daya
na ga sun feso, ranar da Sabeer- ya soma ganin
hannu na, daga; nan Yake ’ karuwa".Tashi muje,
dole mu bar kauyennan ; Ta, kalle shi, "Ibrahim!
Inna
e "Za muyi mata bayani, in ta kama mu tafida ita,
amma ya; zama miki dole .har in kina son
rabuwa ‘da .ciwomnan kiyi
sallama da Kauyen nan gaba daya,
_;mu je a soma magani. Muje,ni zan yiwa ' Inna
“bayani yadda hankalin ta ba zaitashi Girgi‘za
masa...kai ; tayi alamar to, suka juya
. ‘Ihu ta sa, gabantaya fadi, da ta ga Inna kwance
a Wurin, bakinta .karkace, tana mimmiqewa in
banda innalillahi wainna ilaihirrajiun babu abimda
Ibrahim ke fadin cikin tashin hankali
allah shared a profile .
birnin gayu
chapter☜(⌒24⌒)☞
Shi ne abinda ibrahim ke fadi, ‘yayin da Deeda ta
rasa wane irin addu'a zata yi? Saboda tashin
hankali da fargaba, tayi wannan ta saki tayi
wannan, tana
kuka tana kiran
‚Inna me ya same ki?"
Ibrahim ne ya daga ta Suka nufi asibiti da ita,
asibitin da: washegari ya kamata ya fara aiki, a
ranar ya soma aiki 'akan Inna Ibrahim tare da
sauran likitocin suka hau duba lalunar wadda
hawan jini ne ya ka da ita lOkaci guda.. maganar,
da. Deeda taima Ibrahim duk tajisu ganin ciwon
Deeda yai mummunan daga mata hankali, wanda
lokaci guda ya‘ ta da mata hawan jini ya ka da
ita. Deeda , na tsaye a Rofar (Emergenéy) tana ta
zabga kuka,
hankalin ta tashe Farida 'da Sabeef suna .mota

tana
qokarin kwantar Wa da Sabeer hankali ta
hango Ibrahim dauke da‘ Inna‘ ya koma cikin
kauye'Deeda na biye'da shi. _
, Hankalinta taji ya tashi, ta soma , tunanin meke
faruwa? Ta fadawa Sabéer k0 sai ta je ta ‘
tabbatar .da mene ne? Nan ta kalle shi ta ce.
muje muga meke faruwa
" . Tare suka taho, suna shiga kwanar da zai
kaisu ‘ "cikin Kauyen suka hango taron jama' ar
Kauyen, na'basu labarin ciwon Inna. Da‘sauri
suka kamsa asibitin.
Inna kam. tana da- jama'a, kuma abinka da_
Karamin. kauye,' nan da nan . asibitin ya ya‘cika
da , mutanen ‘kauyen, babba da yaro, suna mata
fatan- samun lafiya tare da addu'a.» ‘ ' ’
Sabeer ; ~tuni hankalin'sa yai mummunan tashi,
yana fadin Me ya samu Innan?deeda ta fadA
jikinta tana kuka Farida ke lalla‘shinta, :tana
fadin. ' "'Kiyi hakuri, ki mata addu'a, insha Allah
za ta samu lafiya. ‘ Sabeer ya kalle ta yana
’shafa kanta. "Kar kiyi kuka Deeda,~ ba abinda
zai .samu .Innar mu, za ta. samu; sauqi‘,‘ zata-
samu lafiya. muyi‘ . .. ,Wasa, muyi dariya . kamal'
Nan ta rungume shi =tana kuka taCe“ ’
' "Sabeer, Inna za ta tashi ko?" ‘_ "Insha Allah
zata tashi Farida ce'ta ce bari ta' shiga ta ga' '
meké ’faruwa? Sabeer ya‘zauna " Farida ta-samu
an kai'ta» (Intensive. care ’unit) tana tare da
Ibrahim; yayin da take '“munfashi‘ sama-Sama,
ansa ."mata‘ '(oxyge'n); Dole- ta sa Ibrahim ya
cire don‘ tana son magana da ‘shi'Faridan
tsayawa tayi tana kallon su, tabbas Inna.‘Sai
wani‘ ikon' Allah zai sa ta ‘tashi "Deeda".-Shiné
abinda take ’fadi.ibrahim, amanar_ Deeda;Zan
baka bata da koWa mahaifinta bai ‘damu da “ita
ba k0 Wane hali take ba-‘Wannan hali da Deeda-
take ciki tana bukata ta, sai dai bani da ikOn iya :
mata komai Ibrahim; ka“? taimaka mata ta samu‘
laflya, ta rabu da wannan-
mummunan: ciwo. Ibrahim, ka zama mata. dan
uwa,» danginta, mai” share mata' hawaye. " . .
Ibrahim, ka zame mata Inna yadda . nake gatan

ta,- koman ta, ka zame mata gatan ta. Deeda ba ta da kowa". ‘ .
: "Nayi alkawari Inna zan, rike amana, karki damu. Kina bukatar hutu". Idon sa ya Kada ya yi ja.
: . - faridace ta juya da sauri ta .koma dan kiran Deeda da Sabeer, ya zama dole ayi mata adalci ta gana da kakar ta, ta yi mata addu'a
Deedan suka shigO,‘ ta kalli Innan ta fashe da kuka.‘
"Karkiyi kuka".
Ta’ fada tana numfashi da Kyar.
"Karku damu, Allah Na nan, komai zai dai daitai".
Sabeer Ya kalle ta, ya dauke kai, idon sa yayI jajir
"Inna na me ya same ki? Ki tashi 'mu taf1 gida, nan ba wurin zama bane". Ta yi murmushin Karfin hali, tace
Innar ka-tsufa ya’kawo, jiki ina bukatar laushin katifar asIbitin nan tafi sabuwa da 'tauShi akan ta gida, don haka ka barni in tare a nan
Ya yi duriyar karfin hali, hawaye ya gangaro masa, ya ce; _"Inna har a wannan halin ma kina: jin yin wasa?"
_ Ta yi murmushi tace, "To yanzu abinda zan fadi ba wasa bane, tunda ni yanzu na tsufa ga matar ka Deeda sabuwar jini ce ita, ka rike min ita amana, kar ku rabu har tsufa, sai mutuwa. Ka min alkawarin zama da’ Deeda a kowane irin hali, dadi k0 wuya, ciwo k0 lafiya ba 'za ka‘taBa barin Dee‘daba, auren ku nahar abada ne".“. '
Ta kalli Deedan dake ta kuka tana tsorace‘, fuskar ta cike da zulumi da fargaba, ta ce. ‘ ‘
"Kema haka,‘ ki. min alkawarin ‘ biyayya ga' Sabecr da zama da shi « har abada".
"Na yi‘ alKawari Inna. Don Allah kar ki daga hankalin ki, ki kwantar da hankalin ki ki samu laflya ba abinda zai faru da ni"
Sabeer ma ya ce, "Inna, kar' ki damu, ina tare da Deeda,‘ duk rintsi duk wuya, insha Allah ..ba.zamu rabu ba Sai mutuWa". '

Ta 'yi murmushi ta ce."Alhamdu .lillah, Deeda, ki‘ riki Ibrahim dan uwa, duk abinda ya shige miki duhu ki fada masa kinji?',.'.. '
Ta girgiza kai, "Na .ji Inna, me yasa kike irin wannan .maganar? Baki da lafiya, kina bukatar hutu, Inna kiyi shiru ki huta". =
Ta yi‘murmushi, ta ce.
"Deeda, kiyi tamin addu'a Allah Sa baccin nan da zanyi ya zama hutu a gare ni". ' ' ' "Insha Allah Inna zanyi miki". Ta fada tana hawaye. ‘_ _
.. Sai da zuciyarta ta dan yi sanyi ganin yadda Innan numfashinta ya dai‘ daita, da alamar. sanyi a ranta ce
"Allah Sarki Inna ta, 'kwanciyar hankali na shi ne nata, tashin hankali na shi ne nata; In Allah Ya yarda ba za ki sake ganin tashi‘n hankali naba duk yadda za'a- yi in; Allah Ya yarda zanyi Kokarin zama cikin kwanciyar hankali don naki hankalin ya kwanta".
Nan Innan ta kwanta ta .samu_bacci, yayin da Deeda ke riKe da hannunta tana mata addu'a har itama bacci‘yadauke
‘ Ibrahim da Farida suka dita zuwa wani office, dan ya mata bayanin ciwon
Inna— , _(B.p) ne .yaka da ita, sai mayi fatan samun lafiya"- . ' Bayan sun dan- tattauna ya farag._._ mata bayanin ciwon Deeda, ta yi shiru ~ tana Kokarin fahimtar 'sa,‘ sannan "ta ja- dogon numfashi tace. Me kake‘ gani game da ‘ciwon? Za ta iya WarkeWa?" ‘Ya‘ ce, "Kwarai‘, ~sai _ dai akwai tsammanin zai dawo in ta sake zuwa ‘inda jikin ta, bai so, fatar jikin ‘ ta bai so: (Allergy) ne, zai iya dawo wa, k0 in ta ci’ wani ~abu, ko-taBa“ wani abu. Na San dai‘ ’BIRNIN GAYU'ya-karfii jikinta, da (area) din . da take zaune a Kano, matSalar shi ne, ban san me da mene ne jikin tabaya so ba? Sai dai in mun koma ‘zan yi. Kokarin bincike a kuma samamata
‘ (strong) ,magunguna insha Allah '(She Will be fine) in'yaso zatayi rayuwar farin. .
ciki da Sabeer, tunda a BIRNIN GAYU za su zauna"; '
Farida tace"(I hopé so) zan‘f1 kowa farin ciki-in

haka ya”faru'ta wuce Wurin Inna sa Sabeer'zaune
ya zurawa Deeda 'da‘ Inna ~ido yana jin'
kaunar su a ransa. Yana mamakin lokaci guda
Inna da Deeda sun zama Wasu' abu masu
muhimmanci’ a rayuar sa, -- sun zama tamkar?
'yan uWansa na‘ jini; sun
zama rawaar sa‘l - Ya‘ tuna Wasu shekaru
kadan da suka shude babu‘su a rayuwar
sa a, lokaci‘ guda suka shigo rayuwar' sa,
har ma yana jin tamkarba zai iya rayuwa
basuba.’ ‘ _ Da wannan tunanin ya' fita a dakin,
ya nufi can Wajen Kauye inda' ake samUn‘.
netWOrk, ya yiwa' Daddy ,waya ya ‘ sanar "
da shi halin' da aké ciki,'don‘haka ba‘ zasu
samu damar1' dawoWa ba' sai ~ ta samu
sauki.
Daddy ‘ ya ~ce, "Allah Ya: bata lafiya". ‘ ’ , Yayin
da ya girgiza kai, ya ce. . ‘ "Dama Sabeer ban
zaci dawowar ka yau ba". Nan ya koma cikin.
asIbitin ya‘ samu. ‘ . Deeda da Innan yadda ya
barsu. -_Washegari .da asuba Inna ta amsa kiran
'MahalicCi'. Deeda ta idar da sallar "-asuba» tana
zaune kan Sallaya tana taSbihi tacigaba. da
addu'a; yayin da Sabeer ke xan masallaci, Farida
nawani daki na kuSa da nasu Innar tana‘sallah.
r Dukkansu a aslbitin suka kWana, sai dai
hankalin su ya dan kwanta saboda Innan ta ji
sanki SOsai, ta Samu bacCi mai lafiya,
wanda‘ashe saukin taf1ya’ne ba su sani ba. ’
Bayan an idar da sallah Ibrahim da ‘ Sabeer suka
shigo, kai tsaye gun Innar‘ suka wuce‘, a nan
suka tarar da rai yayi
halinta
"Inna -lillahi wa *inna ilaihi, raji'un'". Abin da
suka fadi kenan. ‘ ‘ . Ibrahim V kan , ‘ sa‘ ya
rikice balle Sabeer da hankalin sa‘ ya nemi barin
jikin ‘ sa saboda dimauta. -
Ibrahim ya juya-yana hango Deeda kan sallaya
tana ta. addu'a, tausayin .ta ya kama shi; Ta
yaya zai fara sanar mata ta yi rashin Inna har
abada? _-
Ya kalli ‘Sabeer ya ga yadda ‘shi ma 'ya rikice,
shi kansa yana‘ bukagar kulawa ta yayai'zai iya

kula 'da Deeda? Sai dai_ba'mai iya yin wannan sai shi, ‘saboda shi ne mijin ta.
Ibrahim ya dafa shi, ~ "Sabeer, “ka daure, ka sanba abu'mai sauki ba ne‘, na' san irin sabo da shakuwar da ka 'yi da Inna, abin‘da Wuya. sai dai ya zama dole . ka daure; sab0da kai né mai kula’ da Deeda‘, in ta ganka .haka za ta Kara shiga tashi hankali"
Lokacin Farida‘ ta shigo,ta fahimci abinda ya faru nan ta daure taje tana‘
yiwa Inna addu'a
Lokacin Deeda ta shafa‘, ta taso tare DA fadin -. ."Ina kWanan ku? Ya jikin Innan?" 'Yadda ta gansu yasa ta sha jinin jikinta, ta kalli Innan da ’ ke kwance, ta
- kalle su. Farida ta daure taci gaba da tofawa Inna‘ addu'a, daga nan Deeda ta' soma fahimtar me ke fawwa. Sai ‘dai ba
., r-ta tabbatar hakan ba,‘ sai da ta 'ga Farida taja mayafi ta rufe ta har kai, ta cire (drip) soda (ozygen) din da aka sa mata, wanda hakan shi ne hanyar mafi sauki da za'a sanar' da ita
., Tuni hankalin ta ya tashi,' ta fada kan :Innan ta'- fashe da kuka. Tuni ta flta Hayyacin‘ta tana sambatu. ‘ ‘ _Inna... ta taf1 ta~ barni, Inna ki yafe
min, na Bata miki rai, "na daga miki hankali, har kikayi fUShi ki ka tafi kika barni. Inna kece komai.na,-Inna na-ya zanyi in rayu ba ke? Allah Ya jikan ki Inna,Allah Ya dauki raina nima in huta".
‘ .Kuka' take sosai kamar ranta. Zai‘ fita Farida'ta sa hannu' ta dago ta gami da girgiza mata kai A'a Deeda, kar kima Inna haka, ‘da hankalin ki da ilimin k1 me, ya déeda ki .mata Addu'a. Na san abin da ciwo, dai amma rayuwa haka ta gada, wataran duk haka ‘za mu tafi Mu yiwa Inna addu'a duk, Allah Yasata tafi a sa,a
" Ibrahim ma ya kalle ta,"ya ce. _ '."Gata daya za ki yiwa Inna,“addu'a.
Kar ki zama mai son kai, kiyi 'ta tunanin kanki. Kina' buqatar Inna, sai dai wanda yaf1 sonta ya dauke ta. Ki yi mata~ addu’ar Allah Yasa ta

tarar‘ da Alkhairi,‘ Yasa. mutuwar ta hutu ne. Mu taru muyi
ta mata addu'a don sama “mata rahma wurin Ubangiji. kuyi hakuri Nan ta mike cikin :sanyin murya, tace ‘_,‘na gode,, Allah 1,.Ya . :.saka Tana fadin. ’haka; ta .sa‘ kai ta‘ f1ta :daga dakin, ta bar asIbitin,‘ takama .hanya tana kuka. Ta rasa ma ina zataje? Ina zata ta shiga ta ji dadi da sanyi a zuciyar ta Shi‘take ta fadi tare; da‘famanfadin
" "Allah Ya jiqan kiI inna Haka ta ji. zuciyar ta . nata tsinkewa; gaba dayatakaraya.
, Ta nufi gidan su,kai tSaye ta shiga ‘ dakin Innan, komai yana nan kamar Innan -ta‘na nan, tamkar wacce ta fita Unguwa k0 ta shiga kicin k0. bayi,
Deeda ta kwanta akan gadon, hawaye a idonta tamkar an Balle famfo;
' fashe da tana fadin. '
cikin mtiryar kuka; "Ina ki ka shiga ka dade har? yanzu ba ki daWO ba?" " Ta duqunkune guri guda. ‘ "Inna .ina ki ke ne? Ina jim tsoro kiyi sauri‘ ki dawo Inna, k0 in shiga Inna ni dai ki dawo, ki shigo. Inajin tsoro, ba Ta fashe'da kuka; "Inna, na ina kike? Deedan na jin tsoro, Sabeer ne ya biyo ta,ganin .halin da take ciki ya ruda Shi sosai, hankalinsa a tashi. Ya ‘shiga dakin, tana kwance a. wurin; ya taBata ‘ta mike da,sauri. Tace
"Sabeei', kaga_taKi tado
k0?"‘ « Ya jawota. yana shafa
yana lallashi, tsananin sonta da tausayin ta suka lulluBe shi, ya‘ce. Deeda; ki’ daure, ki jure, ki' nutsu kiyi addu'a. (I know its a painful moment} -for you) .Deeda wanda ya mutu baya‘dawoWa, kiyi kokarin sa wa ~zuciyar ki hakuri, kar ki yaudari zuciyar. ki da ; Kwakwalwar ki dinga tunanin Inna na dafi, don ba kya; so ace'Inna ta raSu. Sai “ dai wannan ba zai can'ja gaskiya ‘ba Deeda, Innar mu tafi ta barmu har abada, sai mu yi addu‘a da fatan Allah Ya‘ ' ' hada faskokin mu da Alkhairi Allah/ Ya jikan Inna". . Nan ta Kara kankame shi, ,ta faShe ’ da‘ kuka, tana hawaye,

' . "Ki yi kuka Deeda samu KO zaki samu sauKin ' zuciyar ki? k1" zubda hawayé Deeda, amma ihun nan da surutan nan ki. ‘dainasu, wannan .ba sai karawa ‘mamaci komai ba
. sai wahala..i_ Kar ki nemi yin jayayya da ikon Allah". .Haka suka kasance yana'ta lallashi, duk da shimé yana bUKatar mai lallashin sa, tana hawaye .yana'hawaye'.‘
Lokaci ’gida Kauyen ya rude' ‘ 'da‘ matuwar Inna, duk qauyenba wanda bai ji ’mutuwar ta ba’, su kansu sun san sun yi rashi. babba, saboda Inna tana daya daga dattijan . Kauyen, Su, masu mutunci’ 'da’ suka jima a' qauyen'. Tana taimakon su da yi. musu Kokari ta hanyoyi' daban-' daban.
' Ibrahim ya yiwa Daddy waya, nan suka sa janaizar Inna ’Karfe tara na safe.
" Nan ya aika aka kira masa mahaifin Deeda Wanda . dawowar sa daga Saudi kenan, likkafa ta ci 'gaba, ya tafi Umra shi da matar‘ sa, bai~ san wane hali 'yarsa ke ciki ’ba, bai’ san me ke faruWa da ita ‘ba
rayuwar ta ba, shi, dai cin duniyarsa DA tsinke kawai yake “
DR Sulaiman yayi masa fada sosai hade da nasiha ya kara da ceWa, yayi hankali _da_duniya,yaji tsoron_Allah,' sannan ya "fada masa rasuwar Inna; Shi kansa sai daya tuno.deéda,‘ da irin so da shaKuwar 'dake tsakanin su' da‘ inna Ya tausaya mata, Nan Alhaji yace ya Shirya...su- tafi jana'iza, sannan ya bada mota da direb‘a ya ‘tafi da matar sa da Tabawa. ' ' ‘ Haka k0 aka ‘yi,_ba; su bata lokaci-ba suka kama hanyar Kauyé.
_ Deeda, .Farida tare da,_ Tabawa su suka hadu sukaiwa ina Inna wanka, Deeda. na hawaye, amma hakan‘ ta_ daure' saboda wannan ne gatan da‘za tai mata
Karfe tara akai ,jana'izar Inna,aka
kaita gidan'ta na' gaskiya” ' ; Deeda dai tayi kuka harta ji ba'dadi,
Tabawa mata yi KoKarin lallashinta bata DA bata baki 'da' Kwarin._ gWiWar ceWar ita zata

zame mata Inna
Farida da Tabawan taré da 'matar ; mahaifinta
'da‘ wasu matan maKo‘tan su_ suka za’una
karBar gaisuwa,;a waje su kuwai " su DR
sulaiman ne‘ wato mahaifin Sabeerfi din, da
'mahaifin Deeda, dankuma sauran? "
,jama'a. ke amsar gaisuwa a wake
‘Abinci‘kuwa daga BIRNTN GAYU aka dinga
kaWo‘ musu har na tsawon
kwana uku ana karBar gaisuWa; '
’;,‘Gata da karamci dangin Sabeer sun nunaWa
Deewa, don har Momi da sauran'dangin' Sabeer,
‘qannen Daddy da yayun; ~ ‘ sa, da ’yan uwa sun
zo yiwa Deeda ta'aziyya tare_ da; yiwa Inna
'addu‘a da kalamai‘: masu kWantar da hankali.
daga karshe ' ta dau" dangana.
daga qarshe suka tattara sukai sallama da
kauyen, da niyyar zasu dinga‘, zuwa ziyara
da' ,kuma» 'Zuwa zagawa asIbiti da 'makaranta,
don. ganin yadda‘ ‘abubuwa ke tafiya. .
' Sabeer na rumgume da Deeda a bayan', ‘ ‘
mota; Ibrahim na tuKi, Farida na'gefen sa, _ suka
kama hanya sai BIRNIN GAYU
' Tun da Deeda ta kutsa-kai BIRNIN - GAYU
gabanta ke faduwa, tana tunanin ya rayuwa za ta
kasance mata? Haka nan , ’shigar ta gidan ya
tuno mata da rayuwar ' da‘ suka yi da Inna a
gidan. Ba ta‘san'" Iokacin da’ ta fashe da kuka
ba. Wannan ’ - karon Sabeér bai yi kokarin hanar
ta 'kukan ba, gaboda ta samu ‘zuciyar. -ta cikin
kewane Bangaren su ya kai ta har daki,‘ ya
zaunar da ‘ita bisa gado, ya zauna gabanta yana
kallon ta, hawaye na .
zubo mata, yace. ‘ "Kar ki Boye kukan ki Deeda,
yi
kukan kan dazai ‘dauké nauyin dake zuciyar ki"«.
Nankuwa ta fada'jikinsa‘ta barke da‘kuka, har
tayi mai isar ta, bacCi ya soma fisgarta Nan ya
,gyara’~ .mata kwanciya, ,sannan-ya‘ tashi ya je
bayi ya shirya mata ruwan ‘wankan .da. 'duk
wani abu da za ta buKata, sannan ya; sauka ya
nifi babban kicin din cikin, gidan ya ba‘da. (Oder)
a shirya mata abinci, mai lafiya. Sannan ya

.dalwo yana' shafar ‘ fuskar ta? a. hankali da hannunsa mai' .danshin: sanyin A C Cikin“ idanun bacci ta; budei_ido a hankali ta rufesu tana hango. kyakkyawar .‘ '- fuskar sa, mata .yana mata mumushi, Nan 'ta soma kokarin miKeWa,ya yi saurin-rike ta dantaimaka mata yace Tashi ki yir 'Wanka kici .. wani abu sai kiji dadin jikinki _ Ba ta;musa masaba ta mike nan ya soma KOkarin' zai “cire- ‘mata riga, . Zuciyarta . ta ‘tsinke, ta yi saurin rike hannun sa, har bari jikin ta yake tsabar firgita. Ya kalleta cikin mamaki. "Deeda, wai ’mene ne- ki ka firgi haka? Abin da kike tuna'ni ba shi nake~ 'niyya ba. Deeda, ni mijin ki ne, bai ' kamata ki dinga tsoro na haka ba. Na lura ‘ a duk lokacin da na matso kusa da ke‘kina tsorata‘, jikin ki har karkarWa yake, « 'me yasa? Ba"ki 'i'ya sa kaya ' gabana , kullum jikinki na rufe ~ Deeda, ban ce dole sai kin yarda da ni ba, amma‘dai ya kamata ki saki jiki dani a matsayina na mijin ki, ba zan taBa' cutar da keba, ba zan taBa miki abinda' ba ki amince' da shi ba.‘ Ki saki jikin ki, ki ‘ daina' rayuwa‘ cikin dar dar, nan gidanki ’ ne, ni mijin neni (Please) Deeda, kinji?“ Ya fada 'cikin marya kamar zai yi kuka

chapter 25

. . . Kanta . sunkuye ta ,.ce, "Na. ‘ji . Sabeer . Nan .ta shige toilét din; ta bUde sabon babin kuka.’ ;.. "Shin har yaushe' zan dinga rayuwa: haka. a .takure, a tsorace? K0: gaskiya‘zan fada masa?" 7.‘ ‘ ‘ ' "Ba zan iya'ba"; _ Ta bawa kanta amsa. .. "Ban san. a wane hali zan jefa shiba ‘ , Ta jima a hali na tunani kafin tayi' wankan, ta nemi .rigan towel tare da tOWe’l din DA zai eufe k0 ina a jikinta, ta. dan leko tana' dube-dube, tayi Sa‘a.‘Sabeer din 'ya fita daga dakin.Nan ta fita da sauri' ta}. je ta. sa wa, Kofar, key; sannan‘ ta 'dawo ta yi _saurin"shiryaWa' 'cikin 'gaggawa; Amma duk saurin ta bata gama ba ta ji Sabeer na murda Kofar yana kiran SUnanta.

Jikin ta na rawa ta hau neman (body suit) dinta amma' ba fa samu ba, kayanta . ma da ta-daWo

da shi ‘daga kauye ba ta gansu ba, don haka tayi saurin komawa *dauko wanda ta cire' a toilet ta 'saka, sannan' ta dora 'Wasu, kayaz akai; ta yi hanzarin bude masa.‘ .Yana’ tsaye ya harde hannu a Kirji. yana kallonta, ya ce. -"Su' Madam Deeda mai' rufewa miji Kofa'» don- kar 'ya =ga abinda Allah ya ‘halatta masa"... , Kanta sunkuye ta" kasa cewa komai, ,» ‘ yayi murmushi. ‘ ‘ ‘ ' karki ,damu, tunda kinyi ' wanka“, saura abinci". "
Nan ya turo table din ’abinci cikin dakin, ya-zaunar' da‘ ita. Yadda ya yi; mata k0 bata da niyyar \ci ya zama dole ta ci don farin cikin sa, don haka ta zauna ta ci sosai wand-a ta, lura' hakan ya ~sashi‘
, farin ciki matuKa.
‘ Haka Sabeer ya ‘dinga; qokarin sa‘ Deeda, dari'ya, sam-“baya. barinta cikin damuwa', ‘
__ Ya koma aiki, sai’ dai ita har yanzun- ' ba ta koma‘ba, saboda a wannan lokacin Ibrahim ke samun damar zuwa _ya: 'duba Deeda shi da ’Farida tare-da bata' magani. Saboda dama shi Iikita ne‘ Kwararre _na fata‘, amma duk da haka sai da _ya hada da (reséarch) bincike game da ciWon ta, don» samun'nasara. .
"‘Alhamdu lillah Deeda ta soma Samun sauKi, fatar ta soma Sakewa daga .nannadewar da yayi. ~Haka "nan yadda jikinta ‘yayi rudu-rudu, ya tashi‘ kamar an mata bulala har _sun soma .Bacewa, A. Kokarin .da Ibrahim yake mata Shi ne. tasamu ta ‘rabu da'-wannan ciwo gabadaya.
" .
' Sai dai k0 bai samu kai ga cimma‘ '
wannan nasarar ba, da alama nan gaba akwai abinda zai iya dawo da_ shi. Abinda ya kuma fi‘ daure masa‘kai shi me; ya yi mata (test) ’gwaji, akwai ~bambanci tsakanin ciwon dana kwanakin. baya Wan'can~ yasan (Allergy) take da» shi da qauyensu' ‘da ruwan garin su,’ yayin da 'wannan ya sha bamban, ya ‘rasa mene ne yajawo shi? Mene ne dalilin fitowar sa? ‘ '
Sam Ibrahim bai 'da hutu, 'kullum yana fadi tashi akan tashin lafiyar Farida da, Deeda, ‘ duk da yanzu sun sami nutsuwa da. kwanciya‘r hankali,

komai na' tafiya musu dai dai, amma shi ba shi da: nutsuwa har sai ya kai ga cin ma nasara. Sabeer Office kadai‘ ke ' raba shi da Deeda, hakan nan ~ya samu nutsuwa; saboda yanzu ‘ta rage (far-(far da shi, ta: sake da shi sosai._
Yawanci k0 da yaushe Deeda tana‘
ta samu la'flya,;ta rayu tare da. mijinta da ‘yan uwanta. Hakabya bata. karfin gwiwa,- ta ji ._ itama: ba zata karaya ,akan nata ciwon ba, don haka ta‘dage da addU'a} da ’bin dogar: maganin- Wanda ta': yi nasara a kwana a tashi fatar'ta ‘ta mike,ciwon ya zama tarihi, _'sai_., .wani. ~kyau da' baske ma da fatar ta-yi.‘ . 'Babbar nasarar ta shi ne yadda ta yita. yaqin zama‘da‘ Sabeer bai ga jikinta da ciwon ta ba, duk da k0 Suna kwana ta're su tashi tare‘ Deeda” tanA matukar ~ girmama Sabeer, saboda tunda ‘ya lura ba ta qaunar ya,je kusa da. ita 'bai sake Kokarib. kusantar taba. ' Zama da Deeda ke yi da Farida agidanta tana kula; da ita ya batadamar'. 'koyan abubuwa da yawa. a Wurin.ta,~ musamman'. in Ibrahim~ ya dawo yadda sukekula da' juna da nunawa juna ’Kauna Yana burge;
a haka taji tanason yima sabeer wannan kular k0 fiye da’haka.
A cikin dabara ta dinga yiwa: F arida tambayoyi yadda mata zata 'sanya namiji~ farin ciki, jan hankalin sa tare da' kWantar .masa da hankali, da sauran zamantakewar
aure ‘ ' '
Farida takan yi murmushi, .sa'boda, ta -fahimci manufar Deeda, hakan._,kuma ya' mata dadi', don haka 'ta ' dinga koya ‘ mata abubuwa da dama, tun daga - . kwalliya, iya‘ . magana mai dadi, da‘ kallo ‘ mai jan hankali. .Yayin data bata babban sirrin sabeer, yana son a shagWaBa shi tamkar yaro Karami, da yawan sa' shi a jiki. . . "
Farida’ta .kalle ta tayi murmushi, ta ce. ‘ ‘, ,. -- ~
"K0 yaushe ki dinga- manna shi.‘ a jikin'
yana«son haka; "Sannan (body ,~ Contact) Wani babban‘ 'sirri ne da‘ yake'
dasa mugun shakuwa da Kauna tsakanin mata da 'miji,_ ‘kikaasance, kina 'yawan kwanciya a jikin

sa, k0 shi ya kasance kullum yana jikinki Yin
'haka{ tamkar da ne da mahaiflyar .sa kullum
tana like ’ da yaranta suna manne a jikinta ta
basu abinci suna zaune cinyar ta,‘ maganiko
ruwa k0 abinci suna manne tare: To duk ran da '
suka flta ba tare da ita ba 'unguwa k0 da na
wuni, daya ne haka .‘za ta yi kewar su, kowane
motsi kadan ‘sai ta yi maganar su', hakat zasu-
zauna ranta. ‘Suma haka yaran, Don haka jawo
mutum a ka, manna- shi k0 uwa da yaranta, ko
mata da miji .da sauran su, yana dasa so da
qauna tare da .shaquwa. dauwamamiya~na har
abada.‘ .Don haka 'kar kiyi Wasa da wannan". -.
~, ‘
Ganin Farida na kallon ta yasa ta sunkuyar kai
don kunya .sai dai duk
maganganunta sun Shiga KWakwalwar ta. Ta
tuna Sabeer yana' yawan sata a jiki‘
k0 yawan kWanciya a jikinnta
l"K0 shi yasa nake yawan jinsa a
raina da zuciya ta? Deeda". ' _ . . Farida ta katse
mata tunanin kinajina
‘Ta daga kai, Ba tare da ta -
dago kai ta kalle ta ba. , Faridan tayi
murmushi,»ta ce,
"Deeda, a dinga gayu burge qanina
, (please) ko zaisa mu samu' labari' “me‘ dadi. ,
Lokaci yayi da za aji‘kukan‘ jariri a BIRNIN'
GAYU, Iokaci yayi da Deeda za
.ta zuba irinta a BIRNIN GAYU".
‘ Kunya tasata mikeWa da' sauri za ta
fita,‘.Farida tayi saurin jawo hannunta;
tace
"Ina zaki tafu tun ba ki gamajin burina ba?
Deeda, ba‘ ki ganin 'lokaci 'yayi da Sabeer‘, zai
zama Baban baby?. Tunda yanzu Alhamdu. lillah
komail:,yayi daidai.ba matsala, kina son Sabeer-
yana sonki Sabeer ya samu nutsuwa da
kwanciyar ' hankali," yanzu ya zama
(responsIble)mutum...". ' .1
Shigowar Ibrahim - ya katse musu hirar, hakan
‘ya‘ bawa Deeda damar-‘fita daga dakin farida
tace.

"Kar ki‘manta da magana ta fa?" . Bata amsa mata ba. ta fita, Ibrahim ya kalle,‘yace Naga alamun-samun sauki '"a‘tare . da ke kwanan nan, na ji dadi Kwarai Alhamdu lillah_ Tayi ' murmushiKa. san-kwanciyar . hankali da. nutsuwa;~ tare ‘ .da .farin ciki;na karawa _.-mutum lafia Yanzu nake ceWa Deeda ya kamata mu ‘ ”
ji labari me dadi daga gare ta". ‘ ‘ Ibrahim ya kalle ta, ‘Wanne irin labari kUma?"" ’ Ta ce, "Kukan jariri a gidan nan"; Dam Ya ji gabansa ya fadi,‘ Wanii ' irin .kishi ya ji ya turnike shi, da Ryar ya - " samu yayi ‘ (controling) din kansa, yaqe yayi DA yafi kuka ciwo ,ya,ce.‘ ‘"Haka ne". ,
‘ Nan ya kawar da maganar ta hanyar- dauko (report) dinta yana dubawa, ya ce. "Ina ganin‘ nasara «kwarai‘, 'insha ~ Allah ciwon ki zai zama tarihi". ‘ " ' Ta kalle shi ta'ce, "Ibrahim, ni me 'kake ganin ya hana ni haihuwa? Naga daga ni har kai ba mu da matsala". ' Ya yi murmushi, "'Allah Ne ,Bai ‘ kawo ba". ‘ '-
Nan ya fice‘ ya da sauri. tare da ‘ fadin. ‘ "Ina zuwa". Ya nufi dakin sa.
, Bayan ta gama- koma bangarenta ta gyara »=ko-ina,. sannan ta? shiga kicin 'ta shiry'awa‘ Sabe‘er irin abincinda' ta san Zai so. Sannan taje’‘ta yi wanka, ~‘t'a fito ta" zauna» ‘a gaban‘ ‘tafkeken madubin dake a dakin,-.wanda ya bata damar kallon kanta gaba" daya.-:'Ta'kurawa kanta ido," gaba daya ta- ‘canja; don har wani sheqi ‘ take tsaban; sumi DA gyaran farida
‘ , Ita dai kwalliya" ba ta' dameta ba donba zata iya tuna yaushe taYi kWalliya‘ da hannun ta ba don haka batasan wane gyara zata yiwa‘ fuskarta ba: Ita dai kwalliya mai sauki, - take so ba wai ta‘ ‘ tashin hankali ba.’ Yauce"'~rana ta 'farko data zauna yin kwalliya da niyyar yiwa mijinta Sabéri donya gani yaji‘ dadi ta samu‘lada; ta kuma Sashi farin- ciki'.kamar yadda. kullum yake ’mata..
(P.C) dinta ta dauko, ba Bata lokacin ta ,shiga yanar..,gizo, ta shiga Bangare na kwalliya anan, ta dinga dubawa, har, -ta hango wan} wuri inda,

taga-‘ansa (Simplicity of‘dress and style).- Nan taryi murmushi saboda ta zo inda take'so, bata ' bata lokaci ba ta dinga bi tana. dubawa har‘ .ta_dace- da irin kwalliyar da ’kuma' shigar da take sonyi, Wanda; ya; dace.:da TSarin kwalliyar, ta yi shiga mai sauKi, amm kuma mai daukan» hankali da shiga zuciya, wanda duk ya gani dole ta burge shi koda kuwa maKiyinta ne.” ' ‘
saidata jima tana kallon kanta. ; ‘ , 'Wato [Deeda kema da kyanki baki‘sani baTadan kwanta tana murmushi.
. ‘Nanta dinga kaiwa da kamowa tana' jiran ,shigow'ar Sabeer', har qarfe biyar
shiru, don haka ta yanke shawaralj kiran office , " aka ce mata ‘ya’ shiga (meeting).Zama tayi tana' jira, nan ta mike tana kallon kanta, ba ta taBa , k0 da ' makamancin wannan shigar ba, don haka yau kyan da tayi daban ne.- Amma duk da haka da zata samu wacce zata? Ce mata tayi, kyau, k0 ta gyara wani abu za .ta so haka. '
' "Sister’ ce zan .iya nunawa, kuma ba zan iya flta haka inje gidanta ba". ' ‘
Nan da‘bara fado mata; ta dauko (Caméra) ’da' sauri ta daukan- hoto, ta saita ta (Automatic camera) ne, don haka ta dauki hoto kala‘ biyu ta tura cikin wayar ta _.ta turawa Farida tare da tura mata sako
{Sist‘er ga hotonanan na turo miki kiga kwalliya ta . shin tayi kyau? Wanda
inna yiwa Sabeer zaiso? (hope he will like .it).
Farida na kwance Ibrahim na‘ mata hira ta ji’ karar 'saqo ya shigo wayar ta, nan ta sa hannu. ta dauka ta duba
"Wow a, ta fada tana murmushi, ibrahim ya kalle ta.'Me ya faru?"-'A'a ba komai, wannan bata Shafe ka ba, sirri na ne ni da Deeda". Girgiza kai yayi yana murmushi, ya
Ce, "To. masu sirri, bari na shiga na , shirya, zan; shiga asIbiti..Indai Jikin ki. da ._ Sauki ma 'ina so in kwana a can, akwai' ~ aikin'da zanyi". _ , '
*‘ ‘ Ya lura hankalin ta na kAn waya, bata ma san yana ‘yi ba.. . ',_ Murmushi' yayi ya shige "K0 ba

komai (she is happy ya fada a ransa. Farida ta yiwa Deeda I (reply) da
cewa- . ‘ . ' (He will only 'not like u, but also love you more) Kin burge ni kwarai, (I am proud of you). Ta tura mata; . ' Deeda dadi‘ ya-lulluBe ta, yayin da ta
kasa ,zaune da'tsaye,don ganima take kamar lokaci baya. tafiya haka kawai, taji
kaWar sa da s0n sa sun dame ta‘ Wayar ta ta sake daukowa ta soma' rubuta masa message kamar haka:
Assalamu. 'Babyna (i
" Wonder Why i am missing you so much
._ today?) Haka- nan son Sabeer‘da tunaninSabeer sun matsa ma zuciyar deeda (come back soon I love you)
. Sabeer ne zaune "tsakiyar‘ (meeting), kansa ya dau zafi, ya gama gajiya gaba' daya’, sannan yau tunda' ya bar gida‘ baiyi magana .da Deeda ba saboda aiki; Ya ja ‘.
dogon numfashi, yace 'deeda (i really need you here) na gaji, ya kamata ki fara zuwa aiki, cikin Wannan yanayi yaji shigoWar saKo wayar sa,;da, dai yayi “kamar bazai duba ba sai kuma ya fada ya dauko- “yabude‘ : Wani murmushi yayi tareda jin‘ wani sanyi da sukuni a zuciyarsa ya bata amsa DA cewa Wslm ; my Deeda. ~ -Kina tunanina da missing din Saber ne .Saboda . " ina buqatarki Ina tsakiyar (meeting), da client ne duk na gaji ganin text dinki ya Kore duk wata gajiyata . (thanks Deedan 'Sabeer, I luv : you more)ina hanyar daWoWa (take care).
wani dadI taji
ya lullubeta ta kifa wayar .a: .kirji -'tare-da lumshe ido'tana jin
.son Saber nabin jinin jikinta daga
a karshe ta dinga juyi akan. gadon tana shakar Kamshin kayan sa da turaren‘ sa, tana jin sonsa mai' karfi a ranta.’
‘_ Karfe shida dai dai ya‘bar offlce ya nufi ‘gidé, 'zuciyarsa ciké“ da‘ ' nishadi da son Deeda. *"Kai‘ *tsaye’ ya: wuce" (area) dinsu Tun' da ya shigo gidan ta hango Shi *daga sama, da sauri' ta-

sauk'o ta nufi kofa » don taryansa.. Don haka
kafin'Sabeer Ya .kai ga bude kofar ya ga ta bude
